[03/05, 6:47 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

MABUƊI
Duniya da mutanen da ke kewaye cikinta sun jima yi mini kaura tun ina shakar matsakaiciyar iska a cikin mahaifiyata,a lokacin da ko numfashi ban taɓa yi a cikin duniyar ba.
Abun mamakin sai ya zamto harda wanda ya zama silar kasancewar rayuwata acikin cikin ma ana mahaifina!
Me muka aikata?
Me muka yi wanda ba daidai ba?
Shin Musuluntar da mahaifiyata tayi tare da sadaukarwa shi ne ya zame mana tikitin siyan  rigar da za a wofantar damu?
In danginta kirista sun gujeta domin bijerewa umarni da addininsu  da ta yi.
Kuma suma musulman sai kyamacemu,saboda daga mara sallah ta dawo mai sallah?
Abar ƙyamace?
Abar guduce?
Abar kyamatace?
Ba ma wannan ba to ni kuma mene ne laifina?
Aa!
Addinin musulunci bai koyar da haka ba,hasalima ya nunar da a kyautattawa kowanni Ɗan Adam ko da kuwa ba musulmin bane,bare kuma wanda ya musuluntar.
Tabbas mahaifiyata jarumace da ke iya juriya,jajircewa hakuri tare da sadaukarwa wajen tabbatuwar rayuwata a duniya ba tare da taimakon kowa ba kuma ba tare da jin cewa hukuncin da ta yanke na kasancewarta a musulma laifi bane.
Ban da wata jarumar da ta zarce ta domin kuwa ta kara gasgata babu abun bautawa da gaskiya sai Allah, a lokacin da take da tsananin bukatar taimako ta kauda kanta ga duk wata hanya da zata iya sauya mata kudirinta,ta rayu ita kaɗai,cikin kadaici,talauci da tsanani har zuwana duniya kuma ta ɗaurani akan Addinin musulunci ba tare da wani tantama ko jin cewa ba a kyauta mata ba,illa kara nuna mini d take lallai duk rintsi ka da in bari zuciyata ta yi galabar rabani da addinin gaskiya.
Yanzu na girma na mallaki hankalin kaina na yi karatu kuma na san daraja da kimata ina son rama juya mun baya da duniya da mutanen cikinta da suka yi tun kafin zuwana cikinta ta wata

sigar da ni kadai na san mai nake aikata,to amman kuma sai ana yi mini kallon mara adalci? mara gaskiya kuma macuci? Aa sam ba zan fasa ba na tabbata akwai tarin mutanen da ke fuskantar irin kalubalen da ni da mahaifiyata muka fuskanta.....

PAGE-1

Malaysia
Kwance Farouq ya ke a cinyar mahaifiyarsa tana shafa gashin kansa,kamar an tsikaresa ya tashi ya zauna yana kallonta.
"Lafiya?"Maah ta furta.
Murmushi ya yi kafin ya ce,"Maah."
Ta amsa da ,"Yes me ya faru?"
Farouq ya ce,"me yasa duk da cewa sanadin shiga musulunci duniya da mutanen cikin ta suka juya miki baya amman kin gagara fita daga ciki?"
Numfasawa ta yi ita ma ta saki wani Murmushi kafin ta ce,"Dalilan suna da yawa amman kuma kafin nan ina so in fara sheda maka cewa babu wani ingataccen addini fiye da muslunci domin kuwa shi ne haƙiƙanin addini na gaskiya ba tare da sirki ba, duk zuciyar da ta shaƙu da musulunci zai yi mata matukar wahala ta iya fita cikin sauki,kuma duk idanun da ya yi tozali da hasken musulunci ba zai taɓa iya bari ya rufe idanunsa ba domin komawa duhu ba,duk da cewa na wahaltu na azabtu kuma na tozartu sanadin canja addini na izuwa musulunci amman ban taɓa jin ba dadi ba ko alamun dana-sani ba a rayuwata sam sam ko kadan hasali ma a kullum ina jin cewa wannan shine hukunci mafi kyawu da na taɓa yankewa a cikin rayuwata tunda kuwa gashi karshe naci riba ko ince  ina ma cikin cinta dumu-dumu.
Ina son musulunci,zan rayu cikinsa kuma zan mutu cikinsa da ikon Allah. "Maah ta karasa maganar tana ajiyar numfashi.
Farouq ya ce,"wannan gaskiya ne amman kuma Maah tunda ki ka dawo nan  mahaifina ko danginsa ba su taɓa nemanki ko jin cewa basu aikata miki daidai ba,ba su taɓa tunanin waiwayarki ko don saboda ni da na kasance jini a garesu ba?"

Maah ta ce,"A kan me zasu neme ni? A tunaninsu abun da suka yi shine daidai tunaninsu ni kazamiyar kafirace da baza su iya haɗa jini da ita ba duk da cewa na jima da daina amsa wancen sunan na shiga addininsu,suna son kansu fiye da kowa suna jin cewa kyara ko tsangwama ga wanda ya taɓa kasancewa ba musulmi ba inya musulunta daidai ne bana jin cewa akwai ranar da zasu ji cewa basu aikata mun daidai ba aransu kai kuwa ai basa fatanma ka zo duniya tunda hasashensu na basu cewa katon arne za a haifo masu cikin dangi ba ma wannan ba basu amince da cewa kai din nasu bane,gani suke ai kasancewata ba musulma ba yadda na yi mu'amula da mahaifinka haka nake yi da wasu sun manta da cewa kaddara ta wuce komai kuma ba a iya taɓa tsere mata domin a rubuce take ga rayuwar kowanni Ɗan Adam sun yi mini kazafi sun kore ni sun wulakantani da ya kai inji cewa addinin ya fita akaina.

Duk da cewa ba duk musulman bane suke da hali da ɗabi'a irin tasu domin kuwa na ga zahiri yadda wasu yan kasar nan suka jani a jiki mussamman da suka fahimci dalilin kasancewata ni ɗaya da cikinka a wancen lokacin ba wai anan dinma ban fuskanci kalubale bane aa amman dai

da sauki kuma na samu wa inda suka karbeni hannu bibbiyu duk da cewa ana nuna masu cewa ni kafirarce kuma kazamiya sun toshe kunnuwansu sun rufe idannunsu sun fuskanci abubuwa da dama silata amman hakan bai sa sun gujeni ba sai ma kara kusantata da nuna mini so da kauna
*amman abun na gagara ganewa shine tsakanin su na cen da musulman nan masu practicing addini da dukiyarsu zasu iya ba da komai nasu domin ci gaban addini da da wa inda kuma koda suna da dukiyar ba za su iya badawa sai dai furuci da nuna cewa su musulmai ne su waye masu kishin addini na hakika tsakani?*."
Farouq ya ce,"Allah ya kyauta ya rabamu da sonkai irin na zuciya amman dai kam a tunani wanda zai iya sadaukar da dukiyarsa domin addininsa ai ya gama komai kuma ubangiji da zuciyar mutum yake aiki ba furucinsa ba addini ya kwadaita mana sadaka indai inada hali kuwa ya kyautu dukiyata ta zam bango ga al'umma."
Maah ta ce,"kai ke nan da wannan tunanin".

Farouq ya kara fadin,"Ina neman wata alfarma a wajen ki ban sani ba ko hakan zai samu amman na miki alkawari indai bakya so to na hakura."

Maah ta ce,"In sha Allah ina jin ka."
Farouq ya ce,"Ina so inje Nigeria niger state wajen mahaifina da danginsa amman hakan ba wai yana nufin kin kasa mun bane akwai bukatar lallai inje ne domin tabbatar masu da kasancewarmu tare da tunatar da su abun da suka manta da kara nuna masu hakikanin rayuwar musuluncin da suke taƙama da shi ba tare da amfani da ainihin haƙikaninsa ba."

Shiru Maah ta yi take yanayinta ya canja idanunta hawaye suka cika.
Da sauri Farouq ya ce,"Na miki alkawari indai bakya so na bari kuma na bar maganar bana so inga ɓacin rai ko damuwarki."
Shiru ta yi can kafin ta yi murmushin karfin hali,"aa innace ma na hanaka ban kyauta ba Farouq,ban yi maka adalci ba kuma na tauye ma hakki,ka je ka ga mahaifinka amman ka sani zaka fuskanci kalubale kila ma fiye da wanda ni na fuskanta kuma bana da adireshensu ban san ta ya zaka samo bayanai akansu."

Farouq ya ce,"kar ki damu da wannan abu ne mai sauki aguna karki manta yaron naki computer titan yanzu zan iya binciko komai nasu a media."
Murmushi ta yi ta ce,"tabbas to ina yi maka fatan alkairi,Ubangiji ya baka sa'a kuma yasa tafiyar da za ka yi ya zame ma alkairi yanzu yaushe zaka tafi?"

"Ni da zan samu flight ma zan wuce amman zan bari zuwa gobe ko jibi haka."
Maah ta ce,"iye wannan saurin fa?"
Dariya kawai Farouq ya yi.
Ta ce,"Shikenan Allah ya kaimu."
Ya amsa da Ameen kafin ya tashi ya shige dakinsa da sauri yana daukan computer.

Kai tsaye Javed ya ma magana.

"Friend ina tunanin gobe zan tawo In sha Allah."
Javed ya ce,"Ok Ma sha Allah  daman kasan mun kammala komai zuwanka kawai muke jira."

Bayan sun gama magana Farouq ya shiga 5stars group  yana fadin,"Hi guys na kammala komai fa kan batunmu na yiwa yara mata marasa karfi training akan computer a niger state I think gobe zan wuce so a tayamu da addua."
Deejerh ta ce,"weldone our mummunan mutum Allah ya bada sa'a  i wish u all the best ba don abubuwa sunyi yawa ba da bika ai."
Dariya Farouq ya yi yana fadin,"wa? Yaushe wannan anacin mijin naki zai bari ki bi a yanzu ana ganiyar cin amarci ai kiyi zamanki kawai."
Dariya kawai Deejerh ta yi.
Khalil ya katse su da fadin,"Ma sha Allah weldone mutumina abubuwa na kyau Allah ya bada sa'a saura aje can a bige da neman mata kuma."
Dariya suka yi duka Farouq ya ce,"kai ma ai kasan wannan dole ne ko ni ban bisu ba suna ganin handsome guy suke ruɗewa,kun ga bara inje in fara shiri ba time."
Haɗa duk abun da yake bukata zai tafi dasu ya yi dake maganar flight ma ya riga ya yi booking tun kafin ya sanarwa Maah.

Washegari
Ya kammala shirin tsaf kuma jirgin safe ya yi booking sai da Maah ta rakasa airport har jirginsu ya tashi kafin ta koma gida.
Jirginsu ya sauka a abuja daga nan ya hau motar da za ta kai shi Niger.

NIGER STATE
Minna

Tsaye yake bakin titi dauke da lemarsa a hannu dake anyi sosai yana jiran Javed yazo ya daukesa.
Kamar daga sama ya ji saukar ruwan laka daga fuskarshi har jikinsa.
Daga idanun da zaiyi ya ga wata budurwa ce ke kokarin tada motarta.
Cikin fushi da takaici ya yi saurin karasawa yana fisgar hannun motar ya bude ya..........
[03/05, 6:48 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at

08103080717*

PAGE-2

Ganin yadda ta nuna bata ma san ta aikata wani abu ya fusata shi,janyota ya yi daga cikin motar cike da zafin rai.
Budurwace da ba zata zarce shekara ashirin da biyu ba irin dogayen matan nan farare masu diri irin na Nufawa sanya take da farar da abaya da glass a idannunsa kallo guda za ayi mata a tabbatar da cewa cikakkiyar yar boko ce kuma wayayya.
Kafin Farouq ya samu damar magana cikin sauri ta fisge hannunta tana binsa da wani irin mummunan kallo.
A harzuƙe ya ce,
"How could you be so careless with your dirty car and splash muddy water all over my clothes?"
Gyara zaman glass din dake fuskarta Janinah ta yi kafin ta saki wani guntun tsaki cike da tsiwa ta fara magana,"As I see, there's no problem with your eyes, but it seems you are acting like a blind person. Why can’t you stay off the road? sannan batun motata kuma da kake alakantawa da kazanta ai gwanda ni ba a titi nake tsaye ba tamkar mabaraciya."
Daga hannu Farouq ya yi zai mareta.
Ta yi saurin dakatar da shi ta hanyar rike masa hannu.
"Kuskure mafi girma da ka tafka a rayuwarka shine tunanin kai min marin kafin ma ka aikata din,So Don't ever try it in ko ka aikata za ka san ni wace ce za ka san wa ka taɓa sai ka yi dana sanin kasancewar ka a duniya ma gabadaya. "

"Oh do you have this confidence?"
Farouq ya fada.
Girgiza kai ta yi.
Kafin ta ankare kuwa sai jin saukar wani azababben mari ta yi a fuskarta.

Ya ce,"So na yi kuskure mafi muni ko? Zan yi dana sanin zuwana duniya ko? Alright duk ina jira ko wa zaki kira ki kira ina daidai da ke da rashin kunyarki and sai na gyara miki zama sai na koya miki ladabi da biyayya da kuma ba da hakuri ya yin da kika aikata ba daidai ba ga wani na lura da cewa yan kasar nan kuna dauke da ɗabi'ar cewa duk abun da kuka aikata daidai ne ko da kuwa ba daidai din bane."
Cikin ɗimaucewa Janinah na kuka ta je cikin laka ta dibo tamkar wacce ta zauce tazo jikin Farouq tana shafa masa.
"Na kara,na ce na kara duk abun da za ka yi kai ma ka yi inka isa kuma wallahi sai ka yi dana sanin sanya hannunka da ka yi a fuskata kazamin banza da wofi kawai." Ta karasa maganar ita ma tana kokarin marinsa.
Mutane ne suka cika wajen wata mata ta rike Janinah ta na fadin,"Stop this please Janinah ina cen ina jiranki ace kina nan kina fada me zai kaki fada da namiji akan titi for god sake?"
Kokarin fisge kanta ta fara yi tana,"ki bari in nuna masa waya taɓa nina ce yazo ya tsaya akan titi yanzu haka ma irin matsiyatan nan ne yaje ya kwaso talaucinsa zai sauke akaina,ni ki barni inje in rama marin da ya yi mun ya san bai ci banza ba."

Dariya Farouq ya yi yana,"please ku saketa tazo ta rama,yau zata ga yadda ake maida mutum laka,tunda ita lakar kasa ta shafa mun ni kuma lakar mutum zan maidata sannan ni bana bukatar in zama wani ai indai arziki irin naku ne bana so ko da kuwa a mafarkine wawiyar yarinya kawai."
Hakuri mazan wajen suka fara bashi kan ya yi shiru ya kyaleta haka yarinyar take bata da kunya sam ga tsiwa da raini.

Aranshi ya ce,"in ko hakane tabbas indai Allah zai hadani da ita sai na gyara mata zama ta san daraja da kimar mutane."
Ihu da sambatun da Janinah take ne yasa ya dawo daga guntun tunaninsa ana janta ta shiga mota tana kokarin dawowa wajensa.
Wani dutse ta dauka ta wurga masa tana kara fadin,"Wallahi Allah duk sanda na sake ganinka na rantse ba makawa sai na rama marin da ka mun ka ci bashi kuma kasa aranka sai ka biya indai zan ganka a duniyar nan you must pay for it."
Da haka ta shiga motar da kyar.
Shi ko Farouq wani irin murmushi ya sake wanda shi kadai ya san dalilinsa da kuma ma anarsa.
Wani namiji agun ne ya ce masa,"Sir ko za muje in baka kaya ka canja tunda wannan duk ya jike? Ka yi hakuri fa yarinyar ce sai a hankali tana ji da cewa danginsu na da kudi a tunaninta zata iya komai ba komai bane."
Farouq ya ce,"kar ka damu abokina nake jira kuma...kafin ya karasa maganar ma sai ga Javed na kiransa ya iso yana ta ina ne.
Daga kan da Farouq zai yi suka hada ido.
Da sauri Javed ya karaso yana,"Subhanallah what's wrong with your clothes?"
Mika masa hannu Farouq ya yi suka gaisa kafin ya ce,"ina zuwa na fara cin karo da marasa kunyan yaran kasarku ta ɓata ni da motarta."

Javed ya ce,"Sorry wasu yaran in suka gansu da mota jin kansu suke a wani matsayi daban na shirmen tunaninsu yanzu dole kafin mu wuce sai mun nemo hotel ka yi wanka ka huta ka ci abinci ka canja kayan nan kafin mu wuce Mokwa."

Farouq ya ce,"Okay tom shikenan ai har sai da na mari yarinyar Allah ta bala'in bata mun rai ni ban saba ganin irin wannan rayuwar ba wato in danginku na da kudi shikenan kuma lallai kasarku da gyara."
Javed ya ce,"wasu kam sai hamdala Allah dai ya kyauta."
Kai tsaye hotel suka wuce suka kama daki Farouq ya shiga ya yi wanka ya yi sallah ya canja kaya kafin ya ci abinci.
Javed ya ce,"zaka dan huta kafin mu ci gaba da tafiya ko?"

"Hutun jaki da kaya? Ai inaga gwanda kawai mu karasa sai ayi hutawar mai gabadaya. "
Farouq ya fada.
Javed ya yi dariya.
"Alright mu je to."
Hanya suka dauka.

NIGER STATE/MOKWA
Da ke sunyi sauri tafiyar awa uku suka yi suka isa cikin mokwa.

Mokwa local government ne da ke cikin jahar niger state.
Gari ne mai kyau da kyawawa yanayi.

Garin ya kan kogin neja wanda ke taka muhimmiyar rawa a tattalin arziki na yankin.
Haka kuma tattalin arzikinsu ya dogara ne ta hanyar noma, filaye kusa da kogin neja suna basu damar noma nau'ikan amfanin gona da dama kamar alkama,rake,riɗi,masara da shinkafa.
Sannan suna bawa kamun kifi mahimmanci saboda kogin da suke da shi hakan ya na samar da sana'a ga mazauna yankin.
Suna da al'adu da dama  tare da kabilu amman sai dai mafi akasarinsu nufawa ne.
Suna gudunar da bukukuwa na al'adunsu kamar su bukukuwan girki wanda ake shiryawa domin girbe abun da aka noma,rites na wucewa  shi kuma bikine da ake shiryawa matasa yayin da suka kai wani mataki na rayuwa  kamar shigar da su cikin manya.
Sai kuma bukukuwan aurensu wanda shi ma yake cike da kayatarwa da al'adu akwai kuma bikin girmama kakani ana gudanarwa domin tuna gudunmawar da kakanni suka bada ga al'umma da kuma bayyanar da hikimarsu ga matasa sai kuma bikin kirsimeti da sallah kamar yadda sauran jahohi da garuruwa ke yi.

Suna da sarauta mai karfi mai karfi da tsari wacce ta hadda da sarkin gari,kakakin gari,sarkin noma,sarkin kudi,sarkin Al'adu da sauransu.

Farouq sai kalle kalle yake yi karshe dai ya kalli Javed ya ce,"amman wannan garin na ku ya matukar tafiya dani tsarinsa da komai tamkar wani babban birni a kasar waje kai kace ba a Nigeria muke ba."

Javed ya ce,"gaskiya kam kowa na aikinsa bisa tsari ba wasa damuwar kowa yafi wancen yin abun da ya dace daga shugabbanin har sarakun nan."

"Ma sha Allah  yanzu wani hotel din zaka kaini?"
Javed ya ce,"Hotel kuma? Haba dai ai a gidanmu zaka zauna har ma na sanar an shirya tarbarka."

Farouq ya ce,"anya ni dai ban cika son takurawa mutane ba."
Javed ya yi murmushi,"ba takura bane ai kasa aranka gidanmu tamkar na ka kaima haka kuma nima duk sanda zan je Malaysia zan dauka kamar a gidanmu nake."
Murmushi shi ma Farouq ya yi ya ce,"Shikenan na gode Allah ya bar zumunci."

Daidai wani gatafaren gidan saurauta suka tsaya ana kokarin bude masu.
Tun daga wajen gidan za asan cewa zai amsa cikakken kowani suna da gidan sarauta ke amsawa.

Farouq yana daga kanshi sama yaga an rubuta shedar MASARAUTAR SARKIN AL'ADU ma sha Allah ya furta a zahiri ya yin da aka bude masu gate din.
Janinah na hango motar Javed ta fito da sauri tana jira ya karasa parking ta masa magana.
Yana fitowa kuwa ya yi saurin komawa bangaren da Farouq yake ya bude masa kofa.....
[04/05, 10:15 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-3

Janinah na kokarin tawowa inda suke Farouq na fitowa daga cikin motar.

Kansa na kasa ita kuma tana kallon wayarta da kira ya shigo ciki.
Da saura ta dauka tana fadin,"Mammah Mi da nan (ina nan),Okay to me bedabo (gani nan zuwa)."
Ta karasa maganar tana juyawa cikin sauri.
Farouq ya karewa gidan kallo kafin ya kalli Javed ya ce,"Ma sha Allah nidai tunda nazo ina ta cin karo abubuwan ban mamaki da sha'awa ban da mara kunyar yarinyar da na ci karo da ita ban ga wani abun rashin jin dadi ba a garin nan mussamman cikin mokwa ni anya ni ba zan nemi waje inyi gini ba kuwa ina zuwa ina dan hutawa."
Dariya Javed ya yi ya ce,"aiko da na ji dadi abokina dan malaysia garinmu ya birgesa ya yi gida."
Farouq ya ce ,"aikuwa dai na ji inaso gaskiya. "

"Ubangiji ya tabbatar mana,yanzu mu shiga ciki ko?" Javed ya fada.
Wani irin faduwar gaba Farouq ya ji zuciyarsa na bugawa cikin sauri sauri.
Nemawa kansa nutsuwa ya yi cikin ransa ya fara karanto,
"Allahumma inni a'uzu bika min al-khwaf."
Ajiyar zuciya ya yi na karfin hali kafin ya amsawa Javed da ,"Okay mu je."
Daidai kofar da zasu shiga fadar Sarkin Al'adu suka ci karo da wani dattijo.
,"Ah Javed bakon naka har ya iso ne?"
Javed ya amsa da murmushi,"Eh wallahi Abba."
Dagowan da Farouq zaiyi suka haɗa ido da Abba wata irin yanayi dukanninsu suka shiga wanda basu san dalili ba kallon kallo suka tsaya yiwa juna na tsawon second talatin Farouq ne ya yi karfin halin kashe shirun da fadin,"Barka da warka Abba ina wuni fatan mun sameku lafiya."

Murmushi Abba ya yi kafin ya ce,"lafiya lau,Alhamdulillahi barkanka da zuwa,Allah  ya yi albarka ko."
Farouq da Javed suka amsa da Amin.
Abba ya wuce yana fadin,"ina da meeting bara inje sai na dawo  ma yi hira."
Ya karasa maganar yana fita da sauri.

Javed ya ce,"wannan shine Alhaji Abdulmalik wanda yake kanin mahaifina mutum mai kirki da son mutane dan gaye ajin farko duk da kasancewar yana rayuwa cikin gidan sarauta kuma yana da gadon sarauta hakan sam bai dameshi ba,hasalima yafi son sanya kananun kaya fiye da manya kamar yadda ka ganshi a yanzu,yana nuna mana soyayya da kauna fiye da zato wanda in ba an fada ba kai kace shine mahaifinmu mussamman bangaren karatu duk wanda zai taso cikin wannan gidan sai ya yi iya bakin kokarin wajen tabbatar da cewa ya samu ingataccen ilimi kuma shi Allah bai bashi haihuwa ba har yanzu kuma baya taɓa nuna

damuwarsa ga hakan ya kan ce ai gamu mun ishesa."

Farouq ya yi murmushi kafin ya ce,"aiko gashi tamkar sabon saurayi baya tsufa. "
Javed ya yi dariya,"ina zai tsufa kullum mutum na cikin ado har yanzu mata rububi suke akansa a yadda aka bamu labari tun yana matashin saurayi mata ke binsa kuma har yanzu ma basu daina ba yana da farin jini sosai don ko ni da nake matashin saurayi Abba Malik yafi ni kwarjini da farin jini agun yan mata."

Dariya Farouq ya yi.
Suna ci gaba da shiga cikin fadar suna ci gaba da tattaunawa har suka shiga inda sarkin al'adu yake.
Shigarsu dakin tun kafin Sarki ya dago jikinsa ya bashi wata alama da ya gagara fahimta aranshi dai yasan cewa dole wani babban al'amari ne yake shirin faruwa ko kuma ya riga ya faru.
Durkusawa duka suka yi suka gaisar da shi.
Ya amsa cikin izza da isa irin ta sarauta idanunsa na kan Farouq duk da cewa javed ya sanar da shi cewa daga malaysia bakon nasa zai zo.
Har sai da suka fice idanunsa suka bar kan Farouq aran mai martaba ya fadin,"gashi da yanayin turawa amman babu shakka jikinsa akwai jinin sarauta duk yadda akayi acen malaysian ma suna da sarauta."

Suna fita Javed Ya ce,"shi kuma wannan shi ne mahaifina Alhaji Abdul-Raheem wanda yake shine Sarkin Al'adu na garin mokwa kuma ya gaji sarautar ne tun daga wajen kakanninmu shi mutum ne da bai da sakewa da mutane kuma mai tsaurarran ra ayi da kafiya inya furta abu baya so aja da shi ko kadan baya wasa da al'adu sannan yana da kokarin kiyaye duk wani mutunci da martabar wannan gida duk wanda ya yi kokarin kawo tsaiko cikinsa ko waye shi sai ya yi kokarin dakilewa domin ya kan ce martaba da kimar gidan nan tana da mahimmanci a gareshi tamkar rayuwarsa zai iya rabuwa da kowa kuma zai iya ɓatawa da kowa akan martaba da kimar gidan nan in kana neman asali kuma cikakken  dan gargajiya to ka samu mai martaba."

Farouq ya ce,"ai kuwa kasan yawanci haka masu sarauta ke da tsauri sosai."
Javed ya yi ajiyar zuciya,"e kam Amman fa Mai martaba ya yi yawa gaskiya. "

Falon Hajiya Kaka suka je suka gaisheta.
Kasa dauke idanunta akan Farouq ta yi tana ji aranta wani da ta sani ne amman kuma ta gagara tunawa hakan yasa kau da kai kawai ta ce
,"Ah anzo mun da sabon mijine"
Ta faɗa cike da tsokana.
Farouq ya ce,"ai kuwa ga sabon miji kin samu amman ni ina da kishi sai dai a saki dukka sauran abar ni ni kadai."
Dariya hajiya kaka ta yi ta ce,"anyi an gama don kasan daman ni nafi gane fararen fata irinmu tuni zan basu yellown kati na saki dari ba ɗaya."

Duka suka kyalkyale da dariya.
Hajiya kaka ta ce,"waiji lafiya? (Ka zo lafiya)"

Farouq ya ce,"to fa inda matar zata kada mijin kenan ai ba jin yaren naku nake ba."
Hajiya kaka ta  ce," aiko tunda kake da mata banufuya dole ka koyi nupanci."

Farouq ya ce,"anyi an gama daga yau yanzu ma."

Dariya hajiya kaka ta yi ta ce,"ince kun gama gaishe gaishen ku samu kuci abinci gashi cen nasa an haɗa muku."
Javed ya ce,"ehto ba mu gama ba amman daman su nake ya ci abinci anan muyi sallar magrib tukun sai mu karasa sauran."
Hajiya Kaka ta ce,"ya kyautu kan gwanda hanjin sabon mijina ya fara daukan girki ban so ya wahala kun sanmu a zamaninmu mun san salon rike miji."
Dariya suka yi duka kafin suka tashi suka koma bangaren da aka jera masu abincin suka fara ci.
Suna cikin ci Javed ya ce,"wannan ita ce hajiya kaka mahaifiyar mai martaba da Abba Malik da Kuma Kilishi Hajiya Khaleesa ita kaɗai ta rage mana a fannin kakanni kamar yadda ka gani dattijuwace mai faran faran da mutane ga fara'a da wasa da dariya tana matukar kaunar jikokinta sosai sannan ita ma ba baya ba wajen ado duk da cewa ta tsufa zan iya ce maka gadon Abba malik ta yi a fagen tsafta da son ado da kuma son jama'a."
Farouq ya ce,"gaskiya kam har na ji ina kaunarta da ma ace ni ne nake da kaka kamarta da na ji dadin rayuwa sosai."

Javed ya ce,"umm yanzu ma kasa aranka tamkar ita din jinin kace na tabbatar da cewa kuma Hajiya kaka zata sa kaji hakan aranka domin kowa nata ne kuma babu bambamci."

Bayan sun gama cin abincin suka yi sallah Javed ya ce," To yar tsohuwa mun gode da abinci bara mu karasa gaishe gaishe bako ya samu ya huta."
Hajiya kaka ta ce,"aa fa ka daina cemun yar tsohuwar nan kar sabon mijina ya fara guduna yan mata zaka na cewa. "
Da dariya Farouq ya ce,"ai ni kallon budurwa yar shekara sha shida nake miki ki rabo da shi yan matana."
Hajiya kaka tayi dariya ,"yawwa mijin kirki to sai da safe ko a huta gajiya lafiya."
Da amin suka amsa kafin suka fice suna dariya.

Bangaren mahaifiyar Javed suka wuce.
Ita ma ta tarbesu cike da sakin fuska tare da yiwa Farouq maraba da zuwa.
Javed ya ce,"wannan ita ce mahaifiyata ita ma dai mace ce mai son mutane da son kyautatawa al'umma mu hudu ta haifa nine na uku akwai yayuna maza guda biyu Ya Jamaal da Junaid duk sunyi aure suna cikin gidan nan suna rayuwa da yaransu sai ni da kuma kanwata ɗaya tilo

Janinah da ta kasance m081030807q7inmu,mahaifiyata tana matukar bin umarni da dokikin mai martaba domin ko gyaran murya ya yi tasan me yake nufi inko yace mata kar ayi abu to bazata taba aikata wannan abun ba ko da kuwa ranta naso in yace kawai ta bi babu makawa."

Farouq ya ce,"Ma sha Allah."
Daga nan suka wuce bangaren Matar Abba Malik ita ma ta karbesu cike da fara'a.
Suna fita Farouq ya ce,"lallai ita ma matar nan tana yanayi da mijinta naga ita ma tana son mutane sosai."
Javed ya ce,"ai Aunty Heedaya ba ruwanta kam wallahi rayuwarta so simple kamar Abba Malik."

Bangaren Kilishi Khaleesa suka shiga tana zaune ta cikin izza da isa ta harde kafa kan kujera.
Suna sallama amman karewa Farouq kallo take wani irin kallon banza da rashin isa.
Yatsina fuska ta yi ta kalli Javed shi kuma wannan fa daga ina?
Kafin Javed ya bude baki zaiyi magana kenan sai ga muryar Janinah sun fito ita da Arham tana fadin,"Aunty Kilishi mun dawo."
[05/05, 6:26 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials

- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-4

Hada ido suka yi da Farouq cikin sauri ta karasa inda yake tana nuna shi da yatsa.
"Kai ne?,sai kuma ta yi wani Murmushin mugunta ta kalli Javed ta ce Yah Javed wannan shi ne bakon naka kenan maddallah ma sha Allah. "
Kilishi ta ce."Au shi ne bakon? Yo ni na ga mutum ne ai gashi nan dai shi ba bature ba kuma ba fulani ba."
Ta karasa maganar tana yatsina fuska.
Javed ya ce,"shi ne mun zo gaisheki ne daman."
Farouq ya ce,"ina wuni? Fatan mun sameku lafiya."

Kanta na gefe ta ce,"Alhamdulillahi yadda kake gani muna lafiya. "
Javed ya kalli Farouq,"mu je ko."
Da haka suka fice.
Ita ko Janinah binsu take da kallo a zuciyarta tana jin dadin cewa babu shakka zata rama marin da ta dau alwashin ramawa.
Kilishi ce ta lura da yadda ta ke wani irin tunani fuska kuma cike fal da annashuwa ta zurngureta.
"Ke lafiya kuwa? Ban gane ba."
Gyara zama Janinah ta yi tana fadin,"ai tsuntsu ne daga sama gashasshe har gida Aunty Kilishi wannan shi ne wanda na baki labari ya mareni a minna

Na ji dadin ganinsa sosai a gidan nan domin zan samu damar aikata masa abun da yafi mari ma in ninka abun da ya mun.
Lallai sai yasan da cewa ya tabo jin sarauta."
Kilishi ta gyara zama.
"No wonder na ga ni bai wani mun ba sam sam bai kwanta mun gashi nan dai abu kamar ba mutum ba aiko na daure miki gindi kiyi masa yadda kikeso zan tayaki ina bayanki dari bisa dari."
Arham ya ce,"Ayyah Momy ke kike kara daurewa Janinah gindi tana abun da  ba kyau na tabbatar da cewa in an bincika wannan tsiwar taki kika masa har ya mareki kuma fa shi ba dan

kasar nan bane ba."
Janinah ta ce,"Kai Yah Arham ai kullum daman ni mai laifi ce kuma wallahi ni dai sai na rama ba fashi."
Kilishi ta ce,"Au kai kafi so ana taba mu muna bari? Ai nafiso mutane ko da sunan wani a gidan nan suka ji su razana bare kuma ganinsa da har za ayi tunanin aikata mana wani shirme ba ruwana da shi dan kasar waje ne inma dan kasar cikine muna daidai da shi sai ya san waya taba."
Dariya Janinah ta yi tana rungume Kilishi ,"shiyasa nake kaunarki wallahi Momy."
Arham kam saboda takaici tashi ya yi ya bar dakin.
Su kuwa suka shiga kitsa abun da za su aikatawa Farouq.

Suna fita Javed ya kaisa bangaren Jamaal da junaid sai da suka gaishesu da matansu kafin suka koma bangaren Javed din.
Suna shiga Farouq ya numfasa ya ce,"lallai masarautar nan da girma take."
Javed ya ce,"ba laifi kam gaskiya kuma haka akwai bangaren yan uwa da ba mu karasa ba,yawwa kuma ina so in baka hakuri duk da cewa na san hakan daman zai iya faruwa wacce muka je bangarenta ita ce Aunty Kilishi ita ce yar auta agun hajiya Kaka tana zaune da mijinta da yaranta su uku a cikin masarautar nan Arham shine babba wanda muka ganshi da Janinah kuma su ake shirin hadawa aure sauran mata biyu kuma Ameemah da Amnah suna school a minna Aunty Kilishi bata fiye son mutane ba mussamman bare tana jin cewa a kullum ita sama take da kowa kuma tafi karfin kowa zan iya cewa bata dadin sha ani sam sam gaskiya shiyasa banyi mamakin tarbar da ta yi mana ba."

Farouq ya yi murmushi ya ce,"Ayyah ba komai ai daman kowa da yanayinsa kuma baza a taba taruwa a zama daya ba."

Javed ya ce,"haka ne kam,yanzu barin barka ka huta ka samu barci zuwa gobe da safe sai mu tattauna."

Farouq ya ce,"alright thank you so much ."

Javed ya ce,"kar ka damu an zama daya ai duk abun da kakeso na sha akwai a fridge snacks ma gasu can nasa an hada a dinning in kuma akwai wani abu da kake da bukata let me know sai da safe. "

"Okay Allah ya tashe mu lafiya."
Javed ya fada.

Dake bangaren nasa babba ne bed room biyu ne da falo ya shiga dayan ya bar Farouq a dayan.

Sai da Farouq ya yi sallar Isha kafin ya dauki waya ya kira Maah.
Cike da zumudi ta amsa kiran tana fadin,"Yan nigeria fatan an isa lafiya? Ina ta tunaninka ina so

in kira sai kuma nace kila baka samu nutsuwa ba kar in takura maka."
Farouq ya ce,"Wallahi kuwa na dan jima da isa ma kawai zaman ne ban samu ba sai yanzun fatan kina lafiya?"

"Lafiya lau,ka dai ci abinci ko? Kuma ina fatan babu wata matsala."
Maah ta fada.
Farouq ya ce,"ina lafiya lau kuma na ci abinci na koshi sosai kuma babu wata matsala."

"Ma sha Allah Alhamdulillahi haka na ke son ji,ka tabbatar kana kula mun da kanka ka ji Dan albarka kuma kar ana wasa da sallah da azkar duk da cewa na san ba ka wasa da ibada sam sam amman a kara rikewa da kyau,ina nan ina tayaka da addua da fatan nasara,Ubangiji ya tsare mun kai ya kare mun kai daga sharrin mutum da aljan aduk inda za ka kasance."

Farouq ya ce,"Amin amin ya Allah Maahnah Adduarki da fatan alkairinki da ke biye dani a kullum ba zai taɓa bawa wasu damar cutar dani ba,ina alfahari da kasancewarki mahaifiya a gareni,Ubangiji ya kara miki lafiya da nisan kwana kuma ibada In sha Allah ina turbar da kika daurani babu wasa ko kadan."

Maah ta yi ajiyar numfashi kafin ta ce,"Yawwa Darling kuma kuma ana barci da wuri ban cewa za a kwana akan Internet. "

Dariya Farouq ya yi ya ce,"Okay Maah I love you,Gudnight."

Maah ta amsa da,"I love you to Nighty Night Byee."

Kafin suka katse wayar.

Shiga Group dinsu ya yi na 5stars
Suka yi masa sannu da hanya kafin sai ga kiran Zeeyter ya shigo wayarsa.
Ta ce,"Friend bro ya ake ciki ne? Fatan ka sauka lafiya."
Farouq ya ce,"lafiya lau gimbiyata,kamar ko kinsan ina tunanin kiranki kenan."
Zeeyter ta ce,"aiko gashi na rigaka,ya ake ciki ne akwai alamun nasara kuwa?"

Farouq ya ce,"Ehto ina jin hakan a jikina kuma ina fatan hakan dai."

"Ka sa aranka akwai nasarar ka bawa Ubangiji yaƙini sai ka ga ya tabbatar da abun da ba ka taɓa zato ba,ka rokesa cike da yaƙin samun abun da kake nema kuma kasa aranka tamkar ka samu babu shakka Ubangiji shi ne mai badawa kuma shi ne mai hanawa ina ji araina komai zai zo da sauki,ni dai babban buri da fatana duk yadda za ayi kar ka karaya kuma kar ka fidda tsammani daga rahamar Ubangiji ." Zeeyter ta fada.

Farouq ya ce,"Ta ya ma zan karaya bayan ina da ke jarumar jarumai Yel? Dadina da ke wani lokacin akwai guntun hankali ko da yake ina ga mijinki ne yake sammiki."

Dariya Zeeyter ta yi ta ce,"Za ka sani zan yi maganinka Oyaa Sai da Safe Mijina na bukatata."

Farouq ya ce,"Umm Cingom ba to Allah tashe mu lafiya."
Kashe wayar suka yi duka suna dariya.

Wajen karfe biyu na dare ne sai da Farouq ya yi alwala ya yi nafila kafin ya kwanta.

Washegari da safe
Bayan ya yi wanka za akai masa breakfast Janinah ta ce ita zata kai masa har da rawar jiki ta karbe a hannun masu aiki.
Ya fito daga wanka ke nan yana zaune daga shi sai towel.
Ko sallama ba tai ba ta kutsa dakin kawai da ke bai rufe kofar ba turawa ya yi.
Motsin da ya ji ne yasa shi daga kai.
Ta saki wani munafikin murmushi ta ce,"ga abinci nan an kawo sai a zauna aci ko don na tabbata wannan ko a malaysian ma kila dan aiki ne ko mai gadin gida."
Murmushi kawai Farouq ya yi bai kulata ba ya ci gaba da goge ruwan da ke jikinsa da towel din.
Da ya ji shiru a tunaninsa ta fita.
Sai kawai saukar mari ya ji a kumatunsa.
A razane yago da jajayen idanunsa har ta isa bakin kofa tana fadin,"Daya kenan ko ince kadan ka fara gani don wallahi Allah sai na yi ma abun da zai saka zubda hawaye kamar yadda nima kasani zubarwa."
Tafasa zuciyar Farouq ta fara,ya ji aransa ya bita ya yi maganinsa wani bangaren kuma zuciyarsa na basa hakuri da dannesa.

Tana daga bakin kofa
Ta yi masa wani dogon tsaki tana fadin,"mai gadi kawai."
Kawar da kai Farouq ya yi zuciyarsa cike fal da sake-sake.

Tana fita ta ci karo da Javed da mamaki ya kalleta,"Janinah ke kuma me ya kawo ki nan?"
Inda inda ta kama can kuma sai ta ce,"ansa su talatun aikine shi ne nace bara in kawo wa bakon breakfast dinsa kar ya gaji da jira."

Javed ya ce,"okay shikenan kin kyauta."
Ya wuce dakin da Farouq yake.
Yana shiga yaga yanayin Farouq ba yadda ya bari.
"Ya dai? Ba dai yarinyar can bane ta maka shirme."
Javed ya fada cike da zakuwa.

Murmushin dole Farouq ya yi ya ce,"aa fa sam kaina ne na ji ya fara ciwo na sha magani kuma naji kamar karuwa yake."

Javed ya ce,"Ayyah Sorry kila gajiyan hanya to ka karya in mun fita sai mu fara bi ta asibiti."

Farouq ya amsa da ,"Okay tom."
Abincin ya ci bayan ya gama ya ce,"To mu je in gaida amaryata kafin mu fitan ko."
Bangaren hajiya kaka suka nufa.
Bayan sunyi sallama ta amsa Farouq ya ce," Tsarugu anu." (wai yana nufin ina kwana da nupanci)

Dariya Hajiya Kaka ta yi ta ce,"Ai kaine Tsarugu anu din wato kai a dole ka fara iya nupanci."
Farouq ya yi dariya,"Yo ina gudun yellow card ba dole ba."
Hajiya kaka ta ce,"To Tsaragi Anu ake cewa ka rike da kyau."
Farouq ya ce,"Anyi an gama Yan Maya tsaragi anu."
Hajiya kaka tayi dariya."lafiya lau,kofo eze anu (ya ka ke)."

Farouq ya ce,"Lafiya lau kawai amsar ce dai sai naje na kara koyowa amman fa ina fahimta."
Dariya suka yi duka.
Janinah ce ta shigo da sauri hannunta dauke da bowl ga dukkan alamu farfesun nama ne mai romo.
Gefen Farouq tabi da niyar tunkude kafadarsa.
Ya yi kaman bai ga tana zuwa ba ya sa mata kafa ta kasa daga ita har bowl din sai gasu kwance shaɓe-shaɓe kan tais farfesun kuwa ya yi mata fenti domin bowl din kifewa ya yi a daidai setin fuskarta.
[06/05, 6:26 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace

- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-5

Ya ji ya shigan mata ido gashi farfesun da zafi.
Wata irin karya ta sake.
"Wayyo Allahna wayyo na shiga uku,idona,fuskata."
Kau da kai Farouq ya yi kamar bai san me ke faruwa ba.
Da sauri Javed da Kaka tare da mai aiki suka yi kanta.
"Subhanallah Janinah sannu Javed taimaka adagata aje ban daki a wanke fuskar in kuma da matsala a kira BabanGanye ko da taimakon da zai iya bata."
Sai a lokacin Farouq ya tashi ya karasa wajen shi ma yana fadin,"Ya ilahil alamina garin ya ya haka kuma sannu ko."
Toilet suka shiga da ita aka wanke mata fuskar amman duk da haka idanunta zafi yake yi mata haka ma fatar fuskar domin farfesun yaji kayan yaji matuka.
Hannunta na kan fuskar tana fadin,"wallahi radadi yake mun Yaya Javed zafi sosai kamar an zuba mun barkwano." Ta karasa fadan suna zaunar da ita kan kujera.
Hajiya Kaka ta ce,"To a kira BabanGanye ba zai rasa abun da zai shafa mata ya dauke zugin ba."
Caraf Janinah ta ce,"cab wallahi gwanda ma abarni inta jin zugin yazo ya wani zubamun abubuwa masu wari a fuska,wai ku gidan nan ba dama akai mutum asibiti sai ace sai dai wani BabanGanye saboda mu muka yankewa Gargajiya cibiya."

Hajiya Kaka ta ce,"ungo nan kinci gidanku yo ba dan su BabanGanyen ba ai da baki girma cikin walwala da karfi haka ba,tun kafin kizo duniya kika shan kayan ganye da itacuwa,Javed maza zai ka kira wo mun shi."

Kallon Javed ta yi ta ce,"Yah Javed Please ni abari kawai. "

Wani kallo ya bita da shi ba tare da yace komai ba kawai ya fice.
Shi ko Farouq na zaune yana danna wayarsa kamar ma bai san me ake yi ba.

Kai tsaye Javed ya je ya kira BabanGanye dake a cikin masarautar duk masu magungunan gargajiyan suke.
Da buhunsa yazo kuwa cike fal da kaya dake Javed ya fada masa abun da ya faru.
Yana zuwa ya baje yana fadin,"ai Hajiya Kaka wannan babban al'amarine in ba ayi saurin sanya tsari ba sai ya jawo mata matsala cikin kwayoyin hallitar fuskarta da cikin idon."

Hajiya Kaka ta ce,"Babu shakka ai shiyasa na ce a kira mun kai cikin gaggawa."

Ita dai Janinah sai cuna baki take tana kananun maganganu.
Shiko BabanGanye tuni ya hada kwamacalarsa kayen da itace da wani irin ruwa ya fara shafa mata a fuska sannan sauran ya mika mata yana tasha."
Wani irin kallo Janinah ta bisa da shi tana fadin,"ni ba abun da zansha abarni ma inji da daddawar da ka raƙafa mun a fuska wallahi har amai nake ji."

Hajiya kaka ta ce,"Ko ba amai ba? Aa hanjinki kike ji zai fito ki waje wannan bajajjen bakin naki ki kurbe tun muna mu biyu kafin in mai martaba ya ji labari."
Tana jin batun mai martaba tuni ta amshe ta rufe ido ta kwankwaɗe domin ta san sarai mai martaba na jin labari ba za ta ji da dadi ba.

Haka ta sha ba don taso ba tana gyatsine fuska.
Farouq na kallonta dariya na son suɓuce masa ya make yana fadin,"aiko dai gwanda aka shafa magani kar fuskar yar budurwa ta dagargaje abata mai gadi."
Wata irin harara ta bisa da shi.
Hajiya Kaka ta yi dariya.
"Ai wannan ba dai mai gadi ba sai dai aba almajiri."
Duka suka kyalkyale da dariya.
Wani irin takaici Janinah ta ji aranta ta gama kula cikin fushi ta tashi fuuu ta fice daga falon cike da ɓacin rai.

BabanGanye ya mikawa Hajiya Kaka sauran hadin da ya shafa mata a fuska ya ce,"Hajiya Kaka a ajiye wannan zuwa safe ta dan kara shafawa don naga yanayin fatar ta sauya kuma ga dukkanin alamu ruwan dabgen ya shiga cikin ruwan idanunta."
Hajiya kaka ta bude baki.
"To fa ka ga kuma a haka ja'ira ke son wasa da lafiyarta ita zata nuna mana boko wai aje asibiti."
BabanGanye ya tashi yana fadin,"Yoo ai yaran zamanin yanzu ba ra su gane bane abun da su kansu asibitotin da itattacuwa da ganyayyenki mu suke hada nasu maganin tare da karin bulaguronsu."
Hajiya kaka ta taɓe baki,"ai kuwa dai."
Daura buhunsa ya yi aka ya  fita.

Javed ya kalli Farouq ya ce,"Oga mu tafi ko."
Karaf Hajiya Kaka ta ce,"Ah ku tafi kamar ya zan yi hira da sabon mijina dan kwalisa."
Farouq ya ce,"Wajen aiki zamu je Yan Mata amman na miki alkawari ina dawowa anan zan dira."

Hajiya Kaka ta ce,"to ai shikenan a dawo lafiya,Ubangiji ya ba da sa'ar abun da aka je nema."
Farouq ya amsa da ,"Amin tsaraba me zan kawo miki?"

Hajiya kaka ta ce,"Da Goro da wannan abun sanyin yaran iskirim yake ko me?"
Javed ya katseta da fadin,"Hajiya Kaka ba an hanaki shan Ice cream dinnan ba?"
Harara Hajiya Kaka ta bisa da shi kafin ta ce,"wato ku kusha dadi ni kuma in mutu ina cin goro da garin goruba to ahir dinka sai na sha Mijin a siyo mun iskirim ka ji ko."

Dariya Farouq ya fara yana,"Au wai daman Ice Cream ne iskirim din Hajiya Kaka? Kice inzo in zauna darasi biyu zanna koya ga turanci ga nupanci."

Hajiya Kaka ta kyalkyale da dariya har sai da wawulun bakinta ya bayyana tas.
Ta ce,"Babu shakka je ka dawo yau zan koya ma is me is you is turanci."
Dariya suka yi duka.
Ganin lamarin kaka ba mai karewa bane Javed ya ce,"Hajiya Kaka kinga sai mun dawo."
Farouq ya ce,"sai mun dawo yan matana. "
Duka suka fita suna dariya.
Kai tsaye makarantar Javed suka nufa.

Dake babu nisa sosai cikin mintuna goma suka isa Makarantar da tamabarin makarantar suka fara cikin karo mai taken DIGITALCRAFT.
(Transforming Ideas Into Digital Reality)
Makarantace ta kwamfuta da ke horar da matasa ilimin kimiya mussamman bangaren computer,yadda zasu gina shafukan yanar gizo (web development)
Zane-zane na hoto da kirkiran tambura (graphics design)
Bayar da horo mai karfi
Kan tsarin kare kwamfuta da hanyoyin sadarwa daga hare-hare da kan iya lalata ma'adanan sirri (Cyber security) da kuma hanyoyin yin kasuwanci ta intanet.
Sai yanzu sabon horon da Farouq zai ja ragamar badawa wato aiki na haɗa kwamfutoci da sauran na'urori,raba bayanai da kuma samar da ingatacciyar hanyar sadawarwa (Networking).

Tsari da yanayin makarantar ya birge Farouq sosai mussamman yadda dakunan karantun suka kasance dukkanin dalibai suna da kwamfuta da suke amfani da ita kuma ga dukkanin yanayinsu ana tabbatar da cewa sai sun samu kwarayewar aiki da kwamfutar.

Kallon Javed ya yi bayan sun gama zaga makarantar sun dawo office dinsa ya ce,"yanayin tsarinku gaskiya sun birgeni sosai har na ji sha'awar bude irinta a malaysia."
Javed ya yi murmushi,"na tabbatar da cewa zaka iya bude mafiyin hakan ma na yarda da kai."

Shi ma murmushin Farouq ya yi ya.
Javed ya kara da fadin,"yanzu ka dan huta akawo mana shayi mu sha don nasan rayuwar ture sai da shayi zuwa 11:00am zamu gana da dalibanmu kuma yanzu 10:30."

Dariya Farouq ya yi ya ce,"wato rayuwar turai sai da shayi to ai shikenan."
Bayan an kawo masu shayin sun sha 10:55 suka fita zuwa babban hall din makarantar.
Zaune matan suke dukanninsu sanyi da riga wacce aka rubuta DIGITALCRAFT a gaba da tambarin makaranta a gefen dama gefen hagu kuma tambarin NACOSS wato National Association Of Computer Science Student sannan a bayan rigar kuma aka sanya sunan kowacce a jiki.
Karamin hijabi fari da kuma bakin wando rigar kuwa daman blue black ce ga dukkan alamu makarantar ce ke tadar da komai domin komai nasu sak iri ɗaya kuma ba karamin kyau da haskawa suka yi.

Farouq ne ya fara yi masu jawabi.
,"Welcome, Students!

My name is A. Umar Farouq, and I’m from Malaysia. I am here to collaborate with DIGITALCRAFT under my team’s five-star company to provide you with training and knowledge in my field of Computer Science.

Da farko dai bara in baku shawarwari da nake tunanin zasu taimaka mana a wannan tafiyar har ma da rayuwarmu duka.

Always Ask Questions
Kar kuji tsoron yin tambaya aduk lokacin da baku fahimci wani abu ba,haka kuma
Practice coding
Adadin yadda kukata maimaita yadda zakuyi saurin iyawa da kwarewa
Work with others
Ku kasance kuna da hadin kai wajen yin aikin gayya yana taimakawa sosai domin cimma nasara
Stay organized
Kar kuyi wasa da lukutanku ku kasance masu tsara komai akan lokacin da zai tafi cikin tsari.
Don't give up
Karantar ilimin na'ura na da wuya amman kuma yana da matukar dadi tare da sakamako mai kyau indai an samu sadaukarwa.
A karshe ina jaddadda muku cewa kar ku manta kasancewarku Yara Mata Iyayen wasu a nan gaba karatun ku na da matukar muhimmici ga rayuwarku,iyalanku har ma da al'umma gabadaya.
Allah ya bamu sa'a kuma yasa an fara asa'a ina yi muku fatan alkairi sannan zan fara da bada aiki inaso kowacce a cikinku ta je ta yi bincike akan Networking gobe In sha Allah zamu fara tattaunawa."
Cikin fara'a da jin dadin jawabansa suka fara tafa masa tare da yi masa godiya.

Komawa office ya yi shi kuma Javed ya ci gaba da gabatar masu da abubuwa da tsare tsare.

Wayar Javed ce ta fara kara dake ya bari a office din Farouq ya share ya ci gaba da danna wayarsa ya ga kiran yaki karewa yana katsewa wani na kara shigowa.
Daukan wayar ya yi yana dubawa Yaga Sister Janinah.
Tsaki ya yi ya ajiye wayar yana "ashe wannan mara kunyar yarinyar ce ma."
Ci gaba da kiran ta yi da ya ga bata da alamun dainawa sai ya amsa wayar ya kara a kunne yana fadin,"....
[07/05, 6:25 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240

*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-6

"Hello, he's not around. He's a bit busy. You can call him later, okay?"
Ya karasa maganar yana kokarin datse kiran.
Wani irin dogon tsaki Janinah ta ja tana,"Mtswwww Rubbish Who says you must pick up the call? bana son shisshigi  da neman gidin zama wallahi."
Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Ayyah Ashe mai fuskar ambaliyar romoce,ya fuskar? Ina fatan dai da sauki? Sannu ko."
Ya fada cike da mugunta.
Katse wayar ta yi ba tare da ta ce komai ba tsabar takaici.
Ta kalli Kilishi ta ce,"Kin ga Aunty Kilishi barin wayarsa ma ya yi fa gun wancen bakon kuma ina so in lallaɓashi ya karbo mun wani cream ne a asibiti in zai dawo don wannan abun BabanGanye tunda ya maka mun har na wanke fuskata bata daina mun warin nan ba duk a tsarge nake ko fita ba zan iya yi ba."
Kilishi ta ce,"Miye na tada hankali ga Arham nan ki kirashi ya tawo miki da shi cikin sauki."
Janinah ta taɓe baki,"Umm Aunty Kilishi Yaah Arham dinne fa kin san shi ya cika tsari shi ma yanzu sai ya fara mun wasu jawaban da ban sani ba."
Kilishi ta kalleta ta ce,"Haba Janinah karki manta fa shi ne wanda zaki aura in tun yanzu baki koyi yadda zakina mu'amulantarsa ba in anyi auren ya za kiyi? Namiji fa a tafin hannu Mace yake in kinso kuma kin isa cikakkiyar Mace zaki iya juyar da Arham yadda kikeso yanzu zan kirashi ya tawo miki da shi amman daga yau kar in kara ji kuma kar in kara gani inaso duk wani abu da kike da bukata ki fada ma shi kai tsaye."

Janinah ta ce,"To In sha Allah Aunty."

Kilishi ta gyara zama,"Yawwa Yarinyar kirki,kin fara bani labarin wancen mara kirkin bakon ina fatan dai kin masa marin da ya ji a jikinsa."

Janinah ta ce,"Sosai fa sai da na sace shi naga alamun bai sani irin abun da mutum zai ji ba zato ba tsammanin nan kawai sai jin saukar mari ya yi a fuska,amman ni fa duk da haka hankali na bai kwanta ba tunda bai fara jin shakkata ba ina so in masa wata mugunta ta mussamman yadda ko mai irin sunana ya ji sai ya gudu ya bar wajen karshen ya kwashe kayansa ya gudu a masarautar nan ba shiri."

Dariya Kilishi ta yi ta ce,"Wannan shine gado kuma da kika tashi gadonma gani nake kina so ki fini ki danne ni,to Allah ya baki sa'a da nasara kamar kullum dai in kina neman wani taimako kofa a bude take."

♡♡♡
Javed cike da farinciki ya yi Daliban barka da zuwa tare da jawabai masu ratsa zuciya.
,"Kar ku ga cewa wannan karatun da za kuyi kyauta ne kuyi tunanin wasa da damarku ina mai tabbatar muka da cewa tamkar wasa da nasarorinku ne domin kuwa kasancewarku anan ma kadai babbar nasara ce kuma jigo sannan bango ga rayuwarku,yadda duniya ta waye ko ince take kan kara wayewa a komai yanzu Kimiya da fasaha ke aiki,ku rike maraicinsu ku bude kwakwalanku da idanuwanku ku mai da hankali kan neman ilimi,shi zai zama madogara a gare ku shi zai zam haske a gareku rayuwarku da ta ma al'ummar da ke tare da ku kamar yadda A.Umar Farouq ya sheda maku nima a karshe ina mai yi muku fatan alkairi Ubangiji ya bamu ikon amfana da juna."

Yana gama nashi jawabin shi ma ya bi Farouq ya barsu da sauran Lectures din.
Yana shiga Farouq ya mika masa wayarsa yana fadin,"Janinah ta kiraka."
Ajiye wayar ya yi yana,"rabo da rigimammiyar yarinyar nan yanzu zamu duba yadda tsarukan lectures din zai kasance."
Farouq ya ce,"Okay."
System Javed ya bude suka shiga dubawa Farouq ya danyi masu gyaran abun da yake tunanin za a gyara.
Sun jima sosai har suka yi sallar azahar suka idar suka ci abinci suna kan aikin sai wajen karfe biyar kafin suka kammala.
Zasu tafi gida Farouq ya ce,"Mu bi ta inda zan siyawa Yan Mata iskirim dinta fa."
Javed ya ce,"wai kai yanzu biyewa hajiya Kaka za ka yi ina ita ina shan wani ice cream. "
Farouq ya ce,"Au shi ice-cream din an zabi wanda zasu sha ne? Ku bar tsohuwa ta ji dadin rayuwarta please ni muje."
Aiko hakan aka yi sai da suka je THE ICE CREAM LAB, ya siyawa Kaka suma sun siya nasu kafin suka dau hanyar gida.

Suna zuwa kuwa bangaren Hajiya Kaka suka fara wucewa.
Farouq na mika mata leda ta washe bakin nan da wawulonta tana,"Ah lallai yanzu ne na san na yi miji dole inyi maka kwalliya ka ji dadi irin wacce na ke yiwa Mai Martaba Allah jikan rai sai kuji yana "Uwar Gida Marurin Zuciya ganinki ke kara karfin zuciya." Wani lokacin fa inai wanka na yi kwalliya sosai muna hada idanu sai fadawa sun rikesa domin tsabar farinciki sai ya fara kokarin faduwa yana,"Ya Allah ni ko a aljanna ka bar mun ita,ita kadai nake so."
Dariya suka yi duka Javed ya ce,"Yana cen yana jiranki ai gashi kuma kin masa kishiya da wani."
Kaka ta ce,"Yoo ai tun yana raye yake da kishiyoyi shiyasa yake dagewa ganin yafi kowa,shi fa ba ruwansa da wata sarauta in yana gabana har rawa yake tirka mun irin wanda yan indian nan suke."
Ta karasa maganar tana kwatantawa daga zaune.
Don Dariya Farouq da Javed na tsaye sai da suka zaune na.

Farouq ya ce,"Ah lallai Mai martaba ya iya diga soyayya dole nima in dage in kwace zuciyarki ras."

Hajiya Kaka na kokarin bude Ice cream tana,"Aa fa sai dai abaka rabin zuciyar abar mai rabi don in bani akwai matsala yana mutuwar rayuwar sona."
Ice cream dinta ta fara mamula da harce kamar abinci.
Javed ya ce,"Za a shiga salla ka ga in muka biyewa wannan Matar taka sai mu rasa."
Ficewa suka yi masallaci Hajiya Kaka an samu abun nema ko kallon inda suke batai ba har suka fita daga bangaren nata.
A masallacin suka hadu da Abba Malik.
Bayan sun idar yake cewa,"Aiko inata so in zauna abani labarin Malaysia ashe kunje gaida Madam lokacin ban dawo ba."
Javed ya ce,"Eh wallahi."
Abba Malik ya ce,"To yanzu ba kwa komai muje can mana sai mu ci abincin dare tare daga nan sai mu yi hira abani labarai kasanni da son jin labari."

Murmushi suka yi duka.
Farouq ya ce,"Ba matsala Abba."

Bangarensan kuwa suka bi shi.
Bayan sun zauna a falo sai ga Momy Zulaihart matarsa ta fito.
Cike da fara'a take fadin,"Ah yau manyan baƙi garemu a gidanmu ashe to barkanku dai maraba lale."
Gaisheta suka yi ta amsa cike da sakin fuska.
Abba Malik ya ce,"Nace bakon Malaysia yazo mu ci abinci tare mu yi hira ."
"Ya kamata dai kam yanzu bara insa akawo maku abincin in kun gama dole nima in zo in zauna ayi hirar nan dani."
Ta fada cike da zolaya ta fice.

Bayan an kawo masu abinci sun ci sun koshi Abba Malik ya kalli Farouq  ya ce,"Malam Umar ya ka ga dan garin namu ne ko ince kauyen namu?"

Farouq ya ce,"Abba ai nan ya zarce kauye banyi tunanin zan ga hakan ba gaskiya garin ya birge ni har ina cewa Javed na ji sha'awar gini anan sannan kuma yadda na ga ana ruruta matsalar rashin tsaro a Nigeria nidai tunda na shigo ban alamar hakan anan ba."
Abba Malik  ya ce,"mu kam gaskiya ba mu da matsalar rashin tsaro sam sam Shugaban dake jan ragamar garin nan a tsaye yake  ba a yadda da batun sace-sace ko hare-hare duk abubuwan nan da ake a sauran garuruwan dake kewaye da Nigeria mu bama fuskanta domin a kwanaki ma yan Ta'addan sun turo da takadda mai dauke da sakon suna son shigowa su karya tarihi da ya kafa ya ce da su ba matsala  yana jiransu su shigo,to karshe ma dai koda suka zo garin basu ga Mokwa ba cikin garin nan din suka bi amman daji ya zame masu sai da suka yi nisa har sun fada kanji tukun suka hango mokwa,Babban matsafi ne na karshe amman yana taimakon al'ummarsa kuma yana karesu da tsafinsa a yanzu haka shekara biyu ke nan ba yana fama da lalura bai da ishasshiyar lafiya magauta sun sanya masa hannu an hana shi zuwa sallar idi a yadda aka sheda mana lallai muddin yaje zai iya rasa ransa kuma gaskiya ana matukar kaunarsa al'umma na kukan rasashi domin duk ranar da ya bar duniya mun rasa adilin

shugaba a mokwa.

"Ikon Allah ke nan lallai yana da karfi sosai wannan shi ake kira shugaba mai sadaukarwa kuma na lura yanayin garin nan sam babu yunwa ga dukkan alamu babu tsawallawa a kan kayan hatsi."

Abba Malik ya yi murmushi,"Ai Mai Martaba bai yadda da batun rashin abinci ba ga al'ummarsa ka ga ko boye kayan hatsin da ake a wasu jihohin? Mu nan ba a isa ba domin in ma kunyi za a karba a rabawa al'umma shiyasa kowa yake taka tsantsan mussamman ma dake muna da albarkar noma sosai."

Javed ne ya kalli agogon wayarsa ya ce,"Abba dare ya yi karfe sha ɗaya da rabi  gashi baku gama ba."

Abba Malik ya ce,"Subhanallah lokaci na sauri kuje ku kwanta kam."

Farouq ya ce,"Gaskiya ban so a katse wannan tarihi ba amman dole watarana inzo in zauna a ci gaba mun daga inda muka tsaya."
Murmushi Abba Malik ya yi ya ce,"Baka da matsala In sha Allah akwai shagali ma da za ayi na al'ada kana nan ai zaka gani . "
Sallama suka yi masa kafin suka tafi.

♡♡♡Barci ya gama cin idanun Javed sallama shima yama Farouq ya wuce ya kwanta.
Shi ko Farouq  Nafila ya yi kafin ya dauki system dinsa ya fara aiki,sai wajen karfe uku kafin ya kwanta.
Asuba na yi kuwa da ya tashi yin sallah bai kwanta ba.
System din ya dauka ya shiga bincike....
[10/05, 8:50 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*

Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*



Jin alamar motsin mutum yasa Javed shiga dakin.
Yana shiga Farouq ya yi saurin kashe System din kafin ya karasa gabansa.
Ya daga kai yana binsa da kallo,Javed ya ce,"kai dai kam baka hutu inaga a kullum da kyar in kana samun barcin awa uku zuwa huɗu."

Farouq ya yi murmushi,"Hutu ai ba nawa bane,akwai abubuwa masu mahimmanci da yawa da nake kan gudanarwa kuma hankalina ba zai taɓa kwanciya ba har sai na ga tabbatuwarsu na cimma nasara."

Javed ya yi dariya,"Ai kai kwaro ne Ga ka barawo ga ka adili kodayake ba ace da kai barawo ba tunda kana kwamusowa al'umma hakkinsu ne da manya ƙasa suka danne, nima fa da zan iya lamarin nan naka da na fara anan Nigeria wallahi don muma muna da azzaluman shugabbanni da attajirai da suka danne dukiyoyin talakawa suna gina rayuwarsu da ta iyalansu."

Farouq ya ce,"Mai zai hana?  Tsab zaka iya kuma zan baka gudunmawa wajen tabbatuwar hakan,Duk da cewa ba hanyar kwarai nake bi ba wajen diban dokiyoyinsu ba amman kuma hanyar kwarai nake bi da ita wajen tallafawa mabukata kuma na tabbatar da cewa Ubangiji zai

dubi zuciyata don haka ban taba jin dana-sani ko fatan dainawa ba,muddin numfashi bai bar karakaina a jikina ba zan taba dainawa ba duk wani arzikin da bai taimakon al'umma ko yake danne al'umma idona na zuwa kanshi sai na kwatar masu rabonsu sun amfana  suma sun gina rayuwarsu cikin aminci hakan ba karamin tallafawa yake ba wajen kawar da talauci a kasa ba sai iya ka gwamnati ke da alhakin kula da al'umma ma muma muna da wannan nauyin muddin ana son ci gaba a kowacce kasa."

Javed ya numfasa ya ce,"Gaskiya ne dukkanin bayanka kuma na gamsu da su sannan nima ina bukatar ka daura ni akan hanya amman dai kasan nan ba malaysia ba ne abubuwanmu da bambamci."

Farouq ya ce,"Yeah kuma ka ga ni kowanni mutum indai na taɓa masa dukiya ina tura masa takaddar gargadi kan dalilin da yasa na diba tare da hujojjojina kuma ina basu tsari da dokoki yadda zasuna tallafawa al'umma yadda na tsara ina biye da duk wani motsinsu ta yadda duk wanda yaki aiwatar da abun da na bukata ina iya kara aikata masa mafiyin abun da na yi a farko,to hakan yasa suke shakka suna kokarin bin tsarina ko iya hakanma babbar nasara da galabace a gareni ìna sanya su yin alkairi ga al'umma  ko da basu yi niya ni in samu lada suma su samu kuma ubangiji ya kara buɗa musu to amman kuma kamar yadda ka fada Nigeria da kamar malaysia zan danyi bincike mu ga yadda abun zai iya kasancewa."

Javed ya ce,"Yes My Boss da ana iya hallarta sata da nace wannan satar hallartacciya ce tunda da nufin alkairi ake yinta."

Farouq ya yi murmushi.
Javed ya kara faɗin,"yanzu bara in barka ka ci gaba da aikinka kar in dameka."
Ya fada yana dariya ya fice.

Yana fita da sauri Farouq ya dago system dinsa ya kunna.
Wani page ya shiga wanda aka yi rubuta NIGER STATE/MOKWA
a kasa kuma GIDAN SARKIN AL'ADU.
Sauran rubutun da ya yi a kasan duk da programming language wanda sai cikakken Computer scientist ne kadai zai iya fahimta.
Shiga ya dunga yi yana ta duba wasu abubuwa kafin daga karshe ya kulle wajen karfe bakwa na safiya.
Cikin sauri ya karya domin 8 daidai zasu fara Lectures kuma Farouq ne farko.
Kafin ya gama Javed ya fito,yana gamawa suka fice ko Hajiya Kaka basu je sun gaida ba.

Kai tsaye lecture room Farouq ya nufa inda student duk sun hallara shi kadai ake jira.
Da tambayoyi ya fara masu kan binciken da yace su fara kan cybersecurity.
"Ko akwai wacce zata iya fadamun mene ne Cybersecurity atakaice?"
Kusan mutane biyar ne suka daga hannu ya tashi ta farkon ta ce,"Hanyoyin sanya tsaro ga na'ura."
Sanyawa ya yi atafa mata kafin ya kara tada wata ma ta ce,"Yadda ake kula da kwamfuta

gudun samun hari."
Ita ma sawa ya yi aka tafa mata bayan sun zauna duka ya ce,"Ehto duk kunyi kokari yanzu amman akwai bukatar cikakken bayani kowacce ta kunna system dinta ta login PDF dinmu na Cybersecurity daman ai jiya ance an koya muku ko?"
Suka amsa da ,"Yes Sir."
Cike da zumudi dukkaninsu suka bude systems din suka shiga PDF din gwanin sha'awa.
Farouq ya ce,"Are we ready?"
Nan ma suka kara amsawa da ,"Yes Sir."
Cikin kwarewa Farouq ya fara jawabinsa.
Da farko shin mene ne CYBER SECURITY?
Cybersecurity shine tsaro na yanar gizo yana da alaƙa da kare kwamfutoci,hanyoyin sadarwa,kiyaye bayanai ta hanyar shiga ba bisa ka'ida ba ko ba da izini ba,kawar da hare-hare,lalacewa ko sata,kunshi fasahohi da hanyoyi tare da ƙa'idoji da aka tsara don kare bayanai tare da tabbatar da ingancinsu,sirrinsu da samuwarsu.
Wannan shi ne cikakken bayani dangane da Cybersecurity ina fatan kowa ya fahimta?
Sai da ya tabbatar da duk sun fahimta kafin ya ci gaba.
"Yanzu za mu wuce gaba,Akwai muhimman abubuwa na tsaro a yanar gizo da ya kamata ku sani kamar su.
Network Security
Kare hanyoyin sadarwa.
Application Security
Sanya tsaro ga aikace-aikace da kubutar da su daga rauni.
Information Security
Kare ingancin da sirrin bayanai a dukkan na urori da hanyoyin sadarwa.
Endpoint Security
Tsaron na'ura guda dake samun damar shiga hanyoyin sadarwa na kamfani.
Cloud Security
Shi kuma shi ne tsaron gajimare wanda ake kare bayanai da aka ajje cikin yanayi na gajimare.
Sannan akwai
Disaster recovery
Incident response
Regulatory compliance wa innan kenan
Sannan ina so ku sani cewa tsaro na yanar gizo yana da matukar muhimmici a wannan rayuwar yayin fa barazana ke ci gaba da wanzuwa yana da kyau ga murane da duk wasu kamfani ko kungiyoyi da su kasance masu tsaurara tsaro da ka idoji masu karfi ga dukkan wani abu da ke mallakinsu a yanar gizo." yana ka karasa wannan maganar ya ce,"ko akwai masu tambaya ko abun da baku gane ba?"
Caraf wata ta daga hannu.
Ya bata damar tashi kafin ta ce,"Sir Amman a binciken dana fara na ga akwai yadda mutum ke koyan yadda zai kai kutse ko hari ga wani shin ba za a koya mana bane."

Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Ke ko Meemah wa kikeson kaiwa hari tun yanzu? Za a koya maku amman hakan ba wai yana nufin ku koya ku dunga cutar da mutane bane,za a koya muke

domin karin tsaurara tsaro tare da fahimtar tsaron da hanyoyin da ake iya bi don ruguzawa amman ba don cutar da kowa ba,kuma ba mu zo bangaren ba tukunna muna tafe zamu zo In Sha Allah amman a yau dai zamu tsaya anan."
Godiya Meemah ta yi masa cike da gamsuwa da bayanansa ta zauna.

Cikin jin dadi Farouq ya kammala masu lectures dinsa na ranar kafin ya fita.

Can yamma suna zaune da Javed ya kalli wayarsa ya ce,"Oga na manta fa in sheda ma yau muna da zaman babban falo da dare duk ranar Friday haduwa ake aci abincin dare dukka family a babban falon mai martaba sannan muna sanya kayan gargajiya a daren za aci abinci tare ayi wasa da dariya in mutum na da matsala ko wata magana da yake son yi yana iya yi duk a gun."

Farouq ya ce,"Ma sha Allah hakan ba karamin kara dankon zumunci zaiyi ba to yanzu har ni zan iya shiga? Zanso in ganni cikinku ko zanji kwatankwacin yadda mutane suke jin yayin da suka gansu cikin danginsu."

Javed ya ce,"Haba dai,ai ba kwatankwaci za ka ji komai zaka ji duk yadda kowa ke ji na sha fada ma always feel like home please. "

Da hirar suka yi sallama da sauran Staffs din kafin suka tafi gidan.
Sai da akayi sallar isha suka nufi babban falo.
Suna zuwa kuwa kowa ya hallara hatta hajiya Kaka.
Tana ganin Farouq ta fara washe baki tana,"Mijin aiko yau inata nemanka."
Karasawa gabanta Farouq ya yi ya zauna yana,"aiko gani nan yan mata kaina kasa."
Duka suka fara dariya.
Mai Martaba ne ya yi gyaran murya da yasa dukkaninsu yin shiru.
Janinah da Kilishi suna ganin shigar Farouq suka fara kuskus.
Karshe dai Janinah ta tashi ta fita kafin ta dawo suna kallon juna suna sakin murmushi.

Abinci aka fara kawowa a ƙa ida jikoki  maza faranti ɗaya ake masu su ma yara matan da matan jikokin ɗaya,na iyaye ma ɗaya.
Mai martaba kuma shi da Abba Malik da Hajiya Kaka.
Hakan kuwa ya kasance.
Sannan a ƙa ida ba a surutu lokacin da ake cin abincin hakan yasa gabadaya falon ya yi shiru.
Suka yi bismillahi aka fara ci.
Tuwon shinkafa ne miyar wake wanda yana daya daga cikin abincinsu na gargajiya da suke ji dashi.
Falo ya yi tsit
Kowa yana cin abincinsa cikin nutsuwa karaf cikin Farouq ya fara kugi.
Kallon kallo suka fara.
Ya make ya ci gaba da cin abincinsa.

Can da cikin ya yi masa wata irin murɗawa da kuka bai san lokacin da aguje ya tashi ba yana.....
[12/05, 10:21 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials

- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-8

Yana gudu ba, kai tsaye ya faɗa bayi.
Cikinsa ya riga ya burga kafin ya ƙarasa toilet ɗin har wandonsa ya fara ɓaci.

Janinah da ta kalli kowa anyi tsuru-tsuru ta haɗa ido da kilishi  tuntsirewa da dariya suka yi har da riƙe ciki.
Cike da ɓacin rai da fushi mai martaba ya yi gyaran murya.
Ba shiri  suka guntse dariyar suka yi nutsuwar dole.

Cike da izza ya fara magana.
"Javed garin ya ya ka kawo mana mashirmaci irin haka? Me hakan da ya yi yake nufi? Ni fa ba wani son  alaƙa da turawan nan nake ba."
Ya yi shiru ya na jan numfashi kafin ya ce. "Ni ban gama yarda ma yana sallah ba, domin yawanci duk 'yan ƙasashen wajen nan ko sun ce su musulmai ne, a baki ne kawai ba su cika yin addinin ba."

Kan Javed na ƙasa ya ce. "Ranka ya daɗe a yi mana afuwa, amman ga dukkan alamu cikinsa ne ya ɓaci, tunda ba saba cin irin cimarmu ya yi ba, sannan kuma batun ibada gaskiya ba ya wasa da ita sam."

Mai martaba ya ce. "Maddalla! Amman ba hakan ne zai bashi damar  zuwa yana karya mana dokoki da ka'idoji ba, daga yau ba na buƙatar sake ganin sa a duk wani taro ko zama da za a yi har ya tafi, hasali ma ban so ya shiga duk wasu lamura da suka shafi sarautar gidan nan."

Ta ido Janinah da Kilishi suka kalli juna cikin jin daɗi.
Ba wanda ya yi magana sai can Abba Malik ya ce. "Kar ka manta wannan bako ne kuma ya nuna yana sha'awar kasancewa cikinmu aka ce bakonka annabinka, ko ba komai in muka masa halacci zai ji daɗin bayyanawa yayin da ya bar ƙasar nan, kuma ga dukkan alamu ba da son ransa ko da gangan ya yi ba."

Mai Martaba ya ce. "Na riga na gama magana kuma ka san ba na magana biyu."
Hajiya Kaka ta ce, "Da dai an yi masa lamuni yaron na da hankali. "

"Ko da a ce jinin gidan nan  ne zan iya dakatar da shi balle kuma wani bare, kun wani dage kuna son kare shi kun manta cewa maganata ba mai canjuwa ba ce."
Mai martaba ya faɗa cikin fushi yana miƙewa.
Cikin sauri dakaransa suka rufesa har zai fita sai kuma ya tsaya ya ce. "Ba ma shi kaɗai ba, daga yau ba na buƙatar wani bare cikin zaman da ya shafi al'ada." yana gama faɗa ya fice.

Ba abin da Abba Malik ya iya furtawa sai. "Allah ya kyauta."
Shi ko Farouq yana nan zufa ta  jiƙe shi shakaf kamar wanda aka kwara wa ruwa.
Da ƙyar ya rarrafo ya kwanta a kan gado domin ƙarfin jikinsa kaf ya tafi.

Mai martaba na fita da Sauri Javed ma ya bisa ya je gun Farouq.
Yashe a kan gado ya gan shi yana ta murƙususu.
Ƙarasawa ya yi ya riƙe shi yana. "Ya dai cikinka ke ciwo?"
Farouq ya girgiza masa kai alamar eh.
Javed ya rasa ta ina zai fara daga kan da zaiyi sai ga Abba Malik ya shigo.
"Subhanallah ya kamata asamu abashi magani gashi ba ma kusa da asibiti kuma kar abashi maganin gargajiya ya zame masa matsala tunda ba saba sha ya yi ba."
Javed ya ce,"Abba ko dai za a gwada domin jinkirin zai iya zama wata matsalar kuma."
Abba Malik ya ce. "Eh to haka ne kuma, yi sauri ka kira Baban ganye mu ga ko da taimakon da zai iya yi masa."
A hanzarce Javed ya fita ya kira Baban ganye, yana zuwa kuwa wani ruwa ya fara ba wa Farouq ya sha cikin mintuna kaɗan ya fara dawowa hayyacinsa.
Tambayoyi ya fara yi masa me ya faru.
Farouq ya ce,"Ehto na fara cin abinci sai na ji yaji ya yi yawa ba irin wanda na sababa daga nan kawai sai na ji cikina ya fara murɗawa kuma cikin ya yi zafi sosai kamar wuta na ci."

Numfasawa Baban ganye ya yi ya ce. "Ba matsala In sha Allah, wannan ruwan ma da na baka kawai ya wadatar, zan ajiye maka sauran zuwa anjima sai ka ƙara sha, da izinin Allah cikin zai wanku ko ma miye a ciki zai fita, yanzu ka samu ka huta ka ɗan yi bacci ko da zaka farka zuwa anjima."

Abba Malik ya kallesa ya ce. "Sannu ko Malam Umar, Allah ya ƙara sauƙi, ka kwanta ka huta ɗin."
Cikin muryar rashin lafiya Farouq ya amsa "Amin Abba, na gode Allah ya saka da alkairi. "
Ya kalli Baban ganye ma ya ce,"Na gode Baba Allah ya saka da alkairi. "
"Ba komai sannu ko."
BabanGanyen ya fada yana haɗa kayansa kafin ya fita.

Abba Malik ya kalli Javed ya ce,"Sai ka zauna da shi Incase ko zai buƙaci wani abu."

Javed Ya ce,"Okay tom In sha Allah Abba."
Sallama ya yi masu ya fice.
Farouq kuwa wani barcin wahala ne ya yi awun gaba da shi.
Javed ya hau kujerar da ke gefen gadon shi ma ya fara barci.
Karfe biyun dare na yi tsilif kamar an tsikari Farouq ya tashi.
Da sauri ya dauki System dinsa cikin Foldern Gidan Sarkin Al'adu ya fara shiga.
Wasu abubuwa ya yi tickin sannan ya yi kansil ɗin wasu ya yi saving kafin ya shiga Yanar gizo bincike.

Jin motsin da Javed ya yi ya saka shi farkawa.
Yana farkawa ya ga Farouq ya duƙufa kan System sai shiga da fita yake.
Cike da mamaki ya ce,"Ah mara lafiyan ke nan?"
Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Na dameka da mutsu-mutsu ka farka ko? Sorry ko zaka koma dakinka to na ji sauki fa."
Javed ya ce,"Ba wani damu wallahi,amman dai wannan ƙarfin hali ne sai ka ce aikin barin duniya ba za ka kwanta ka huta ka samu ishasshen barci ba?"
"Umm Allah na ji ni kamar wani abu bai same ni ba,gaskiya ban ga laifin mai martaba ba da yake riƙo da al'adu sosai ka ga maganin gargajiyan nan ko kaɗan ban yi tunanin zai yi mun aiki ba, amman gashi cikin mamakina ina ji na tamkar wani abu bai sameni ba, kai ba ma wannan ba ashe kuma kuna da kasurgumin barawo a gari." Farouq ya faɗa.

Da sauri Javed ya ƙarasa inda yake yana,"Kamar ya ? A ta ina kuma?"
Farouq ya ce,"Anan Niger State mana mai kwamushe kudaden mutane amman ba halin ganin address Location ɗin ma da ya bari aka ga Nigern ina ga akwi dalili kuma ban san wani tsari yake bi ba amman dai zan san yadda za ayi mu kulla alaƙa da shi ta yadda zamuji bayanai duk da hakan zai yi wuya."

Javed ya ce,"Ikon Allah yoo ni wannan abun naku ai na kusa in sare ace mutum ba hutu ba lafiya ma bazai huta ba."

Farouq ya yi dariya,"Kai dai ai ragon namijine ne je ka yi barcinka."
Aiko tashi Javed ya yi yana,"Sai da safe ma karasa magana."
Farouq ya daga masa hannu yana ci gaba da danna System dinsa.

Washegari
Karfe Bakwai na safe ya gama shiryawa zasu bangaren Hajiya Kaka shi da Javed ya ji alamar sako ya shigo wayarsa.
Yana dubawa ya ga.
,"Ya dai? Ya Kashin? Ya tsaya ko dai sai an kawo taimako, yau kam na san da kyar ai a iya motswa,KAƊAN KA GANI asha jinya lafiya."
Da number aka turo sakon amman dake yana amfani da tracker yana dubawa ya bayyana masa da details din Jinanah.

Murmushi ya yi yana karanta saƙon.
Javed ya ce,"Lafiya ? Mu tafi ka tsaya kanata kallon waya kana murmushi."
Farouq ya ce,"Oh Sorry mu je ko."
Suna zuwa bangaren Hajiya Kaka kuwa da Janinah suka fara cin karo.
Da mamaki ta kallesa tamkar wanda ba wani abu da ya sameshi.
Karshe ma kallonta ya yi yana sake mata matsakaicin murmushi ya wuce ya shige ciki ya barta da suman Tsaye.
Hajiya Kaka na ganinsa tai rau da fuska,"Ayyah mijin yanzu nake cewa Janinah ta zo ta rakani mu duboka ashe kana tafe,jikin yi sauki ke nan."
Zama ya yi daidai da lokacin da Janinah ta karaso cikin falon ya na kallonta ya ce,"Kin san ba a taba jinin sarauta cikin ruwan sanyi ko da ace wanda ya taɓa shin kuwa shi ma yana dauke da jinin ne."
Hajiya Kaka ta ce,"Kar dai kace mun kuma acen kasar wajen akwai sarauta."
Farouq ya yi dariya kafin ya ce,"Sosai ma ai ako ina akwai jinin sarauta bare ma ni tunda nake da mata sarauniya kuma gimbiya ai dole jinin sarauta ya zagaye jikina."
Dariya Kaka ta yi ta ce,"Lallai kam mijin ba ka da dama  yanzu dai na ji dadin ganinka haka don ni ban shirya takaba ba ga lokacin shagali na karatowa ina so in dau wanka in kashe kala ai nace muje ka sakeni kawai kafin ka mutu."

Suka yi dariya Farouq ya ce,"Wato ma ta ado da kwalliya kike ba lafiyata ba."
Hajiya Kaka ta ce,"Aa fa tunda dai ka ji sauki ka fasa mutuwar to aurenmu na nan gam gam ba motsin komai yawwa."

Dariya suka yi duka.
Farouq ya tashi yana fadin,"Tom mun tafi ayi mana addua."

"Allah ya bada sa'a,aje lafiya adawo lafiya kuma ubangiji yasa muku albarka a dukkanin lamuranku."
Hajiya Kaka ta fada.

Da Amin duka suka amsa Farouq ya ce,"Amman yau ba ke ba iskirim."

Hajiya Kaka ta ce,"Haba Masoyi na har a bada,bari in maku irin na yarenku ma na yan gayu Elubuyu haka ake cewa ko Janinah."
Ta karasa maganar tana kallon Janinah.
Tintsirewa da dariya duka suka yi ba tare da sun bata amsa ba.
Ɓata rai kaka ta yi ta ce,"Dadin abun ma nima ina da yarena ai sai in fada da shi Na mi ve eko (Ina sonka)."

"Na mi ve eko kwo (nima ina sonki) dole a siyo miki iskirim yau kam harda shawarma ma."
Farouq ya fada yana dariya suna fita.
[13/05, 9:57 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear

- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-9

DigitalCraft suka nufa,suna zuwa Farouq ya yi Lectures Room.
Karatu suka kutsa kai tsaye.
Bayan kowacce ta kunna system dinta.
"Yau za mu magana ne akan HACKERS
Hackers mutane ne da ke da kwarewa a fannin kwamfuta da tsare-tsarenta suna bincika salo da tsarin kwamfuta,hanyoyon sadarwa da kuma software don fahimtar yadda suke aiki,suna gano rauninsu da kuma yiwuwar canzasu,sarrafasu ko ma tarwatsasu.
(Hackers: Individuals who use technical skills to gain access, manipulate, or exploit computer systems, networks, or data, often with varying motivations (malicious, ethical, or neutral).)

Sannan sun rabu kashi kashi kamar su:
White Hat Hackers
Sune masu amfani da kwarewarsu dom kare tsarin kwamfuta suna taimakawa kungiyoyi da ma'aikata wajen sanya tsaro mai karfi a kwamfuta da kuma gano rauninta kuma suna bada shawarwarin hanyoyin da za abi domin inganta tsaro da izinin masu na'ura.

Black hat hackers
Waddannan sune masu gudanar da aiyukan cutarwa ta hanyar bin raunin tsaron kwamfuta domin sato bayanai don wata manufa na cutarwa ko kuma tarwatsa tsari da shirin na'ura ba tare da izinin masu shi ba.

Gray hat Hackers
Su kuma wa innan suna tsakanin white hackers da black Hackers sukan iya yin kutse ga na'ura ba tare da izini ba amman kuma ba da niyar cutarwa ba sai dai don duba raunin tsaro kuma su kan yi kokarin sanar da kungiyoyin ko ma'aikatan domin suyi gaggawar Gyara a wasu lokutan kuma sukan iya neman kudi bayan sun gano wasu bayanai.

Wa innan ukun sune jiga-jigai da kan iya aikata komai amman bayan su kuma akwai.

Script Kiddie

Wa innan masu harin basu da kwarewa sosai suna amfani da rubutun da wasu suka kirkira ne don gudanar da hare-harensu.

Hacktivist
Su kuma wa innan suna amfani da hari ne matsayin nuna ra ayi na siyasa yawanci suna kai hari ne kan shafukan yanar gizo na gwamnati ko kamfanoni don nuna adawa da manufofin ayyukan da basu yarda da su ba.

State Sponsored Hackers
Su kuma wa innan gwamnati ne suke daukan nauyinsu suna cikin harkokin leken asiri na yanar gizo,kuma su kan iya sato bayanai masu mahimmanci daga wasu kasashen ko kuma katse muhimman hanyoyin sadarwa.

Phreakers
Su kuma suna maida hankali wajen harin tsarin sadarwa a tarihi suna yin amfani da tsarin waya don yin kira kyauta ko kuma amfani da hanyoyin sadarwa na waya.

Amman karku manta The three main types of hackers to consider are:

White Hat Hackers: Ethical hackers who help organizations improve security.
Black Hat Hackers: Malicious hackers who exploit vulnerabilities for personal gain or harm.
Gray Hat Hackers: Hackers who operate in between, often without malicious intent but without permission.
Dukkanin wa innan guda ukun zamu gudanar da practical kan yadda kowannensu ke gudunar da aiki In sha Allah.
Ina fatan kun gane?"

"Yes Sir." Suka amsa cike da kwarin gwiwa.

Farouq ya ce,"Ko da kwai mai tambaya?"
Kamar kullum Meemah ce dai ta fara daga hannu ta ce,"Sir Ke nan mu mata zamu iya zama white hackers ko black Hackers dinnan nan?"

Farouq ya ce,"Eheen me zai hana? Ka da kiyi tunanin akwai wani abu da ba za ki iya ba don kasancewarki mace muddin ba addini bane ya haramta miki,mata sun fi maza naci da dagiya ma indai suna son abu har sukan zarce namiji kwarewa ka da al'ada tana ruɗarku kuna tauyewa kanku hakki indai abu ba ubangiji bane ya haneku ga aikatawa mussamman bangaren neman ilimi ko dogoro da kai ka da kuyi wasa da shi sam sam kuma In sha Allah kafin in bar kasar nan sai kun zama kwararrun mata na farko da a bangaren na ura kaf nigeria ba iya Niger state ba babban burina shi ne kusa aranku za ku iya."

Tafa masa suka fara yi cike da jin dadi.

Farouq yana komawa office ya tarar da Javed zaune suka shiga hira yake bashi labarin yadda yake jin dadin tambayoyi da nutsuwar da Meemah ta ke yi "Ga dukkan alamu yarinyar na da basira sosai ba laifi."
Javed ya ce,"Gaskiya nima na lura da hakan,ni fa ba don kar ace na cika azarɓabi bama sai ince ni tamun kamar in shiga daga ciki amman kuma inna tuna yanayin gidanmu sai inji ban da kwarin gwiwa hakan yasa ma ni ko tunanin aure ban sa a gaba ba domin ina gudun kada inje in faɗa kogin da zan azabtu kuma in azabtar da 'Yar da mutane."

Farouq ya ce,"Ban gane ba, Ke nan hatta matar aure ma ba ku da hurumin zaɓa sai dai a zaɓa maku?"
Javed ya ce,"Kwarai kuma Mai martaba ne da kanshi yake shedawa mutum ya je ya ga 'Yar wane kaza su sasanta kuma dole sai jinin sarauta,kuma ni sam lamarin sarautar nan bai taɓa birgeni ba shiyasa na ke jin dadin kasancewa da Abba Malik rayuwarsa ba tsanani sam."

Farouq ya numfasa kafin ya ce,"Lallai abun babba ne shawarar da zan baka kawai shi ne ka dage da addu'a domin babu abun da yafi karfin ubangiji in yaso sai ka ga ka auri yarinyar da kakeso take sonka cikin aminci ba tare da takura ba."
Javed ya ce,"Hakane kam In sha Allah mussamman yarinyar tun farkon ganina da ita nake kwana nake tashi ina daurewa ne kawai."
Farouq ya yi dariya,"Ka bayyana a gareta kawai sannan ka mikawa ubangiji yakinin cewa indai ita alkairi ce a gareka zaka sameta."
Javed ya gyara zama,"Ko?"
Girgiza masa kai Farouq ya yi yana murmushi.

Javed ya ce,"Yess ban taba samun kwarin gwiwa irin ta yau ba,na gode sosai Oga ashe kai fa ka shahara ta ko wanni fanni daga yau za a fara wasan In sha Allah. "

Farouq ya ce,"Yawwa wai Janinah bata School ne na kullum tana gida."
Javed ya ce,"Eheen ai a ƙa'idar gidan Maza ne kadai ke da ikon yin karatun jami'a mace na gama sakandari aure ake yi mata kawai ita ma yanzu Arham kawai take jira ya kammala digirinsa sai ayi masu aure amman ta samu ta yi School dinnan ta samu training akan computer shi ma hakan sai da Abba Malik yasa baki da kyar Mai martaba ya amince shi ma na wata uku kacal ta yi acewarsa karatun ba wani amfani zai mata ba domin a gida zata zauna ta haihu ta kula da yaranta."

Farouq ya ce,"Huh Abubuwan da yawa ashe amman kuma shekararta nawa ne ma wai?"

Javed ya ce,"wannan shekarar zata cika 17."

"Ikon Allah baya karewa,amman ko da an bari ita ma ta dan kara karatun zai fi ko da bangaren computer dinne anan ko shekara ta yi."
Farouq ya fada.

Murmushi Javed ya yi ya ce,"Hmm ba ka san gidanmu bane har yanzu."

Alamar shigowar kira Farouq ya gani.
Yana dubawa ya ga Zoe ce murmushi ya sake a zahiri kafin ya dauki wayar.
"Our Own pilot yau an tuna dani ke nan."
Gajeran tsaki Zoe ta yi kafin ta ce,"Ba wani nan,wato kana Nigeria ba labari sai da mu ka yi magana da Khalil ya ke shedamun kana Nigeria ."
Farouq ya ce,"Eh wallahi a lokacin i try to reach you but bana samun ki seems you're off and ban san wani da zan iya tuntuɓa ba."
Zoe ta ce,"Oh Yeah I have been bedridden for two weeks So wayoyina duk suna kashe."

"Subhanallah yanzu ya jikin to? Fatan dai ya yi sauki."
Cewar Farouq.
Zoe ta ce,"Eh har ma na koma kan aiki."
Farouq ya ce,"Ma sha Allah yanzu yaushe zamu hadu? Zaki shigo ta Nigeria ne?"

Zoe ta ce,"E to bana ce ba amman zan duba jadawalina daman ina so ka dan seta mun wani abu a system dina amman dai za muyi magana zuwa dare ma I will chat u."

Farouq ya ce,"Okay Byee."
Javed na kallonsa tunda ya fara wayar har ya gama.
"Oga ko dai Madam ce wannan irin shauki tunda ka ga kiran fa kaketa murmushi har yanzu."

Farouq na dariya ya ce,"Nop wannan kawatace fa ai ni ban da Madam duk wacce ta nuna tana yina kawai binta na ke."
Javed ya ce,"Kowa darling kenan amman ni dai duk da haka wannan fa kila ta dabance."
Murmushi kawai Farouq ya yi ba tare da ya ce masa komai ba.
[14/05, 12:35 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON

ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-10

Suna tashi zasu tafi gida kamar yadda Farouq ya faɗa bai fasa ba sai da ya yi wa Hajiya Kaka siyayyar ta, har da shawarman kuwa sannan suka tafi.
Suna zuwa ya bata, sosai ta ji daɗi ta karɓa tare da saka masa albarka har ma da ɗan taka

rawar ta daga zaune.
Sun sha hira sosai don a part ɗin nata ma suka ci abinci, suna cikin cin abincin ta ke cewa.
"Bikin Sallar Gani fa ya zo, muna daf da tafiya Bida, don an fara shirye-shiryen tafiyar, ka ga idan na tafi zan yi kewar ka domin muna yin kusan sati a can. "

Da mamaki ya ce. "Mene  kuma bikin sallar gan
Hajiya Kaka ta ce. "Biki ne na Al'ada da ake shiryawa kowacce shekara acn gidan Baban Mai martaba da ke Bida, dukkanin mu za mu tafi can har sai an kammala shagalin kafin  mu dawo nan mu yi namu."
Farouq ya ce. "Ai ko nima zan je don ina son ganin al'adunku na gargajiya sosai abubuwan suna birge ni."
Haɗa ido Javed da Hajiya kaka suka yi domin sun tuna cewa Mai Martaba ya haramta masa kasancewa a cikin su a koma mene ne.
Gudun ka da maganar ta ja  Javed ya yi saurin katsewa tare da faɗin. "Oga dare fa ya yi maganarku kai da matar nan taka ba karewa za ta yi ba, kawai ka zo mu tafi Please. "

Dariya Hajiya Kaka ta yi ta ce. "Kai dai ka faɗi gaskiya kishi kake ya zo ya ƙwace maka mata, yo kai ma da  za ka riƙa shigowa da baƙar leda ai da mun sasanta ko da rabin igiya ɗaya ne in barma."
Dariya suka yi Farouq ya tashi yana. "Na jima da fahimtar sa ai, karki damu 'yan matana ni kaɗai ma na ishe ki."
Dariya suka yi duka kafin nan suka yi mata sallama suka fice.

Suna zuwa ɓangaren Javed suka baje a falo.
Farouq ya ce. "Yawwa gobe Sunday za mu fita yawo dai in ga gari ko? Mussamman river niger, ina so na gane wa idona, na ji an ce Mungo Park ne ya fara gano rafin ko?'

"A'a Gaskiya, asalin waɗanda suka fara gano rafin Richard Leander ce da kuma John Leander kwai dai..."
Kafin Javed ya ƙarasa magana wayarsa ta yi ƙara, yana dubawa ya ga kiran mai Martaba ne ke kiransa.
Tashi ya yi da sauri ya na. "Mai Martaba ne ya ke kira na, bari na je na ji."
Ya ƙarasa maganar yana amsa wayar tare da ficewa.

Numfasawa Farouq ya yi a zahiri ya ce. "Bikin Sallar Gani, tabbas duk yadda za a yi sai na kasance a wannan shagalin, zan iya samun wani bayanin na san."
Ya kai ƙarshen maganar yana ɗaga kai sama.
Kamar wanda aka tsikara ya miƙe tare da shigewa bedroom, waya ya fara yi wanda ba mai jiyo abin da ya ke fadi daga shi sai wa inda yake wayar da su, ya kwashe kusan awa guda yana wayar kafin ya katse ya koma kan System.
♡♡♡♡♡
Ƙarfe huɗu na yamma dukkanin su sun yi wanka sun shirya, sun yi kyau matuƙa.
Farouq sanye yake da ƙananun kaya kamar yadda ya saba saka wa, yayin da  Javed ya shirya

cikin manyan kaya domin ba sosai mai martaba ya ke son ganinsu sun yi shigar ƙananun kaya ba.
Kai tsaye River Niger suka nufa.
Javed ne ke driving din su suna tafe suna hira har suka isa.

Cike da mamaki Farouq da ya ga wasu manyan motoci na tafiya ya ce. "To su kuma waɗannan manyan motocin fa?"
Ya yi magana tare da kallon Javed.

"Suna dawowa daga gabas da kuma kudu ne, don nan din shi ya zama kamar  meeting point ɗin su, don ko lokacin da ka turo taimakon nan da na baka labari, ai a nan aka yi hatsarin.
 Da yake yawanci 'yan cirani suna ƙyashin biyan kuɗin mota, shi ne suke raɓuwa gefen manyan motocin da ke ɗauko mai (petrol) wanda ƙarshe duk kusan a nan suke  rasa rayukansu, babban abun takaicin kuma 'yan road safety ɗin maimakon su kula su riƙa hanawa, to da an basu ɗan cin hanci shikenan bakinsu ya yi shiru."

"Lallai suna wasa da rayukansu sosai, Allah ya kyauta! Gashi kuma hanyar na bukatar gyara sosai." Farooq ya faɗa cikin sassanyar muryar jimami.

Kallon sa Javed ya yi kafin ya ce.  "Sauƙin ta ma yanzu an dawo da tollgate,  ka san shi yana taimakawa sosai da kuɗin harajin da suke bayarwa, ana amfani da shi wajen gyaran titin da tabbatuwar hanya bisa tsari har ma da tattalin arziki."

Kasancewar babu nisa sosai  ba su jima ba suka isa.
Suna zuwa wajen kuwa Farouq ya ce. "Ya Subhanallahi!  Ai kogin ya fi kyau ma a zahiri fiye da yadda ake Misalta shi da kuma hotunansa da ake ɗauka."
Javed ya ce. "Haka ne kam to ka ga wannan shine kogin Nijar yana da matukar muhimmanci ga rayuwar dukkanin al'ummar Jihar Niger da Nigeria da ma tarihin yankin, a matsayin jigo. Kogin yana da tasiri sosai a cikin al'adunmu, yana bayar da gudummawa wajen ci gaban tattalin arziki ta fannin noman hatsi da kuma kamun kifaye. Wannan yana nuna cewa kogin ba kawai wani jigon ruwa ba ne, har ma yana da tasiri a cikin rayuwar yau da kullum na al'ummomin da ke zaune a gefensa.

Batun Mungo Park kuma yana daga cikin muhimman abubuwan da suka shafi binciken Kogin Nijar. Mungo Park ya kasance ɗaya daga cikin masu bincike da suka bayar da gudummawa wajen gano ingancin kogin da alfanunsa,  amman ba shi ne farkon wanda ya fara ganowa ba Richard Leander  da John Leander suna daga cikin waɗanda suka yi fice wajen bincike da nazarin kogin, suna bayar da muhimman bayanai game da tasirin kogin a cikin al'umma kuma sune wa inda suka fara gano kogin.

Dukansu, Richard da John Leander, an binne su a kusa da kogin don nuna girmamawa da ƙoƙarin su wajen tabbatar da ingancin kogin da kuma alfanunsa ga al'umma. Wannan yana

nuna yadda kogin ya zama wani muhimmin ɓangare na tarihin al'ummar Niger, tare da bayar da gudummawa ga al'adun gargajiya da zamantakewar al'umma.

Sarakuna da Al'ummomi baya ga  Richard da John Leander, akwai sarakuna da sauran al'ummomi da suka yi fice a cikin tarihin kogin. Waɗannan mutane sun taka rawa wajen tabbatar da cewa kogin yana ci gaba da zama jigon rayuwa da al'adu a yankin. Kogin Nijar yana da matukar tasiri a cikin al'ummomin da ke kewaye da shi, yana zama tushen rayuwa da ci gaban al'umma.

A taƙaice, Kogin Nijar yana da matukar muhimmanci ga al'ummar Jihar Niger , yana bayar da gudummawa ga al'adunmu da ci gaban tattalin arziki, tare da kasancewa jigo a cikin tarihinmu."

Farouq ya ce,"Maddalla! Amman ya nake ganin kamar electric power Station?" ya faɗa yana ƙarasawa ta wajen.

Dariya Javed ya yi kafin ya ce.
"Ah lallai kana wasa da mu ,ba ka san cewa mu ke da tushen wutar lantarki ba? Mu ke bawa Nigeria kaf wutar lantarki, mu ke da electricity Hydro Electric power station kenan yana samar da wurar lantarki da ya kai 760 megawatts (MW) wanda ya taimaka wajen samar da wutar a ƙasar nan tun cikin shekarun  da aka gina ta a 1960s sannan tana da matakai biyu na bada wuta da kuma tasiri wajen rage  katsewar wutar a Nigeria."

Farouq ya ce,"Ni na isa inyi wasa da ku ni fa son garin nan na ku kara shigata yake a kullum wallahi."
Suka ci gaba da magana suna tafiya.

Wasu mata suka gani sunata wanke ƙasa akan carpet.
Farouq ya ƙarasa gabansu da sauri yana,"Wannan fa me suke yi?"

Kafin Javed ya yi magana ɗaya daga cikin matan ne ta ɗaga kai ta kalli Farouq ta ce. "Zinare muke cirewa."  Ta karasa maganar tana nuna masa yadda suke amfani da chemical suna cirewa.
Bude baki Farouq ya yi yama rasa abun cewa sai.
"Wow!"
Muryarta ta katse masa mamakin nasa ya ji ta na faɗin. "Ka ga yadda a ke gasawa ma."
Ta faɗa tana sakawa a abun gashin kafin ta ce.  "A can sama kuma akwai inda ake narkawa in kana so za mu je in nuna maka."

Javed ya katse su da fadin,"Aa ba mu da ishasshen lokacin yammata,  ya kamata mu koma gida ai dai ka ga wannan ka kara yarda mu ɗin mu ne."

Farouq ya ce. "Gaskiya kam wannan lamuran naku ko ƙasashen waje albarka."

Godiya suka yiwa matan Farouq ya yi masu kyautar kudi kafin suka juya Javed ya ce. "Ai ko gonar Mai Martaba akwai wa inda suka zo suka ce sunga zinare amman ya hana su sam har cewa suka yi ko nawa ne zai saida zasu iya siya amma ya ƙi amincewa wai gonar gadonsu ce."

"Amman ko da Mai Martaba ya sa ana yi masa aikin ya buɗe ƙaramin kamfani karkashinsa da za a samu alfanu sosai, don wannan babbar dama ce domin haɓaka arziƙin gidan." Farouq ya faɗa

Javed ya ce.
"To ka san shi da kafiya da tsayawa a kan batunsa, 'yan uwansa ma basu isa su ce ba bare kuma mu, lamarin mai martaba sai dai kallo."

Da wannan hirar suka shiga mota, suna cikin tafiya motar ta samu matsala ta tsaya ga dare ya yi gashi gari ya haɗe da hadari kan kace miye ruwa  ya kece kamar da bakin ƙwarya.
Ganin ruwan bai da shirin tsayawa ga shi dare ya yi haka dukkaninsu suka fita a motar domin nemo bakanike,
sunyi neman duniya sun rasa saboda ruwa kowa ya tafi gida kuma dama dare ya yi gashi ba a wajen da mutane su ke wulgawa sosai suke ba.
Can tunanin Zeeyter ne yazowa Farouq ya kirata ya faɗa mata abun da ke faruwa.
Ta kirashi video call ita da Haiydar suka ga yanayin motar, da yake Allah ya taimaka Javed na dauke da box ɗin kayan gyara a motar, nan  Zeeyter ta saka yi  ɗauko tana faɗa masa abun da zai yi shi ma Haiydar na taimaka masu har suka samu suka gyara motar da ƙyar.
Sai wajen ƙarfe ɗayan dare kafin suka koma Gidan Sarkin Al'adu,  suna shiga Javed ya kalli agogon hannunsa zuciyarsa ta yi wani irin mummunan faduwa domin ya san a ƙa'idar gidan ba a wuce karfe goma a waje gashi yau shine har ƙarfe ɗaya, sosai jikinsa ya yi sanyi mussamman da ya hango wuta a falon Mai Martaba.
Yana gama Parking suka fitowa gabaɗaya a jiƙe ruwa na bin jikinsu.
Ɗaya daga cikin dogaran Mai Martaba ne ya ƙaraso garesu da sauri yana faɗin.
"Ranka Ya Dade Mai Martaba da Jama'ar gida suna jiranku a babban falo."
Kallon Farouq ya yi cikin dauriya da ƙarfin hali ya ce. "Oga kai ka tafi ɗaki sai na...
Kafin ya karasa dogarin ya katse shi da faɗin. "A'a ai ance dukkaninku ake son gani Ranka yaɗaɗe."
Nan fa zuciyar Javed ta fara bugawa cikin sauri.
Muryarsa na rawa ya amsa da ,"Okay."  Kallon  Farouq ya yi  yana ,"Mu je Oga."

Suna shiga suka ga Mai Martaba tsaye,Hajiya Kaka,Mammah,Kilishi,Abba Malik,Janinah da kowa.
Kafin Javed ya ankare sai jin saukar mari ya yi a kumatunsa.
[17/05, 5:28 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa

Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN KARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*

Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-11

Zai kara masa wani da sauri Abba Malik ya tare gaban Javed yana,"Ayi masa afwa Yaya."
Dakatar da shi ya yi da hannu alamun ya matsa ba ruwansa.
Matsawa gefe Abba Malik ya yi yana kallon ikon Allah.

Mai Martaba ya kalli Javed cike da tuhuwa ya fara jera masa tambayoyi,"Ba ka da hankali ne? na ce ba ka da hankali ne? ko kuwa ka samu taɓuwar hankalin da ya mantar da kai cewa kai ahalin wannan gidan  ne?"

Javed bai iya cewa komai kansa na ƙasa.
Cikin dagun Murya Mai Martaba ya ce,"Za ka bani amsa ko kuwa?"
Cike da firgici Javed ya durkusar da gwiwarsa ƙasa yana,"Ayi mini afwa Mai Martaba akasi aka samu motata ta lalace a hanya." Ya faɗa muryarsa na rawa.

Mai Martaba ya ce,"Amman ka fi kowa sanin doka da tsarin wannan masarautar ko? Daga Yan Uwana har Yayunka da na haifa babu wanda ya taba gigin karya mun doka sai kai? Kana jin ka isa kenan ko kuma zama da wancen ne ya janyo?"
Ya karasa maganar yana nuna Farouq dake tsaye yana bin kowa da kallo yana ganin ikon Allah.
Caraf Kilishi ta ce,"Yoo shi ne ma mana shi ne zai ja shi yawon ma kuma ni ina zarginma gidan rawa ya kai shi domin yanayin yaron nan sam ba na kirki bane kila ma ba wani dan kasar waje bane yafi kama da sadakayalla,kana ganinsa ka ga munafu....

Tsawar da Abba Malik ya yi mata ne yasa ta shirun dole.
Cikin ɓacin rai ya ce,"Wato ke dai babu alkairi a bakinki ko? Sam ke ba kya nufin kowa da alkairi ne sai sharri? Ki rabani da wannan mummunan dabi'ar taki Kilishi."

Kau da kai ta yi tana faɗin,"Ai daman kai baka son gaskiya ni kuma wallahi ko za a mutu sai na faɗi gaskiya ehee."
Shi dai Farouq yana ta binsu da ido.
Gyaran muryan da Mai Martaba ya yi ne yasa dukkaninsu yin shiru.
Jan numfashi ya yi, cikin isa da izza ya ce,"Bakonka na da zaɓi biyu, ko ya bi dokokin wannan masarautar ya zauna ko akasin hakan ya barta,sannan daga yau ba za ku kara fita daga kai sai shi ba za a hadaku da ɗaya cikin dogarai yana lura da motsinku in aka kamaku da aikata wani abun da ba daidai ba babu shakka kowannenku ya karbi hukuncin bulala ashirin sannan kuma in an kammala hukuncin bakonka tafiya zai yi ba zai kara zama ba ya tabbata dai kenan muddin

yana son zama sai ya bi tsari da dokokinmu."
Yana gama faɗa ya fice.
Tsaki Kilishi ta yi azahiri wanda ya bayyanar da ɓacin ranta ta fice,ita ma Janinah ta bi bayanta.

Sauran matan da mazan ma duk suka fice sai Hajiya Kaka,Abba Malik,Farouq da Javed.
Abba Malik ya kalli Farouq ya ce,"Malam Umar sai dai ana hakuri fa nan ba kamar can ba mussamman wannan masarautar ana riko da al'ada sosai tamkar addini. "
Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Hakan ma yana da kyau ai."
Hajiya Kaka ta ce,"Gashi duk kun jike,ku je kuyi wanka ku canja kaya ku samu ku kwanta in kuma ba za ku iya ba ko mu je in muku?"

Dukkaninsu basu san lokacin da dariya ta subuce musu ba da jin maganar Hajiya Kaka duk da cewa basa cikin yanayi mai daɗi.

Abba Malik ya ce,"Hajiya ke ina ke ina yiwa garadan nan wanka,mu je dai ki kwanta."
Ya karasa maganar yana riko hannunta.
Taɓe baki ta yi ta ce,"Yo miye a ciki dukkannsu mazajena ne ai in sun gagara sai in saɓesu tas ba don jikin tsufa ba ma har goyasu zan da majanyi."
Abba Malik ya ce,"Ah lallai wa innan Mazaje ana ji dasu."
Farouq ya ce,"Yanzu dai mun yafe ki je ki huta sai da safe ko yan matana."
Ya karasa maganar yana bata hannu suka tafa kafin suka fita suma suka koma bangarensu.
Bayan dukka sunyi wanka sunyi sallah gabadaya ko abincinma sun kasa ci mussamman Javed ya zauna ya yi shiru a falon.
Farouq ya zauna kusa da shi yana,"Ban san ta yadda zan fara baka hakuri ba domin dukkanin abun nan da ya faru nine sila,Don Allah ka yi hakuri gobe zan koma hotel in sha Allah ba zan so ace sanadina kana samun saɓani da family dinka ba."

Javed ya ce,"Ya Subhanallah  ka daina fadan cewa za ka tafi hotel,ba wani hotel din da zaka tafi kuma ni ba abun da ka zama sanadi a gareni sai alkairi ni kawai na gaji da wannan tsarin ne na gidan nan ba zan jure ci gaba da rayuwa cikinsa ba ace wai mu bamu da yancin kanmu kwata-kwata? Ba mu isa muyi rayuwar da muke so ba sai wacce aka tsara mana? Ba zai yiwu ba ina ji araina akwai abun da ake aikatawa da ba daidai ba cikin wannan masarautar."

Farouq ya ce,"Ni dai ka yi hakuri kuma ka maida komai ba komai ba indai da gaske baka so in koma hotel to ka ci gaba da bin umarnin Mai Martaba za ka ci ribar rayuwa."

Javed ya yi ajiyar zuciya ba tare da ya ce komai.
Tashi Farouq ya yi ya dauko masu Drink da snacks ya mikawa Javed kafin ya zauna yana,"Yawwa ni kam ya batun wancen Bikin Ganin ne? yaushe  ne? Ina son zuwa fa."

Javed ya yi guntun tsaki "wallahi ni na manta ma amman dai a cikin satin nan ne za a tafi ni fa lamuran gargajiyan nan ba sonsu nake ba a dole nake bi,kuma ni yanzu ban san ya za muyi ba mai martaba ya ce ka da ya kara ganinka akan abubuwan da suka shafi gidannan da ma

Al'ada."

Farouq ya numfasa,"Alright ba matsala karka damu dani."

Javed ya ce,"Amman kuma kana son zuwa ai."
Farouq ya yi murmushi,"Eheen ina so amman kuma son da nake zai iya ja maka matsala ni kuma bana so in kara saka cikin wata matsalar."

Javed ya ce,'Kasan yadda za ayi?"
Farouq ya girgiza kai,"Aa sai ka faɗa."

"Zan bi ayarin yan gida mu tafi kai kuma sai in hadaka da wani ko cikin abokaina ne ka ga ba wanda zaiyi tunanin zaka je sannan kuma sai ka yi kokarin yadda baza ka gamu da Mai Martaba ba, ko kilishi dama sauran yan gidan."

Farouq ya ce,"Ba matsala zan so ma inje ni kadai domin in kara ganin gari karka damu komai zai tafi daidai In sha Allah."
Da haka suka dan yi hira kafin Javed ya fara tafiya daki ya kwanta ya bar Farouq shi kadai. Waya suka dunga yi da Zoe yana tsokanarta tana tsokanarsa sunata dariya sai da ya kalli agogo ya ce,"Madam yanzu a Nigeria karfe uku ne,ina son inyi Tahajjud Prayer."

Zoe ta ce,"Ah Har cikin dare kuna Sallah kenan ban da guda biyar din da kuke yi?"

Farouq ya ce,"Nop Wannan Ita ba  farillah ba ce sunnah ce ma ana ba wajibi ba bace amman kuma tana cikin sallar da ake matukar so a cikin musulunci kuma tana da matukar muhimmanci domin yana ƙara kawo kusanci tsakanin bawa da ubangiji sannan ana yinta ne karshen rabi na dare lokacin aka dauka a matsayin mafi alheri don sallah da addua tare da tabbatuwar biyan bukatu domin a lokacin Ubangiji yana amsa bukatun bayinsa babu shamaki."

Zoe ta numfasa ta ce,"Da kyau kuma har guda nawa ake yi?"

"Ba adadi zaki iya yin raka'a biyi ma kiyi sallama ki roki ubangiji shikenan wannan raka'a biyun ta fi duniya da ma abun da ke cikinta inko kina so zaki iya yin takwas har fi ma." Farouq ya faɗa.

"Kenan dai ita wannan sallar in anyita ana samun biyan bukata ko?"

Farouq ya ce,"Yes In sha Allah mussamman kasa aranka zaka samu abun da kake nema din wajen ubangiji. "

Zoe ta ce,"Sai na ji ina son yi da ace ba matsala zan iya da yau na tayaka nima in roki Allah ya biya mun bukatuna kuma ma time dinmu ba daya ba zan iya?."
Farouq ya yi murmushi,"Mai zai hana? Ai kuma yanzun dare ne ba sai lokaci daya ba,yanzu zan

je da wayar toilet muyi alwala kiyi duk yadda na yi sai muzo mu yi sallar ma tare."
Hakan kuwa aka yi suka yi alwala yana mata bayani ta dauko gyaranta ta yi rolling ta dauki wani dankwali ta shimfida matsayin sallaya suka fara sallah tana kallon yadda Farouq yake ita ma tana yi har suka idar.
Rufe ido ta yi ta daga hannu sama tana addua ,"Allah ka bani komai da komai ka kara mun kyau,kudi,jin dadi,lafiya,hutu da komai da komai Allah jikina ya yi kyau sosaiii."
Da karfi take adduar idonta a rufe.
Dariya ce ta suɓucewa Farouq ya ce,"To Amin wato harda kyau bayan wanda kike da shi."
Alama ta masa da hannu a baki ,"Shiiiii." Ka yi shiru.

Ta ci gaba da cewa ,"Allah kasa in samu masu zuwa Nigeria in dauko Farouq in gudo da shi."
Shi dai kallonta yake kawai yanata dariya.
Sai da ta gama jero adduointa kafin ta ce,"Eheem kai ba kasan ba kyau mutum na addua ana magana ba zaka sani."
Ya yi dariya,"To ai na ga kin dage ne harda batun kyau."

Sigina ta masa ta ce,"Eheen naka wasa ne sai ka kasa ganeni ai innazo daukanka." ta karasa maganar tana hamma.

Farouq ya kara dariya kafin ya ce,"To Shikenan yanzu dai kije ki kwanta ni zan fara aiki."

"Alright Goodnight. "Ta fada.

Farouq ya ce,"Nighty Night byee."
Da haka suka katse kiran ya dukufa kan System kamar yadda ya saba.

Yana kunnawa ya ga alamun yana kokarin kawo masa hari system din ta nuna akwai matsala.
Cike da mamaki ya fara bi ya rasa gane wane ne ke son bincikar bayanansa duk da cewa yasan ba za a taɓa samu ba muddin in ba shi ya bada kofar hakan ba.
Abun da ya matukar bashi mamaki shine da ya duba location ya ga abun da ake son yi din a gidan ne.
A tunaninsa error ne ko kuma location dinsa system din ke basa amman duk dubawan da zai yi babu shakka mai kokarin bincikarsa na cikin gidan.

Dakin Javed ya je ya gansa yana barci cikin kwanciyar hankali har system dinsa ya kunna amman bai ga wani abu makamancin hakan ba.
Ji ya yi kansa ya fara ciwo domin abun ya daure masa kai matuka.
Ya dafa kansa yana zama gefen gadon tare da tafiya dogon nazari.

Misalin karfe Goma na safe Kilishi ce zaune da Janinah a falonta.
"Aunty Kilishi ni wallahi jiya na ji haushi sosai da Mai Martaba bai kori wancen gayen ba."

Tsaki Kilishi ta yi kafin ta ce,"Ke ko ni Janinah? Wallahi da abun na kwana araina ban san dalili ba amman kullum inna gansa kara tsanar yaron nake wallahi amman kar ki damu faɗan yanzu nawa ne ba naki ba,ni na san matakin da zan dauka sai ya yi danasanin zuwansa kasar nan inma da gasken zuwa ya yi bare kuma shigowarsa gidan nan."
Ta karasa maganar tana cije baki.

Janinah ta ce,"Aunty ki fadamun in tayaki mana."
Murmushi Kilishi ta yi kafin ta ce,"Kar ki damu zan fada miki bari in kammala shirina."

Farouq na office a digital craft kokarin bincikar mai bin diddigin sa yake tun jiya yanata fama karaf ya ji wayarsa na kara alamar shigowar sako.
Yana dauka......
[18/05, 2:54 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN KARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊

*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- Sleeping dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-12

Ya ga text message ne aka turo "Ko da ka shahara tarwatsa tsari da shirin wasu,ina jadadda maka cewa ba za ka taɓa kaucewa nawa ba,kila kana jin kanka cewa yanzu kana rayuwa ne a fili saɓanin cewa ni kallonka nake a cikin rami mai zurfi takurararre cike da duhu mara misaltuwa."

Murmushi Farouq ya yi ya gyaɗa kai kawai ya ajiye wayar yana ci gaba da duban system dinsa.

Shigowar Javed ne ya katse shi da fadin,"Oga Mun gama,lokacin ka ne yanzu."
Tashi ya yi yana ,"Okay to."

Tashi ya yi ya tafi lecture room din.

"Good morning class."

"Morning Sir."
Suka amsa

"OYaa On your systems Yau za mu yi bayani  ne akan White Hat Hacker,na san da cewa

dukkanin ku kun san wane ne White Hacker to amman ta ya yake gudanar da aikinsa na shiga na'ura? Me da me yake bukata?"
Ya karasa maganar yana zama gaban system dinsa kafin ya ci gaba
"Karku manta sai har an bashi izini kafin yake fara gudanar da aikinsa kuma abu na farko da yake yi shine Binciken tsaro wato
(security assessment) sai kuma gwajin shigarwa (penetration testing) a karkashinsa shi ne ake kirkirar kwayoyin yanar gizo da kirkirar hanyoyin kariya masu inganci da karko

Kayayyakin amfani da aikinsu wato Utilizing tools

Na farko akwai Nmap: Don nazarin hanyoyin sadarwa da gano na'urorin da ke haɗe (for network scanning and identifying connected devices)
Na biyu Metasploit: Don gunadar da hare-hare da kuma gwajin rauni (for executing attacks and testing)
Na uku WireShark: Don nazarin zirga-zirgar bayanai a cikin hanyar sadarwa (for analyzing data traffic within the network)

Sai kuma Access Control tsarin kariya ke nan
Suna amfani da tsarin kariya domin tabbatar da cewa suna kan tsarin da aka ba su izinin aiki akai.

Sannan Tantancewa da rahoto ma ana Evaluation and Reporting
Bayan an kammala gwaji ana tantance bayanai kafin a rubuta rahoto wanda ya kunshi raunin da aka gano da shawarwarin yadda za abi domin yin gyara.

Wannan kenan kafin kuma su shiga kan aikin inganta tsaron,yana da matukar mahimmanci abi wannan matakan domin in babu su ba za a taba samun abun da ake nema ba kenan kuma akwai bukatar ku fahimta da kyau."

"Yes Sir."
Suka furta.
Tun kafin ya bada izinin tambaya Meemah take ta daga hannu.
"Go on Memah." Farouq ya fada.
Tashi ta yi ta ce,"Sir yanzu kenan ko waya tace nasa security wanda ba mai karfi ba akwai wanda yana iya zuwa zai cire?"

Farouq ya ce,"Sosai ma,musamman ku da ke sa password ko pin mara karfi fada mun password dinki inji yanzu zan iya fada miki cikin minti nawa zan iya kwamushesa ba tare da kinsani ba ma ."

Ta ce,"Mima12 ne Sir."
Farouq ya ce,"A cikin 11 minutes zan iya cire password din wayarki ko kasa da hakan ma,shiyasa da an samu kuskure an sace wayoyinku cikin sauki ake kwasar bayananku, yanzu

tunda kin fadamun wannan canja wani ki bani in gwada cirewa."
Canjawa ta yi ta bashi wayar.
Cikin 8minute kuwa ya cire password din sunata mamaki.
Meemah ta ce,"To Sir a koya mana yadda ake cirewa kuma a koya mana yadda zamu sa security mai kyan da ba za a iya canjawa cikin sauki ba."

Farouq ya ce,"For now dai yanzu koya muku yadda zakuna duba karfin password kafin kusa ako ma miye naku amman yadda ake cirewa ba mu zo nan ba."
Suka amsa da ,"Okay Sir."

Farouq ya ce,"Yawwa dukkanin ku ku shiga Google a systems din ku ku yi searching Password Strength Meter. "
Cike da zakuwa dukka suka yi.
Farouq ya ce,"Kowa ya yi?"
Suka amsa
"Okay za ku ga an rubuta TYPE A PASSWORD ko kamar haka."
Ya nuna masu a system dinsa.
Ya ci gaba da fadin,"Yawwa nan zai na fada mana karfin password din da zamu rubuta da lokacin da za a iya dauka kafin a iya cirewa yanzu ni bara in gwada rubuta nawa so simple amman kuma very strong bari mu ga na rubuta [U@M@R_F@R@Q],kun ga dai yadda na rubuta ko me kuka sunsa?"
Karantawa suka yi duka
"Very Strong Password,Time to track your password 1million years. "
Suka karasa fada cike da mamaki suna bude baki.
Farouq ya ce,"To yanzu kowacce ta rubuta a system dinta muga."
Dukkaninsu suka rubuta hakan ya fito sunata jin dadi.

"To yanzu kunga anan zaku iya rubuta kowanni kalan password ku duba ingancinsa kafin kusa a wayarku ko a system dinku zai na indicating maku in mai kyau ne ko akasin hakan."

Da murnar su suka ce,"Thank you Sir."
Fita ya yi ya barsu sunata faman gwada password kala kala.

Farouq na komawa office ya samu Javed na waya Yayansa ya kira yana sheda masa cewa gobe zasu wuce bida domin jibi za a fara bikin gani.
Javed na gama wayar ya ce,"Yawwa ka ga daman yau za a tafi hutu ba mu da matsala dangane da makarantar nan domin jibi ne ma wai ashe za a fara bikin zamu koma gida da wuri domin inje in fara shiri."

Farouq ya ce,"Okay to shikenan Allah ya kai mu amman ni nidai ina so inji tarihin garin bida dinnan da aketa batun acen asalin sarki yake."
Javed ya ce,"Wannan in ka samu Hajiya Kaka ai labarin tarihi sai ka ture ta sha bamu amman yanzu innace zan fada ma na tabbatar da cewa ba zan baka in details kamar ita ba."

Farouq ya ce,"Ai ba na ma son naka ni da nake da Mata guda,yau muna komawa a part dinta zan tare gaskiya. "
Dariya Javed ya yi ya ce,"To mai mata."

Da haka suka kammala wuninsu na ranar har suka koma gida kamar yadda mai matarba ya umarta kuwa akwai mai binsu duk inda zasu je.

Bayan sun koma masarauta sun idar da sallar isha Kai tsaye bangaren Hajiya Kaka suka nufa tana zaune an wage kafafu da hannaye duk an rufesu da leda.
Farouq ya bude baki,"Ah Me zan gani?"
Hajiya Kaka ta ce,"Lalle mana ado ai na yi maka angon."
Zama ya yi daf da ita yana,"Ai kuwa dole in biya kudin wannan ado."

Hajiya kaka ta cuna karamin bakinta tana,"Yoo ba ma dole ba ai wajibi ne a gareki."
Farouq ya ce,"To ni yanzu ba ma wannan ba so nake abani tarihin kasar bidan nan tunda ni dai ba zan samu zuwa ba aiki zai mun yawa."

Hajiya Kaka ta gyara zama,"Tabbas kuwa ka zo gidan tarihi ka karkade kunnuwanka da kyau ka saurareni."

Hannu Farouq yasa a kunnuwansa yana karkadewa suna dariya.
Hajiya Kaka ta ce,"Yawwa Bida na ɗaya daga cikin birnin da suke sahun farko a jahar niger a Nigeria.
Domin ta kasance matsayin cibiyar kasuwanci  tun daga zamanin da kakanni da kakannin kakanni domin ta kasance hanya mai mahimmanci ga masu safarar kayayyaki daga arewa zuwa kudu.
Haka kuma birin yana da tarihi mai zurfi a fannin addini, tare da kasancewar shi a matsayin wurin taron al'ummar musulmi.

Bida an kafa ta a farkon ƙarni na 19 kuma ya zama sananne a lokacin Jihadin Fulani da Usman dan Fodio ya jagoranta. Birnin ya zama muhimmin cibiyar kasuwanci da ilimin Musulunci, wanda ya taimaka wajen yada addinin Musulunci a wannan yanki. Masarautar Nupe, wanda Bida ta kasance cikin ta, ta taka muhimmiyar rawa a cikin tsarin siyasa na tsakiyar Najeriya.

A cikin shekarun baya bida ta kasance gida ga masarautar Bida wacce ta kasance daya daga cikin manyan masarautu a Nigeria kuma masarautar ta yi fice wajen bunkasa al'adun gargajiya da kuma gudunar da harkokin zamantakewa a yankin.
Sannan tana da kyawawan wurare da suka shahara kamar su gidan sarauta da kuma wuraren tarihi da ke jawo hankalin masu yawon bude ido haka kuma birnin na da alaka da harkokin noma inda manoma ke samar da kayan amfanin gona da dama to wannan ita ce bida kuma kuma garin su Matar Abbanku Malik kenan domin yar sarki ce wato babban sarki kenan da su mokwa  karkashinsa na ma manta Jahar bida na bawa Al'adu muhimmici matuka

Bida tana da shahara wajen sana'o'in gargajiya, musamman a fannin tukwane da zane-zane. Hakanan birnin yana da shaharar bukukuwan al'adu na shekara-shekara, wanda ke nuna arzikin al'adun mutanen Nupe, ciki har da kiɗa, rawa, da tufafi na gargajiya kamar dai yadda yanzu muke shirin tafiya bikin Gani.

Hakazalika
A zamanin yau, Bida ta ci gaba da girma, tana zama muhimmin cibiyar gudanarwa da kasuwanci a Jihar Neja. Hakanan birnin yana da manyan makarantu, wanda ke taimakawa wajen bunkasa ilimi a wannan yanki kasan duk da mun tsufa amman ba ma gajiya da sauraren redio domin jin ya duniyar da lamuran cikinta suke tafiya."

Farouq ya numfasa ,"Ma sha Allah ai kuwa tarihi ya fita fes to amman yanzu ke nan ban da mokwa akwai wasu garuruwa da ke karkashin bida?"

Hajiya Kaka ta ce,"Kwarai kuwa akwai Mokwa nan ke nan inda muke sai
Katcha
Yawwa akwai  agaie  ma dukkaninmu muna karkashin masarautar Bida ne."

"Kenan yanzu duk yan garuruwan cen ma zasu tafi bida shagalin bikin Gani?"
Farouq ya fada.
Hajiya Kaka ta ce,"Kwarai ma kuwa ai nan ne tushenmu duk."

Farouq ya ce,"To shi kuma wannan Bikin Ganin fa mene ne ma anar yinsa? Kuma kwana nawa za ayi ana yi?"

Tashi Javed ya yi yana,"Oga in ka shigo ma hadu na lura wannan zantukan naku ba mai karewa ba ne."

Kafin Farouq  ya amsa caraf Hajiya Kaka ta ce,"Yo dole ka tashi mana kana nan da takunannen hanci kamar sabuwar kalwa yara basa son jin tarihi da al'adunsu sam sam bare ma ku koyi  riko da su sai shegen.... kafin ta karasa tusa ta suɓuce mata ga shegen wari ga kara kamar an fasa bomb.

Javed ya kalleta ya ce,"Oku (sannu) ganin yadda ta karkace kafin ta sambado tusar yasa bayan ya ce mata sannu ya fashe da dariya,Farouq ma dai ya gagara rike dariyar toshe hanci ya yi yana yi.
Tsaki Hajiya Kaka ta yi ta ce,"Cuta ce dai na fitar ba wani abu ba kuma kwai na ci dafaffe guda takwas dazu abuna ahto inma zaku bude hanci ku bude wannan iskar da na fitar ma ta albarkace zasu samu."

Da gudu Javed ya fice yana,"ni dai na yafe wa wannan albarka Oga akwasa da kyau."
Ya karasa yana dariya.

Hajiya Kaka ta ce,"Rabu da shi bara in ci gaba da fada ma yawwa Bikin Gani.....I
[20/05, 7:19 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor

- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-13

Bikin Gani na daya daga cikin manyan bukukuwan al'adu da ake gudanarwa a Bida. Wannan biki yana da matuqar muhimmanci ga mutanen Nupe da kuma al'ummar da ke zaune a Bida.
Ma'anar Bikin Gani kuwa
Bikin Gani yana nufin bikin da aka shirya don nuna al'adun gargajiya, kiɗa, rawa, da sauran abubuwan al'adu na musamman. Ana gudanar da wannan biki a kowanne shekara, kuma yana jan hankalin mutane daga sassa daban-daban na Najeriya da ma waje.

A lokacin bikin, ana gudanar da wasannin kwaikwayo, gasa tsakanin matasa, da kuma nune-nunen kayan tarihi. Hakanan ana jin dadin kiɗan gargajiya da rawar al'adu da suka shahara a cikin al'ummar Nupawa.

Sannan Bikin Gani yana ba da dama ga matasa da su yi koyi game da al'adun su da kuma yadda za su ci gaba da su a cikin zamani. Hakanan yana karfafa haɗin kai da zaman tare tsakanin al'umma.

Domin kuwa Bikin Gani a Bida yana zama wata hanya mai kyau ta bayyana kyawawan al'adun gargajiya da kuma taron al'umma, yana kara dankon zumunci da haɗin kai a tsakanin masu halartar biki."

Farouq ya numfasa,"Ma sha Allah abun birgewa kuma kwana nawa ake yi ana shagalin?"

Hajiya Kaka ta ce,"Kwana Uku ne amman mu wani lokacin har mako guda muna yi bida mu huta da ke muna da bangare guda namu da ake ware mana a cen gidan Mai Martaba Babba."

"Gwanin Sha'awa,Yanzu bara in barki ki kwanta in tafi dare ya yi."
Hamma Hajiya Kaka ta yi ta ce,"Aiko kamar ka san na fara jin barci,Bara in kira yarinyar nan ta zo a kunce lallen nan."

Sallama suka yi Farouq ya tafi Javed har ya dade da barci kai tsaye dakinsa Farouq ya wuce.

Gari na wayewa gida ya cika fal anata shige da ficen shirin tafiya Bida.
An jero motoci bisa tsari masu tsaro a gaba kafin motar mai martaba sannan ta sauran mutanen gida.
Farouq na cikin bangarensu ko fitowa bai yi ba tunda
Misalin karfe Ɗaya na rana suka dau hanya bayan sunyi sallah sunci abinci.
Da ke ba tazara sosai awa biyu da mintuna suka yi a hanya kafin suka shiga cikin garin Bida.
Kai tsayen Bangaren da aka tanadar masu suka wuce,suka wuta suka ci abinci sannan suka yi sallah.
Daga nan Mai Martaba Sarkin Al'adu ya tafi ganawa da Sarki Mai Martaba na garin Bida.

Cikin dare Farouq ya isa garin da ke da yamma ya bi motar haya,yana isa TASTE PALACE HOTEL ya sauka domin da ya tambayi Javed hotel mai kyau nan ya yi masa recommending kuma da ya duba google ma ya ga alamun ingancin hotel din hakan yasa ya wuce nan kai tsaye.

Sai da Javed ya tabbatar da cewa Farouq ya iso cikin koshin lafiya kafin hankalinsa ya kwanta ya yi da Farouq dinma akan zai je hotel din su gana ya ki fir gudun kar a samu matsala cewar Farouq haka Javed ya hakura dole ba don ya so ba.
Daren ranar kuwa Farouq bai yi barci ba gabadaya kwana ya yi yana bincike tare da wasu ayyukansa.
Misalin karfe goma na safe ya shirya cikin kananun kayansa ya sanya pacing cap sannan ya dauki wani bakin glass mai dan girma yasa.
Yanayin yadda ya yi shigar zai yi wahala mutum ya ganesa ba in ba wanda ya yi masa sani sosai ba.
Masarautu Bida ya nufa cikin sa'a kuwa yana taran wata taxi cike take da matasa suma can zasu hakan yasa shi jin dadin bin ayarin nasu.
Ya shiga shima tamkar sahun yan gari ya zauna cikin wa inda suka je tare,Javed ne ya masa test kan har yanzu bai gan shi ba.
Farouq ya maida masa da cewa ,"Ni ko na ganka cikin tawagar mai martaba ya karasa rubutawa ya na daga masa hannu.
Murmushi Javed ya yi yana girgiza kai,"Tabbas nima na ganka to Maddalla. "
Anyi wasan kwaikwayo na al'adu sannan kowanni gari sunzo sun kafa dandalin abun da suke saidawa cike da alfahari haka kuma an yi nune-nunen kayan tarihi na gargajiya sannan anci ansha da abincin gargajiya kala kala sai wanda mutum ya zaba kamar su cingini (sakwara),Ezo (wake) Kunu ,Akara (Alale),tuwo,Ɗankuwa,Kuli_kuli da dai sauransu.
Da ke ranar farko ne an gama shagalin da wuri kowa ya watse wanda gobe zasu gabatar da rawa da abubuwan sarauta na gargajiya.

Ba wanda ya lura da Farouq  har aka watse.
Ya karbi number ɗaya cikin wa inda suka zauna tare.

Rana ta biyu

Ranace ta mussamman domin ba iya mutane ke kasancewa wajen ba harda aljanu da sukan iya yin shiga a siffar mutane,cika ake na mussamman abubuwa da yawa na wakana ciki harda tsafe-tsafe da bori.

Wajen taro ya dau harama sarakai kowanne na rufa tare da tawagarsa yan bori ne suka fara anata fama.
Sarkin Raki wanda Aljani Sarki Fahad ne  akansa kamar an tsikaresa ya juya inda su Farouq suke, suna haɗa ido ,Farouq ya ji zuciyarsa ta fara bugun tara-tara da sauri ya kawar da kai yana sunkuyar da kai,bai san dalili ba amman babu shakka ya ji nauyin ci gaba da Kallon Sarkin Raki.
Kafin ya ankare ji ya yi an riko hannunasa yana daga kai ya ga sakice ta rike hannunsa,jan sa zuwa filin borin ta yi ta tsayar da shi rawani ta dauko ta fara naɗamasa tana yi sauran suka zagaye shi suna rawa,nan fa fada ta rikice kowa na son ganin wane ne wannan domin dole zai kasance na musamman ne,abune da bai taɓa faruwa ba a tarihin Bikin da ma masarautar.

Tana gama naɗa mashi ta fara yi masa Kirari ita da Sarkin Raki da sauran kujerar sarauta wacce take cikin na Sarkin Bida ta zaunar da shi daf da Babban Sarkin suna ci gaba da yi masa Kirari.

Ana zaunar da shi Mai Martaba Sarkin Al'adun mokwa idonshi idon Farouq   bai san lokacin da ya tashi tsaye ba gabansa na wani irin mummunan faduwa.

Sai ji yake zufa na keto masa ta ko ina,Shi ko Farouq kara zagayeshi aka yi ana yi masa wasu lamura,wani irin zobe Saki ta dauko ta dauko a jakarta mai kyalkyali zata sanya masa zoben kenan tana fara zurawa a hannunsa gari ya hade nan take akayi wata tsawa cikin sa'i guda wani irin ruwa ya barke.

Sarkin Bida ya ce,"Tabbas akwai babban lamari tare da wancen bawan Allahn domin ba lokacin damuna muke ba,kuma ba kowa yake iya samun wannan zoben ba bare har a sanya masa kai tsaye daga masarautar Sarki Fahad zoben ke fitowa."

Wani irin zazzaɓi ne ya rufe Farouq take idanunsa suka kada suka yi jajur cikin karfin hali ya rufesu ruf.

Mai Martaba Sarkin Al'adu ne ya tashi zai karasa gareshi cikin sauri Saki ta......
[25/05, 3:29 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN KARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*

You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-14

Ta dakatar da shi tana fadin,"Hattara dai."
Ba yadda ya iya ya koma ya zauna yana wani irin muzurai,babban abun da ya fi damunshi shi ne ya rasa gane wane ne Farouq kuma da wacce manufa yazo,duk kokarinsa ya gaza fahimta shi dai tun ganinsa na farko jikinsa ya bashi cewa akwai wani abu,to mene ne wannan abun?
"Sirrin da na binne?" Ya furta a zuciyarsa.
Da sauri ya kawar da kai yana girgiza hannunsa da ke kan cinyarsa azahiri ya furta,"Aa bai isa ba,ba zai yiwu ba,na rufe kowacce kofa,ba mai iya budewa."
Bai san cewa duk furucin da yake azahiri bane sai da ɗaya cikin fadawanshi ya yi magana,"Ranka Ya dade lafiya?"
Tukunna ya dawo hayyacinsa yana wani irin numfashi da haki,"Lafiya,lafiya ba komai,ba komai.
"
Ya karasa maganar yana ajiyar zuciya.
Yanayinsa duk ya firgice.
A cikin ransa ya ci gaba da saƙawa,"Sai dai wani lamarin ba dai sirrin da na binne ba jinin mu ma basu isa ba bare wani bare,ka kwantar da hankalinka ka da a fahimci wani abu. "
Da hakan ya yi kokarin maida hankalinsa waje guda a zahiri wanda kuwa a badini sai saƙe-saƙe yake duk da cewa zuciyarsa na ƙara jaddada masa cewa abun da yake tunani ba zai taɓa faruwa ba domin ya riga da ya rufe dukkanin wata ko ƙofa ko alama.

Farouq kuwa idanunsa kankamewa suka yi a rufe,cikin sauri Sagi ta je tasa wani ƙoƙo daidai inda ruwan saman ke zuba ta taran masa.
Tana zuwa ta buɗe bakinsa ta fara zuba masa ruwan yana sha sannan ta shafa masa a fuska.
Take ya nemi zazzaɓin da yake ji ya rasa idannunsa kuwa fari kal suka dawo da da yadda suke ma a baya saɓanin canja kalar da suka yi cikin ƙaramin lokaci.
Murmushi Sagi ta yi ta kallesa ta ce,"Sannu da kokari ko,Babu shakka kai hasken fitila ne da kan iya haskaka al'umma ko da kuwa kana cikin duhu,bare ma duhu bai isa ya kara bin hanyar da kake ba ko tunanin kai maka farmaki,ka fi karfinsu ba za su taɓa iya ja da kai ba in ko suka yi gigin hakan daidai yake da kokarin salwantar da rayuwarsu da tushensu."
Gabadaya jawaban da take ya sanya Farouq shi ga cikin ruɗani da rashin fahimta hasali ma kansa fara juya masa ya yi yana yi masa wani irin ciwo wanda bai taɓa riskarsa ba.

Karuwa ruwan ya yi cike da iska da wasu manyan kankara dake sauka iska na kaɗa bishiyoyi.
Babu alamun tsayuwa ga ruwan hakan ya sanya aka tashi ga taron hakan nan.

Javed ne ya je ya rike hannun Farouq suka wuce bangaren da suka sauka.

Suna shiga Farouq da ya samu gado sai barci.
Cike da tambayoyi Fal Javed ya zauna kusa da Farouq zuciyarsa na saƙa masa.

Zaune su Kaka suke duk an taru ana cin abinci,
Arham ya shigo yana,"Ikon Allah yau dai an kafa babban tarihi a bikin Gani kowa na ta mamaki ga ruwa sai karuwa yake,lallai Bakoncen na da abun mamaki."

Kilishi ta ce,"Wato yaron cen tsabar na ci sai da ya biyo mu wajen taron bikin nan,kuma ma fa ni har yanzu ban yarda da shi ba wallahi ko kadan kara jin tsanarsa nake araina,ga shi wai Saki sanya masa rawanin sarauta? Irin rawanin da ta sanya masa fa ko mai martaba ba a taɓa sawa shi ba."

Hajiya kaka ce ta ce,"Ke Khalisa ki raba kanki ba tun yau ba ina ji a jikina cewa wannan yaron wani ne,ba gama garin irin mutanen da kike zato bane akwai wani abu na mussamman a tattare da shi."

Janinah ta ce,"Ko ma shi wane ne dai ai ba ya fada mana sarauta ba mu da aka haifemu ciki."

Kilishi ta ce,"Sosai fa ni ba zan taba yarda da cewa shi  jinin sarauta bane ma yanzu haka tsafinsa ya yi kawai daman yan kasar wajen nan suma ance ba baya ba wajen tsafi musamman su turawan nan."

Abba Malik ne ya yi gyaran murya kafin suka yi shiru
Su Mammah,Aunty Heedaya,Yah Jamal da Junaid tare da matansu duk suna gun ana cin abinci ba masu jawabi da Kilishi da Janinah.

Meeting na gaggawa Sarkin Bida ya kira suka shiga kan lamarin Farouq.

Sarki ya ce,"Shin wane ne shi wannan din? Sannan a tawagar wa yake?"

Mai Martaba Sarkin Al'adu ya ce,"Ranka Ya dade, Gidana ya sauka a mokwa,Abokine ga Ɗan wajena Javed sun wani program ne na koyarda dalibai marasa karfi da galihu kimiya a kyauta."

Mai Martaba ya numfasa ya ce,"Ma sha Allah ta kwana gidan sauki ai,hakan ya yi amman a kira mun shi yaron naka ina so in masa wasu tambayoyi."

Sanyawa aka yi aka kira Javed aka masa tambayoyi akan Farouq duk ya sanar da su komai kafin aka bashi izini ya fita.

Hakimin Mokwa mai wakiltar Sarki ya ce,"Lallai Ranka ya dade akwai lamari babba tattare da wannan yaron bisa alamu kuma yana tare da manya domin kafin mu iso nan na yi kokarin

bincikar lamarinsa amman sam ba dama na gagara gano komai illa abu ɗaya da nake da yaƙinin cewa zuwansa alkairi ne garemu a garin mokwa da ma jahar niger gabadaya ɗayan bangaren kuma bana ce komai ba, amman babu shakka alkairi ne a tattare da shi."

Mai Martaba ya ce,"Tabbas nima na lura da hakan kuma na ji dadin hakan akwai iko da kudirar ubangiji da yake tafe da bayyanarwa,sannan ga dukkan alamu shi kan shi bai san shi waye ba don haka ina fatan kafin ya bar kasar nan ubangiji yasa mu amfanesa fiye da zatonmu sannan ina bada umarnin cewa duk wani abu da yake da bukata abarshi ya aiwatar muddin bai saɓawa tsari da dokokinmu ba,anyi biki wanda ba a taɓa yin irinsa ba kuma da kyar in akwai yiwuwar samun ci gaba na gobe a yau komai za a karƙesa domin kuwa ruwan nan shine komai kuma yana dauke da manufofi masu yawa."

Shi dai Sarkin Al'adun Mokwa yana jinsu amman aransa ji yake kamar ya fitar da Farouq ta karfi a kasar ma gabadaya,tsantsar tsanar yaron yake ji har cikin rainsa.

Da haka suka tashi a zaman ana jinjina kasancewar Farouq bisa ga abubuwan al'ajabi da ya faru.

Har cikin dare ruwa bai dauke ba kuma Farouq bai farka ba sannan Mai Martaba Sarkin Al'adu bai iya barci ba,zagaye daki yake yana tafiya yana tunani karshe ya dauko wata kwarya yana karanto wasu abubuwa yana juya hannunsa.
Wani abu ne ya fara hadewa yana yin mulmule,dariyar mugunta ya fara yana kara hadewa,can kuma abun ya tarwatse.
Take ya firgice ya tashi tsaye yana wasu irin sambatu ,"Ya za ku mun haka? Ku barni inyi aikina ku barniiiiiii bana son dakatarwa bana so na ce bana sooooo."
Ya karasa yana ajiyewa tare da kara daura hannunsa yana ci gaba da juyawa,kara fara mulmulewa ya yi yana daf da hadewa ya kara tarwatsewa.
Dafe kansa ya yi yana sakin wani dogon tsaki.
"Wannan ba zai yi ba,babu shakka akwai wata kuma dole sai ya yiwu ba makawa."
Ya karasa yana kyalkyale dariya.
Hannunsa yasa ya bude yana tsaye wani irin haske ya fara fitowa.

Janyo hasken ya fara yi da hannunsa ya yazo tafi hannunsa kafin ya zuba shi cikin kwaryar da ke gabansa.
Yana sawa hasken ya juye ya dawo wani irin abu shi ba mutum ba shi ba dabba ba,a tsaye yake tamkar mutum amman da ƙahon doki da kuma kafar kufoto.
Dariya suka fara daga shi har mutum da ke ciki.
Cikin wata irin murya ya ce,"Kai har akwai wani abu zai razana ka? Hahhhhhhhh kar ka bani kunya kar kace mun ba za ka iya ba,domin ba wanda ya isa ya ja da kai,sai dai wani bangare amman ba dai bangarenmu ba sau dai mu razanar ba dai a razanar da mu ba, kuma sai dai mu

mu aiwatar yanzu haka ma na yi ture hahhhhhh."
Biye masa da dariyar Mai Martaba ya yi suna ta yi ba kakkautawa tamkar zararro.

Karfe uku daidai kamar an tsikare Farouq ya miki tsilif
[25/05, 3:29 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets

- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-15

Ji ya yi kansa yana wani irin sarawa tamkar ana zare masa wani abu,cikin kankanin lokaci kuma ɗakin ya kaure da wani hamshakin baƙin hayaki.
Rike kan nasa ya yi sosai don ji ya yi tamkar kan na kokarin ficewa daga gangar jikinsa,cike da karfin hali ya fara karanto adduar neman tsari da kariya "Allahumma inni a'udhu bika min zawāli ni'matika, wa tahawwuli 'āfiyatika, wa fuja'ati niqmatika, wa jamī'i saḫaṭika."

Yana cikin karantawa daidai lokacin da Maah ta idar da sallar walha karfe goma 10am na safe kenan a cen malaysia.

Zama ta yi akan sallayarta tana yi masa addua ,"Allahumma inni as'aluka liwaladiyya khayra hadhihi d-dunya wa khayra al-akhirah. Allahumma ihfazhu bi 'aynika allati la tanam, waj'alhu min man tuhibbu wa tardha, wa wafqhu fī 'ilmihi wa 'amalihi, waj'alhu min aṣ-ṣāliḥīn al-mufliḥīn, wa qihish-sharra kullahu, dhāhirahu wa bāṭinahu, wa ij'alhu min man yanshuru l-khayr.
(Ya Allah, ina roƙonka alheri na duniya da alheri na lahira ga ɗana.
Ka tsare shi da idonka wanda baya bacci.
Ka sanya shi cikin waɗanda Kake so kuma Kake yarda da su.
Ka ba shi nasara cikin ilimi da aikatawa.
Ka sanya shi cikin masu gaskiya da masu rabauta.
Ka kare shi daga kowanne irin sharri, na fili da na ɓoye.
Ka sanya shi cikin waɗanda ke yada alheri)."

A hankali ya fara jin azabar na raguwa sannan hayaƙin da ya sarƙafeshi na washewa.
Ajiyar zuciya ya yi a zahiri yana faɗin,"Alhamdulillah."

Ya karasa faɗin ya tashi,Toilet ya nufa ya yi ya dauro alwala ya zo ya fara nafila,yana idarwa ya yi karatun Qur'ani sannan ya kara jero adduoi a kan sallayar wani irin barci mai dauke da ni'ima ya kwashe shi nan take a wajen.

Maah kuwa tunda ta zauna ta fara karanto masu adduoi sai da ta kwashe awa guda kafin ta tashi.

Farouq kuwa sai sallar asuba ya farka,yana idar da sallar Maah ya fara kira.
"Fatan dai kana lafiya,na ji muryarka a sanyaye ko dai ka samu mahaifin naka ne,in dai da wata matsala ka dawo gida ka ji,ni ina sonka,ban gaji da ganinka ba,ina son ka ci gaba da rayuwa,na san cewa wa innan mutanen mugayene basa da imani sam a zuciyarsu,suna da son kan su fiye da komai kuma.....

Katseta Farouq ya yi,"Maaah ina lafiya fa,kawai kewarki na yi na ji ina son jin muryarki kuma mu nan yanzu muka idar da sallar asuba."

Maah ta ce,"Ai sai ka ce mun shagwaɓarka ce ta motsa,indai kana cikin koshin lafiya ai shikenan Alhamdulillahi. "

Murmushi Farouq ya yi,"Umm indai adduarki na tare dani ai na san da cewa ba wani abu da zai taɓa samuna sai dai in har yana cikin kaddarata kuma kasancewarsa cikin kaddarar tawa ma adduarki zata iya sanyawa ya zo mun da sauki."

"Sosai kam Yaron kirki shiyasa kai ma nake maka tuni a kullum kan cewa kar kana wasa da azkar domin wasa da azkar tamkar wasa da rayuwane."

Farouq ya yi dariya ,"Kin ga ko yaronki ba ya yi wasa da rayuwarsa ba."

"Ma sha Allah To Allah ya yi albarka ka ga yanzu bara inje in duba abin da zanci na lunch yunwa nake ji."

Farouq ya taɓe baki,"Uhum to ba ki ce kina sona."

"Rigima kai kasan ba wanda nake so a duniya fiye da kai ai,Ina Sonka ina kaunarka kuma ina kewarka,Ubangiji ya kara tsaremun kai a duk inda zaka kasance."

Cike da fara'a Farouq ya amsa,"Amin Maahnah Byebyee nima ina sonki."
Katse wayar suka yi duka suna dariya.

Ruwan sama fa a Bida bai da shirin daukewa har wannan lokacin hakan yasa ma yawanci a masaukinsu sukai sallah sai daidaikunsu ne suka fita da lema zuwa masallacin.

Javed na zaune yana kallon Farouq har suka gama waya da Maah.

Ya ce,"Oga nikam kun burgeni kamar ba da mamanka ka ke waya ba,ji yadda kuke tsokanar juna kuna dariya? Kodayake daman ku yan kasashen waje kuna da wannan wayewar."

Farouq ya ce,"Mahna ai ni ita ce Aboki kuma Ƙawata ta farko a rayuwa ko acen ma wasu gani suke ni ƙaninta ne ba ɗanta ba ganin yadda muka shaƙu ta kan cemun in bata jani a jiki ba wa zata ja? Ni kadai ne gareta kuma ta hakane kawai zata iya zame mun garkuwa yadda ba zan taɓa shakkar fada mata damuwata ba."

Javed ya numfasa,"Hmm mu kam dai ai saidai gaisuwane kawai tsakaninmu da Mammah wai a hakanma mu tana iya dan kulamu ni da Janinah sabanin Jamal da Junaid da suke manya bare akai batun kuma Mai Martaba shi kam ai ba sai anyi magana. "

Murmushi Farouq ya yi ya tashi yana daga labule,"Wai har yanzu ruwan nan bai dauke ba?"

Javed ya bi bayansa,"Gashi kuwa kana gani,yauwa ni ka tuna mun ma,ruwan nan fa akwai alamun cewa ta dalilinka ya sauko,shin kana da wata sarauta ne a bangaren dangin mahaifinka ko mahaifiyarka?"

Farouq ya ce,"Ubangiji dai ya saukar da ni'imarsa, batun sarauta kuma Mahaifiyata ta taɓa fadamun cewa mahaifina yana da sarauta sannan kuma ita ma mahaifinta na da sarauta amman ni ba wani abu da na sani dangane da sarauta tunda ban taso ciki ba."

Javed ya kallesa cike da mamaki,"Ba ka taso ciki ba kamar ya?"

Murmushi Farouq  ya yi,"Ba zaka gane komai ba a yanzu amman in lokaci ya yi zaka sani."

Shiru Javed ya yi ba don ya so hakan ba sai don ya lura cewa Farouq baya son zancen.

"Bara inje in karbo mana abun karyawa don na fara jin yunwa wallahi. " Javed ya fada.

Farouq ya ce,"Okay Food Master ka tuna mun da Abokina mijin kawata Haiydar.

Dariya Javed ya yi ya fita yana,"Ai abinci abin so ne."

Dukkaninsu a ɗaki suka wuni ranar Farouq ya riga ya bar system dinsa a hotel ba damar aiki haka ya fita suka koma bangaren su Hajiya Kaka suka dunga hira.

Suna haɗa ido da kilishi ko Janinah sai dai su galla masa harara,shi kuwa da murmushi yake binsu wanda hakan ke matukar baƙanta masu rai.
Yanata dannawa Hajiya Kaka kafa tana jin dadi  tana bashi labarai.
"Rabon da akwana a wuni ana ruwa irin wannan tun zamanin da muke yan mata ban mantawa kamar ranar da aka naɗa mai martaba Kakanku ne sarautar Sarkin Al'adu wato sai da aka

kwana biyu cur ana tsala wannan ruwa kuma shi ma a irin wannan lokacin fa da ba damuna ba to sai kuma yanzu kusan shekara hamsin rata Allah shi kadai ya barwa kansa sani Kakata lokacin ta fadamun cewa irin hakan na faruwane kawai yayinda wani abun al'ajabi ke daf da shirin faruwa."

Cike da zolaya Farouq ya ce,"To kika sani ma ko abun al'ajabin na aurena da ke ne."

Dariya Hajiya Kaka ta yi ta ce,"Kuma fa hakanne."
Farouq zai yi magana kenan suka ji gyaran murya.
Mai Martaba Sarkin Al'adun mokwa ne......
[25/05, 3:29 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas

- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-16

Suna haɗa ido da Farouq ya yi saurin kawarwa shi kuwa Farouq ƙara kura masa idanun ya yi yana kallonsa shi ksnshi ba tare da ya san dalilin haka ba.
Shi ko Mai Martaba sam yaƙi bari su haɗa ido.
Gaishesa Farouq ya yi.
Kansa na gefe ya amsa yana neman waje ya zauna, bayan sauran sun gama gaidashi ya gaida Hajiya Kaka ya ce ,"Ina ganin ku kasance cikin shiri zamu koma gida domin an kammala wannan bikin da saukar ruwan nan,in Allah yasa ya dauke zuwa gobe za mu wuce mokwa da sassafe."

Hajiya kaka ta ce,"Ni ko ina sai munyi mako guda, ka san fa ina son zaman bida sosai."

Cikin tsawaita magana Mai Martaba ya ce,"A wannan yanayin ba zamu iya zama ba,ina da muhimman abubuwan da ya kamata in gudunar a gida."

Yana gama maganar ya tashi ya fice ba tare da sauraron kowa ba.

Dare ya yi an kawo masu abinci sai da suka ci kafin Javed da Farouq suka koma Dakinsu.

Farouq ya ce,"Ji nake a takure fa,ina bukatar System dita gaskiya i have alot of work to cover,anya zan iya hak'uri daren yau kuwa? Gaskiya zan fita."

Javed ya ce,"Oga da dai ka yi hakuri wannan ruwan ka ga har yanzu da dan saura tunda ya fara raguwa da ka bari zuwa safiya kila ya dauke duka sai muje ka dauko kafin mu wuce mokwa."

Farouq ya ce,"Ai inna tafi acen zan zauna ka ga daman ba tare zamu tafi ba inna kammala abun da zanyi zanzo daga baya nima. "

Javed ya ce,"Ina? Ai umarni daga sama gun Mai Martaba babba ya ce tare zamu koma domin an sanar da shi cewa kai bakon mune."

Farouq ya kalleshi,"Koma yane dai ni ina bukatar System dina a daren nan akwai bayanan da ya kamata in shigar."

"Alright yanzu mu je hotel din in rakaka ka dauko sai mu dawo tare barain samo mana rigar ruwa incase."

Hakan ne ya kasance suka tafi tare Farouq ya dauko System dinsa da sauran kayan kafin su ka koma cikin masarautar Bida.
Suna komawa kuwa ajiyar numfasa Farouq ya yi yana cire rigar ladan ruwan da suka sa.

"Ma sha Allah jin System dinnan nake tamkar wani bangare na rayuwata,kodayake kundin rayuwar tawa ma dukka ai yana ciki."

Dariya Javed ya yi,"Lallai kam ai na ga alamu kai computer ka sai Allah. "

Zama ya yi ya bude ya shiga fara dube-dube da aikinsa,kari gani ya yi lallai an kara kokarin kaiwa na'urar tasa hari,Security Alert ya bayyana kan cewa System din na kokarin fuskar hacking abun da ya kara bashi mamaki shi ne da ya duba location din ya kara nuna masa nan masarautar ta bida kamar yadda ya nuna masa masarautar mokwa lokacin da suke cen.
"Ke nan koma wane ne yana tare dani anan ma,to wane ne ya ke bibiyata haka? Me yake son sani? Alamu ya nuna akwai wanda ya san shirina ke nan? Lallai akwai bukatar na yi taka tsantsan domin gano ainihin abun da nake son ganowa kafin in kai ga matakin karshe ga dukkan alamu akwai mai son kawo mini tsaiko,to amman ai bana jin cewa akwai wanda ya fahimci inda na dosa."
Ya karasa faɗa aransa ya yin da ya tashi tsaye yana kaiwa da kawowa,a lokacin shi kam Javed ya jima da lulawa duniyar barci.

Farouq ya numfasa kafin ya ce,"Whatever na san ba za a taba iya samun abun da ake nema ba,amman babbar matsalata shi ne insa wake yin wannan kokarin sannan kuma mene ne dalilin hakan? Ko ma ta yane dai dole hakan ya shiga cikin tsarina kuma dole in binciko."
Ya karasa maganar yana daukan System din.
Sabon file ya bude ya shigar da yanayin yadda ake kokarin kawo masa harin kafin ya ci gaba

da aikinsa.

Bayan sun idar da sallar asuba Farouq ya ke cewa Javed,"Ka ga ruwan kuwa ya dauke gabadaya kamar ba ayi ba."

Murmushi Javed ya yi,"Ai kuwa kamar yadda yazo lokaci guda haka ya dauke yanzu ma."

Farouq ya ce,"ai kuwa har karfe hudu ma fa anayi amman ana kiran sallar asuba ya dauke nan take ikon Allah ke nan ba ya karewa."
Yana karasa maganar ya ji alamar shigowar saƙo wayarsa.
Yana dubawa kuwa ya ga Gmail ne sako daga SiftaCore Technologies.
Ta shi ya yi cikin murna yana fadin ,"Alhamdulillah,Alhamdulillah,Alhamdulillah. "
Cike da zaƙuwa Javed ya ce,"Oga ya dai wannan murna har ina?"

Nuna masa sakon Approval din ya yi,cikin rashin fahimta Javed ya ce,"Ban gane komai ba fa Oga na ga dai kamar za a bada kyautar Kwamfutoci. "

Farouq ya girgiza kai cikin jin dadi ya ce,"Eheen zauna yanzu zan fahimtar da kai,daman ban sanar da kai bane saboda ban tabbatar da samuwar hakan ba shiyasa na yi shiru amman yanzu komai ya tafi daidai."

Zama suka yi duka a kujerar da ke gefen gado.
Farouq ya ce,"SiftaCore Technologies wani kamfani ne mallakin wani Dan Nigeria mai suna Rasheed kwararren mai ƙyera na'ura ne wanda ya yi rayuwa a kasar South Korea kafin daga bisani ya dawo nigeria nan Abuja ya kafa kamfanin SiftaCore Technologies suna kirkirar Kwamfutocin AI-ready
Na'urorin super-computing don manyan cibiyoyi tare da
SiftaBox – kwamfutar tafi-da-gidanka mai amfani da sabuwar hanyar sarrafa bayanai.
da kuma kananun kwamfutoci domin ɗaliban fasaha.
Burin kamfanin shi ne Inganta rayuwa ta hanyar fasaha mai fahimta.
Sannan kuma a duk shekara suna kokarin bada tallafin kwamfutoci ga kananun kungiyoyi ko makarantu domin ingata karatu mussamman na yaran da iyayensu basu karfi,marayu ko marasa galihu.

Ina cikn gabar bincikena na ci karo da su sai na tuna cewa fa mun yi maganar inda hali muna son saiwa kowacce daliba kwamfuta kafin kammala samun wannan horon shiyasa kawai na shirya na tsara letter na tura masu karkashin DigitalCraft da dukkanin kudirorinmu to cikin ikon Allah sai gashi muna cikin sahun wa inda za abawa wannan tallafi."
Tsabar farinciki Javed bai san lokacin da ya rungume Farouq ba yana fadin,

"Ban san ma me zan ce maka ba,ban san taya zan nuna ma jin dadi da farincikina ka gamsu ba,tun da na sanka babu abun da ke fitowa daga gareka sai alkairi da son ci gabana,Na gode Oga,Na gode Allah ya saka da alheri ubangiji ya biya maka dukkanin bukatunka,ina ma ace

akwai wani abu da zaka nema a gareni da na ji dadi na yi maka shi cikin jin dadi duk da cewa na san ban da abun da zan iya ma fiye da wanda kake mun."

Murmushi Farouq ya yi,"Yiwa kaine ai duk wanda ya zam silar ingata rayuwar wa inda basu da bangon jingina gini yake yiwa kansa a lahira,ladan dani da kai duka zamu samu,babban abun da kuwa zaka mun ka biyani ai ka jima da yimun tunda ka yarda dani kuma ka aminta dani."

Kara rungumeshi Javed ya yi yana,"Na gode,na gode sosai."
Shi ma Farouq ya rungumesa.
Sunata murna da farinciki kallon agogo Javed yyi ya ga 7:am
Da sauri ya mike yana "Oga nasan ba za mu wuce 8 a garin nan ba,ka shiga ka yi wanka bara inje in karbo mana abincin karyawa."
Tashi Farouq ya yi yana,"Okay to shikenan. "
Ya wuce toilet shi kuma Javed ya tafi dauko masu abinci.

Dukkaninsu sunyi wanka,sun ci abinci daidai lokacin aka sanar da su cewa Mai Martaba ya ce a fito za a tafi.
Kai tsaye dukkaninsu suka fita.
Kowacce tawaga ta kowanni gari sun shirya suma an fito ana bankwana.
Sarkin Bida ne yasa a kira masa Farouq,Farouq na zuwa ya dunga sanya mishi albarka sannan ya mika masa wata jaka.
"Wannan kyauta ce ta mussamman, ka cancanci riketa,kila a yanzu ba ka san dalili ba amman ka rike wata raba zai yi ma amfani kuma za ka fahimta."
Karba ya yi cike da fara'a yana godiya.

Sauran sarakunan sai zuwa suke suna gaisawa da Farouq kafin su tafi.
A cikin ransa shi kansa ya gagara fahimtar dalilin hakan da kuma abun da yasa suke nuna masa kauna.

Zasu je su shiga mota tare da javed kenan mai martaba ya ce aa sai dai Farouq ya zo motarsa su tafi.
"Tare a motata zamu tafi."
Mai Mai martaba ya fada yana shigewa cikin motar.
Da mamaki duk suka bi mai martaba da kallo.
To mai zai sa ya ce Farouq ya shiga motarsa?
Shi kuwa Farouq ba tare da tsoro ko shakka ba ya shiga cikin motar a zuciyarsa yana karanto adduar shiga abun hawa.

"Bismillahi, Allahumma inni as'aluka khayraha wa khayra ma fiha, wa a'udhu bika min sharriha wa sharri ma fiha."

Ya shiga ya zauna.
Tunda ya shiga motar nan kan Mai Martaba ya shiga sara masa tamkar za a fisge, kokarin dafe

kan ya yi da karfi ya zauna.
Ina lamarin ya citura,da karfi ya ce,"A Dakata...."
[28/05, 11:08 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials

- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-17

Cikin firgici driver ya ja birki,yana jan birki duka sauran motocin ma suka tsaya cak.
"Yallaɓai,Lafiya?"
Nuna Farouq ya yi da hannu da alamar ya fita.
"Ya fita?"
Ya girgiza kai alamar eh.
Da mamaki Farouq ya bi shi da kallo,aka bude masa kofa ya fita.
Farouq yana fita Mai Martaba ya ji tamkar an zare masa azabar da yake ji.
Ya kalli security ya ce,"ka sa shi a motarsu Javed."

"An gama Ranka ya dade. "
Ya fada suna tafiya da Farouq,bude masa motar su Javed ya yi ya shiga kafin ya koma.

Farouq na shiga motar cikin yanayin rashin fahimta Javed ya kalleshi ya ce,"Ya lafiya dai."

"E, lafiya kamar Mai Martaba zai yi wayar sirri."
Farouq ya fada a gajarce.

Javed ya ce,"Okay shikenan. "
Nan aka ci gaba da tafiya suna yi suna hira, har suka isa cikin Mokwa.
Ana shiga Fada cikin hanzari Mai Martaba ya wuce bangarensa ko cikin fadarsa bai yi ba.

Yana shiga ya kulle kofa,ya fisge rawanin da ke kansa,babbar rigar ma ya jefar da ita tsakar dakin,hannu yasa a cikin aljihunsa ya dauko wani ɗan karamin tulu.

Yana budewa ya fara juya hannunsa wannan karamin mutumin ne ya kara fitowa.
Dariya mutum yake har yana tuntsirawa.
Shi ko Mai Martaba ya ɓata rai cikin yanayin fushi.
"Moli ka daina dariyar nan wannan lamarin yana da girma ba abun wasa bane."

Dariya ya ci gaba da yi sai da ya yi mai isarsa kafin ya ce,"Yo daman kai Abdul-Raheem kana ganin cikin sauki ake iya taɓa mai kusanci ga ubangiji? ai sai dai irinka masu Musa a baki fir'auna a zuci."

Ɓata rai Mai Martaba ya yi ya ce,"Ina ruwanka dani? Ni muyi abun da ya dameni,ke nan yanzu shi ba za mu iya taɓa shi ba ko yaya kake nufi?"

Dariya Moli ya yi kafin ya ce,"Za a iya samun nasara amman fa sai anci kwakwa na fada maka yaron sam baya wasa da lamuran ubangiji farilla da sunna kai har ma da mustahabi kuma taɓa irin wa innan akwai ƙalubale sosai bare shi har yanzu na rasa gane kan gabanshi bare bayanshi dole akwai manyan da ke tare da shi."

Mai martaba ya yi tsaki,"Yaron fa dan ƙasar malaysia ne ban jin cewa yana da riko da addini don yawanci yan kasashan wajen nan sukan fifita duniya ba wani practising addini suke ba."

Moli ya buga wata iska kafin ya kalli Mai Martaba,"Ku fa musuluncin da yawanku a bakine kawai yan nigeria su kuma yan kasashen waje musuluncinsu yawanci ga zuciya yake ba ga zahirin rayuwarsu ba,sannan wai kai yau ka yi tunanin za ka iya cutar da shi ne? kana son wasa da lafiyarka ko? Ka da ma kara wannan gigin cikin sauki."

Mai Martaba ya ce,"Eheen na yi tunanin zan iya kokarin dunkufar da shi ko samun wani abu dangane da shi amman maimakon hakan sai na fuskanci barazana yafi karfina ba zan iya zama inuwa guda da shi ba,ji nake tamkar mala'ika na kokarin zare raina."

Moli ya ce,"Ka sani komin makirci da karfin tsafinka kariyar ubangiji ta fi su tasiri,ka bani lokacin in gama bincikar shi din wane ne tukunna ta hakan ne kadai zamu iya samun damar sanya rauni ga karfin Adduoinsa sannan kuma ka dage wajen yin aikinka in zai samu bakinsa ya rufu kamar yadda akaiwa sauran duk da cewa ba mu san manufarsa ba."

Numfasawa Mai Martaba ya yi,"Wannan ba matsala zan yi kokarin rufe bakinsa tare da kawar da idanunsa akai na,amman nidai babbar damuwata ka samo mana mafita Don wallahi ni kadai na san azabar da na sha yau cikin mintuna kalilan ba don nasa ya fita ba inaga zan iya samun matsala babba kuma zaman wannan  zoben tamkar barazana ce ga rayuwata."
Dariyar mugunta Moli ya ci gaba da yi,"Dole a karbo wannan zoben dolene,dole ne domin shi ma din wata kariyace a gareshi sannan kai ka cancanci sanya wannan zoben ba kowa ba."ya karasa maganar yana wasu irin yare da sambatu kafin ya ɓace ɓat lokaci guda.

Yana tafiya mai martaba ya dauko wani ruwa shi ba ja ba kuma ba yellow ba a cikin kwarya ya kafa kai yasha yana sambatu sannan ya diba ya shafa a fuska da kuma tsakiyan kansa.
Wasu fararen kaya ya dauka yasa kafin ya hau kan gadonsa ya kwanta ,"Tun ranar farko zuciyata bata aminta da wannan yaron ba,Zoben nan mallakina na ne ba na shi ba,dawo ya

dawo hannunaaaaa."
Ya fada a zahiri yana shiga cikin bargo.

☆☆

Farouq suna shiga cikin Bangarensu bayan ya yi sallah sunci abinci Javed ya shiga cikin gida ya dauko jakar da Sarkin Bida ya bashi.
Hannu yasa a ciki ya zaro wani irin rawani mai kyau da sheƙi da daukan ido.
A zahiri Farouq ya ce,"Ko amfanin me wannan rawanin zai mun oho."
Ya na kokarin maidawa ciki sai ga zoben da ke hannunsa na sheƙi yana fitar da haske irin na jikin rawanin.
Tsayawa kallon ikon Allah  ya yi.

Yana maida rawanin kuma sai wutar ta dauke,alamu dai sun nuna cewa wannan rawanin da zoben suna da alaƙa mai karfi.

Karfe ɗayan dare daidai,Farouq ya hango wani yazo masa a siffar mutane baƙinƙirin ƙato,kokari yake ta karfi zai kwace zoben da ke hannunsa.
Cikin karfin hali Farouq ya dunkule hannunsa yana ihu.
Sheƙe masa wuya mutumin ya yi,da kyar yake numfashi yana ta kokarin cire hannunsa a wuyansa,ɗayan barin kuma ya ƙara dunkule hannun.
Da kafarsa ya fara kokarin dukan mutumin.
Yana sa hannu kan zoɓen sai ya fara wani irin jan wuta yana hayaki.
Ja yake amman sam zoben yaki fita ya maƙale hannun Farouq tamkare da shi yazo duniya.
Tun suna yi a kwance har suka tashi suna dambe da juna,sosai suka sha dambe har Farouq ya jiwa wancen mutumin a fuska shi kuma ya cijesa a hannu.
Ganin bai da alamun samun galaba akan Farouq yasa shi ya gudu.
A tsorace Farouq ya farka daga mafarkin da yake.
Kamar yadda Manzom Allah SAW ya umarta ga duk wanda ya yi mummunan mafarki ya yi addua ,"Allahumma inni a'udhu bika min sharri maa ra’aytu."
Hakan Farouq ya karanta yana goge zufar da ta gama jiƙa masa jiki.

Jin yanayin jikinsa ya yi ya masa nauyi sosai,hasken da zoben yake yasa shi kunna wuta domin ya gagara daga hannun da zoben yake.
Yana kunnawa kuwa yaga jini na zuba ga alamar cizo nan asaman hannunsa daf da yatsan da zoben yake.

Cikin jin mamaki ya furta,"Ke nan ba mafarki na yi ba? A gaske hakan ya faru? To ina mutumin? Me yasa ban ganshi a dakin nan ba."
Ya karasa yiwa kansa tambayoyin yana tashi.
Duba lungu da sako na dakin ya yi,ba alamar mutum sannan kuma kofarsa ma tana nan a kulle kamar yadda ya bari.
Gajiya ya yi ya koma ya daure wajen cizon.

Ya koma ya kwanta kenan yana kashe
Motsi yafara ji a karkashin Gadonsa hakan yasa shi saurin sunkuyawa
[31/05, 9:21 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials

- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-18

Yana sunkuyawa yaga babu komai bare alamun wani abu,duk da hakan bai yarda ba ya kunna hasken wayarsa ya haska sai da ya tabbatar bai ga komai ba kafin ya koma yana ajiyar zuciya a kan gadon.
Ji ya yi barcin da ke idanunsa sun kafe kaf ya gagara komawa,hakan yasa ya tashi ya je ya yi alwala ya yi nafila.
Har gari ya waye bai koma ba karshe ma hira suka fara yi da Zoe sai da lokacin sallar asuba ya yi kafin ya yi mata sallama ya je ya yi sallar,yana idarwa kuwa wani irin barci ya cafkeshi take ya koma kan gado ya kwanta.

Kamar wasa Javed ya ga har karfe takwas ta yi Farouq bai fito ba kuma yasan yawanci bai cika barcin asuba ba,har an kawo masu abin karyawa ya ci nasa amman ba alamun Farouq,hakan yasa  ya gagara jurewa ya tashi ya nufi dakin.
Buga kofar ya fara yi cikin magagin barci Farouq ya tashi ya bude.
Da mamaki Javed ya kallesa ,"Oga wai yau kaine da barci haka?"
 Miƙa Farouq ya yi, "Wallahi kuwa wani irin sahihin barci ne ya kwasheni ina idar da sallah dake jiya ban wani samu dama ba."

Idon Javed jaraf akan hannun Farouq,"Subhanallah me ya sameka haka a hannu?"
Javed ya fada cikin yanayin nuna damuwa.

Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Ciwone na ji jiya da daddare a toilet,ka ga bara inyi wanka inzo."
Ya fada maganar yana saurin wucewa domin katsewa tambayoyin Javed.

Wanka ya yi ya shirya sannan ya fita falon ya samu Javed,Zama ya yi ya fara karyawa,hayaniyar mutanen da ya fara jiyowa yasa shi dakatawa yana kallon Javed.
"Wannan hayaniyar fa lafiya kuwa?"

Javed ya ce,"Lafiya lau,ni na manta ma ashe yau ne ake murnar bikin Gani na nan

mokwa,maraba da dawowa daga Bida da kuma murnar bikin Ganin na shekara sai da na fita dazu na gani."
"Oh Ma sha Allah,Shiyasa na ga ka dauko rawani kenan."
Farouq ya faɗa yana kallon rawanin dake gefen Javed.

"Yes kasan dole a naɗa asa kayan gargajiya ko mai martaba ya yi hukunci." Javed ya faɗa.
Farouq ya ce,"Nima ko ina sha'awar yin shiga irin takun nan kuma daman an bani kyautar rawani,da zan samu kayan sai insa."

"Me zai hana? Ai sai in baka akwai sabin kaya da ban saba kasan lokaci zuwa lokaci duk ake sabunta mana kayyayyaki irin na al'ada ko da baka da rawani ma ai dole a nemo indai kana son sawa." Javed ya fada cike da zumudi ya tashi ya je ya daukowa Farouq manyan kaya da alkyabba dukkanin su sabi fil ruwan ƙasa.

Da farinciki Farouq ya karɓa yana "aiko gasu kalan rawanin nawa har ma takalmin. "
Ya karasa maganar yana daukan takalmin.

Javed ya ce ,"To yanzu dai ka gama cin abincin naka zuwa  bayan la'asar zamu shirya za a fara bikin in ka gama sai mu dau rawanin mukai a naɗa maka a ajiye sai sawa kawai."
Farouq ya girgiza kai yana fara kai luma abunsa.

Gida anata shige da fice ana gyare-gyare da girki girki da ma shirye-shirye domin duk da gidan cike yake da adon gargajiya da sarauta na yau ya bambamta da kullum domin an kara tsara komai cikin ƙawa.

Misalin Karfe Hudu daidai an fara taro kowa da kowa na gidan sun hallarci farfajiyan filin da ake taron hatta mai martaba anata raye-rayen da kaɗe-kaɗen gargajiya illa Farouq da Javed da suketa fama da rawani da kyar aka samu aka daidaita ya zauna.
Shigar sarautar ba ƙaramin kyau ta yi Farouq ba wanda ya zarce misali domin kuwa ba zai taɓa misaltuwa.
Javed ya ce,"Ya Subhanallah Oga ka ganka kuwa? Yoo ni ko sarki ban taba ganin yayi kyau cikin kayan nan kamar yadda ka yi ba,gaskiya tsaya inyi ma hoto tukunna in samu da na status a tiktok kuwa na san sai ka kaini viral ba makawa. "

Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Kai dai baka da dama."

Hotuna Javed ya dunga yi masa,ya masu selfie tare sannan suka fita.

Jinin sarauta,izza da kamala,ƙasaita da duk wani  shauƙi na sarauta sun gama bayyana ga takun Farouq,wani yanayi ya riski kansa na jin tsantsar ƙasaita da ba zai iya kaucewa hakan ba.

Cikin izza suke tafiya har suka isa farfajiyar taron,sheƙen da rawanin kansa da zobensa da suke shi ya fara aikawa da al'ummar wajen saƙon isarsa.

Kallon kallo aka fara yi yinyin da idannun kowa ya koma kansa.
Abba Malik na bude baki,"Abdul............"
Tsintar kansa da kasa ƙarasa sunan ya yi yana jin tamkar wani dutse ya maƙale masa a wuya.

Hajiya kaka kuwa kwakwalwarta ce ta fara dawo mata da rayuwar baya,tana so ta gano wani abu amman lamarin ya citura,dafe kanta ta yi tana,"Ina yake....ina yakeee."

Kilishi kuwa zare idanu ta yi cike da mamaki," lallai wannan ba mutum bane."
Ta furta a zahiri ba tare da ta sani ba.

Wani irin kallo mai martaba ya bisa da shi yana zare idanuwa "Zargi na ya tabbata zai juyar masu da tunani zai dawo da su,zasu fahimta,zasu tuna,baka isa ba,wallahi baka isa ba."
Ya karasa maganar ya ciro wani gari ya fesa.

Hajiya kaka na kokarin faɗuwa kenan Farouq ya yi saurin karasawa ya tareta,"Amarya ta ga angonta ya yi kyau ta tsure harda shirin faduwa. "
Ya fada cikin sigar tsokana.

Lamura sun ci gaba da tafiya amman gabadaya zuciyoyin Mai Martaba,Abba Malik,Kilishi da Kaka cike take fal da damuwa kuma a cunkushe mussamman Hajiya Kaka da Abba Malik da abun yafi daurewa kai.

Mutane sai zuwa suke ana hoto da Farouq yadda ake damuwa da yin hoto da Sarkin Al'adu wannan karan ko ta shi ma ba ayi gabaɗaya rububi ake akan Farouq kowa burinsa ya yi hoto da shi kuma mussamman da yake labarinsa ya baza gari kan abun da ya faru a Bida sai nuna shi ake ana ai shine ance dan baiwa ne.

Wani tsoho ne tukuf ya karasa inda Farouq yake ya shafa fuskarshi kafin ya ce,"Kai ne kadai zaka kawo karshen zalinci kai ne zai ka fito da tsagwaran gaskiya,ina rokon ubangiji da ya yi maka albarka kuma ya tsare ka da tsarewarsa tare da kariyarsa sannan ya maka lulluɓi da albarkarSa."

Farouq ya amsa da Ameen duk da cewa bai gama fuskantar abun da tsohon ke faɗa ba.
Hannu yasa a aljihunsa ya ciro wani dumin kudi ya miƙawa tsohon ya karba yana kara sa mishi albarka sannan ya tafi.

Janinah sai cizon yatsa take tana takaici,"shi wai wannan kowa sonshi yake ne? Sai kace Aljani Mtswwww. "
Ta ja tsaki tana kallonsa.
Suna hada sai ta galla masa harara.
Shi ko da murmushi yake binta.

An yi shagali anci an sha an watse.
Farouq ya bazu a social media yan nigeria mussamman mata sai reposting ake da ga Asalin Mijin Novel ya bayyana har da masu rubuta wasikar soyayya,lamura dai kala kala,suna zaune a falon Hajiya Kaka da dare Javed sai dariya yake yana nuna masu,"Oga ka baza capacity fa ka tashi kan yan matan nigeria ko ina aka bude lamarinka ke trending tiktok,Instagram,Twitter,Facebook har WhatsApp status kawai kaine harda me cewa ita in ba kai ba ba zata yi aure ba harta mutu. "
Caraf Hajiya Kaka ta taɓe baki tana faɗin,"Aiko dai saidai ta mutu ko ince su mutu ma don dai wannan kam nawa ne ni kadai,ko ba haka ba Mijin?" Ta fada tana kallon Farouq.
Daga mata gira ya yi yana,"Sosai ma Amaryata Yan matana ai daga ke ba ƙari ke ɗaya ce."

Janinah ma da taga abun yaƙi karewa ko ina ta bude shi ke yawo tuni taje tana nunawa Kilishi,wani yanayi da bata saba riskarta ciki ba ta ganta,"Aunty Kilishi kin ga ko ina fa hoton wancen banzan bakon ne."
Kawar da kai Kilishi ta yi tana,"Kin ga Janinah kije da safe zamuyi magana yanzu kaina na ciwo."
Ba yadda Janinah ta iya haka ta fita amman zuciyarta cike fal da tarin tambayoyi domin bata taɓa ganin Kilishi a yanayi na damuwa kamar na yau ba.
Dakinta ta wuce ta kwanta abunta.

Shi kuwa Mai Martaba Moli ya gayyato cikin fushi da ɓacin rai yana yi mishi magana,"Shin ka ga rawanin da ya sanya? Ka ga rawanin da ke kanshi? Ka ga yadda siffarsa ta kasance a cikin kayan nan?  Ka kasa gano mun shi wane ne tawagarka ma sun kasa,kenan yafi karfinku? Anya ma mutum ne kuwa? Na ce anya ma mutum ne kuwa? Na fara tantama wannan ba mutum bane,kuna gani za a gaba bayana,kuna gani karshena zaizo."
Ya fada yana buga bango.
Dariyar muguntar da Moli ya saba ya yi kafin ya tsagaita ya  ce,"Kai Abdul-Raheem Hattara dai na ce hattara dai,wannan yaron mutum ne kamarka na fadama na sake fada ma mutum ne kamarka kusancinsa ga ubangiji ne mai girma sannan lamarinsa dauke yake da matukar sarƙaƙiya aiki akansa muke ba dare ba rana wanda sanadinsa har wani cikin yarana ya samu matsala,ba shi bane wanda kake tunani domin ba zai taɓa zama shi ba don ya sa wannan rawanin in zaka kwantar da hankalinka ka kwantar."

Cikin fushi mai martaba ya ce,"lamarin ya kai ni makura kuma cikin daren nan zan dauki matakin da kuku kasa dauka."

Dariya Moli ya fara yana,"Ka dauka,ka gwada dauka za ka kai kanka ga tona ramin da ka birni." Ya ci gaba da dariya kafin ya ɓace.

Dare ya yi,kowa ya tafi daki sunyi barci.
Karfe Ɗaya Daidai Farouq na zaune gaban System sai ji ya yi ana taɓa kofarsa.
Zura key aka yi aka bude aka shige,wani mutum ne dauke da wata doguwar bakar riga data

rufeshi daga sama har ƙasa.
,“Lā ilāha illā anta subhānaka innī kuntu mina-ẓ-ẓālimīn.” Farouq ya furta cike da firgici.
Daga abun da ke fuskarsa ya yi,ya bude.
Suna haɗa ido ya ga mai martaba ne.
Wani irin faduwar gaba ya ji yana ja da baya.

Mai martaba ya ce,"Kai wane ne? Ka fadamun kai wane ne?"

Farouq ya ce,"Ni ba kowa bane kuma nima ban san ni wane ne ba."
Cikin Fushi Mai Martaba ya zaro wuƙa yana shaƙo Farouq,"Ka faɗa mun kai wane ne ko in kasheka."
Cikin daurayi Farouq ya ce,"Sai dai in ka kashenin bare kuma ba ka isa ka kasheni ba har sai in kwanana ya kare."

Kara sa masa wukar ya yi akan wuya yana,"Ba zaka fada ba kenan? Zan iya kasheka yanzu in kashe banza anan ba tare da kowa ya sani ba,amman a halin yanzu nafi son insan kai wane ne sannan kuma ina Umartarka da safiyar gobe ka shirya ka bar kasar nan tun kafin ni da kaina ɓatar da kai."

Farouq ya ce,"Kai ya kamata in tambaya ni wane ne,sannan kuma baka isa ka ɓatar dani ba in kana hakan kana cin nasara to ka gwada akaina ka ga ko  zaka ci."

Shaƙesa ya yi yana kokarin daba masa wukar Farouq ya yi saurin kaucewa ya kwantar da shi yana karbar wukar shima yasa mishi kan wuyansa yana,"Ni ba zan kasheka ba,amman zanyi ma illar da sai ka ji cewa dama mutuwar kayi,kuma ina umartarka da ka bar dakin nan tun kafin in tarama jama'a,sannan kasa aranka ba zan taɓa barin gidan nan ba sai aiwatar da kudirina."

Murya na rawa Mai Martaba ya ce,"Daga sai in fita to don Allah ka barni karka tada kowa."
Daga shi Farouq ya yi da wukar a wuyansa har sai da ya hankadeshi waje kafin ya kulle kofarsa ya jefar da wuƙar gefe.

Ficewa daga masarautar Mai Martaba ya yi cikin daren ya shiga wani daji yana tone tone.

Shi ko Farouq ajiyar zuciya ya yi ya koma ya ci gaba da aikinsa da yaga ma ba zai iya ba karshe kwanciya ya yi.
Yana fara barcin babu wanda yake mafarki illa wannan tsohon da ya yi masa addua da yamma.
Kasa hakuri ya yi karfe hudun asuba ya je dakin Javed ya tasheshi.

"Lafiya Oga?"
Javed ya fada.
Farouq ya ce,"Lafiya lau,kasan gidan wannan tsohon da ya yi mini addua dazu?"

Javed ya ce,"E kwarai a cikin gari yake."

Farouq ya ce,"To muna idar da sallar asuba zaka rakani Don Allah ."

Javed na washe barcin da ke idonsa ya ce,"Lafiya kuwa?"

Farouq ya ce,"Lafiya lau ina so in kara masa abun da na basa ne."

,"To kuma shine da asuba bazamu bari sai safiya ba?"

Farouq ya ce,"E ba zan iya hakura ba mafarkinsa nake."

Suna yin sallar asuba kuwa suka fice daga masarautar.
Wani ƙaramin gidan laka ne da duk ya gama jin jiki ya rurrushe duk an yi ciko da leda.
Javed ya ce,"ga gidan nan....
[31/05, 9:21 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN KARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT

*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-19

kallon Gidan Farouq ya yi yana,"To ka ɗan taimaka ka yi muna sallama da shi mana."
Javed zai yi magana kenan sai ga Tsohon ya dumfaro inda suke,ga dukkan alamu daga masallaci yake,tsoho ne tukuf da kyar yake tafiya da sanda.
"Ah Javed kune? Ince dai lafiya?"

Javed ya kalli Farouq ya ce,"Lafiya lau Baba Bakonane ke son ganinka ya ce sai mun zo yanzu na yi na yi ya bari sai safiya yaki."

Wani matsakaicin Murmushi ya yi ya ce,"Daman nasan za a rina,Ɗan samari sannunka ko zamu ƙarasa soro ne?"

Farouq ya ce,"E gaskiya zan so hakan,yanzu kai Javed ka koma gida kar a fahimci bama nan in mun gama da Baba zan tawo."

Javed ya kallesa yana,"Okay to amman dai zaka gane hanyar ko?"

"In sha Allah. " Farouq ya fada.
Baba ma ya ce,"ko bai gane ba ai na rako shi."
Tafiya Javed ya yi ya barsu,suka shige zauren gidan sannan suka zauna kan taburma.
Baba ya ce,"Mene ne tafe da kai yaro?"
Gyara zama Farouq ya yi da kyau kafin ya ce,"Cikin mafarkina ya nuna mini cewa kana dauke da hasken da zaka fiddani daga duhun da nake ciki in daina lalube sannan kuma zuciyata ta ƙara gasgata mun hakan ya yin da ruhina ya aminta da cewa lallai akwai abun da ka sani game dani."
Numfasawa Baba ya yi kafin ya ce,"Ina mahaifinka?fatan yana cikin ƙoshin lafiya?"
Daga kai Farouq ya yi yana yiwa Baba kallon rashin fahimta cike da tuhuma.
"Mahaifina? Shi ne abun da nake nema Baba,kuma shi ne nake jin cewa kana da masaniya akan inda yake domin har yanzu na gagara gasgata shin wane ne mahaifina cikin gidan masarautar al'adu,Mai Martaba ko Abba Malik? Sam babu mahaifina ciki,shi na zo nema amman na lura da cewa tamkar babu shi ma a duniya da tarihin masarautar abun da na riska ya bambamta da abun da mahaifiyata ta sanar mini."

Baba ya ce,"Na ji mamaki matuka da kace mahaifinka ka zo nema,domin a tunanina mahaifinka ne ya turoka domin daukar fansa indai hakan ya tabbata abun da kake fada to tabbas lamarin da girma yake."

Farouq ya ce,"Babu shakka Mahaifiyata bata ƙara sa mahaifina a idanunta ba tun daga ranar da ya kaita filin jirgi domin komawa ƙasarta har kawo yanzu da nake zaune a gabanka."

Girgiza kai Baba ya yi kafin ya ce,"Gatan da zanyi maka bai zarce ace in baka tarihin abun da na sani ba domin kila a ciki zaka samu hasken da kake da buƙata."

Gyara zama Farouq ya yi yana fuskantar Baba

" Nine Malami na farko ga gidan sarkin al'adu tun lokacin da Kakanku ke raye Mai Martaba Abdul-Alim,ni ke bincike da shige da fice kan duk wani abu na tsaro da tsafi dake guduna cikin masarautar domin kuwa ni amintacce ne kuma amini ga Mai Martaba hakan yasa na san komai shige da ficen wannan gidan,Mahaifinka su biyu Allah ya fara bawa mai martaba da shi da ɗan uwansa Abdul-Raheem wanda ya kasance sarkin al'adu na yanzu kasancewar kakarku ta yi jinkirin haihuwa an sha shige da fice kafin zuwansu duniya wanda har kai ga dukkanin su ana haifarsu  muka fara duba taurarin rayuwarsu akaron farko Maihafinka Abdul-Rasheed da yake babba manuniya ta nuna cewa shine ya cancanci gadar sarautar kakanku domin shi ne ya gado kyawawan dabi'u irin nasa saɓanin Hussaini Abdul-Raheem
Dukkaninsu sun taso cikin gata da soyayya matuka ya yin da suka fara girma sun kammala karatuk sakandare sai Mahaifinka ya buƙaci da a turasu ƙasar waje domin yin karatu a bangare kimiya wato na'ura,
A lokacin an haifi Baffanku Abdul-Malik da Khaleesa
Mai Martaba ya amince da hakan amman sai dai inda gizo ke tsaƙar shine Abdul-Raheem sam karatun baya gabanshi saboda zaɓin Abdul-Rasheed ne ba na shi,baya karatun kuma ba ya

maida hankali illa sanyawa mahaifinka karar tsana da ya yi ganin cewa Mai Martaba na matukar ji da shi da kyawawan dabi'unsa.
Har ya kai ga Abdul-Raheem kullum yana cikin shiga da rayuwa irinta sarauta tsangwama da kyarar mutane kuwa ba a magana duk da cewa mai martaba na kokarin tsawatar masa amman ba hakan ke sawa ya daina ba sai dai ya rage aikatawa a gaban idanunshi,shi kuwa Mahaifinka tamkar ba ɗan gidan sarauta ba,rayuwa yake daidai data kowa cike da girmamawa.

Karshe Abdul-Raheem daga zuwa hutu yaƙi komawa makaranta ya zauna a fada,shi kuwa Abdul-Rasheed sai da ya kai wani babban mataki da ba zan iya cewa mene ne ba tunda ba bokon muka yi ba amman dai bana mantawa dawowarshi an shirya shagali mai girma na tarɓarsa wanda bikine da ba a taba yin irinsa ba a tarihin mokwa inda ya haɗa manyan sarakuna na nigeria da kewaye wannan bikinma ba ƙaramin tadawa Abdul-Raheem hankali ya yi ba domin kuwa gagara boye hassadarsa ya yi ban mancewa har tsoron shi mahaifinka ya fara ji ya dakesa ya bigesa kuma ya kwace masa abubuwa amman mahaifinka bai taba faɗa ba ita kuwa kakarku data fahimci hakan sai ta sanya aka raba masu ɗaki amman duk da hakan bai tsira ba
ana cikin hakan ya samu aiki a kasar Netherlands inda ya koma cen na tsawon shekara uku cif ina kyautata zaton cewa anan ne ya haɗu da mahaifiyarka suka fara soyayya wanda har tsautsayi ya gifta tsakani akai yi cikinka ba tare da aure ba,ganin hakan ya sa mahaifinka dawowa gida da ita bayan ta musulunta iyayenta sun gujeta kan cewa zai aureta inta haihu,bai sanar da kowa cewa tana dauke da ciki ba illa ni kadai domin a lokacin kakanku na jinya kwance babu lafiya rai a hannun Allah.
Hakan yasa Abdul-Raheem ne ke kula da duk lamura na masarautar kuma daman abun da yake da buri kenan.
Zuwan mahaifinka da mahaifiyarka ya ce sam ba za a shigan masu da kafura cikin ahali ba su ba za su abun kunya ba,a lokacin Khaleesa duk da tana da ƙarancin shekaru amman ta bawa Abdul-Raheem goyon baya sosai domin tare suka yi shige da ficen da don dole sai aka sa mahaifinka ya nemawa mahaifiyarka tikitin gaggawa na komawa kasarau domin kuwa lamarinta har sai da ya kai ga mai martaba babban sarki na bida ya shiga ciki lamura dai marasa dadi sosai cike da tozarci da cin mutunci duk yadda na so domin kwantar da lamarin abun ya cutura sai da na zam ɗan kallo,
Bayan mahaifiyarka ta koma ba jimawa Allah ya dauki ran mai martaba ya yin da aka fara shiri gadan gadan domin naɗa Abdul-Rasheed nan fa Abdul-Raheem ya fara sabon shiri da na shi aikin,kowa ya san Abdul-Rasheed ne ya cancanci zama sarkin al'adu kuma shine wasiyar mai martaba.
Hakan yasa Abdul-Raheem ya shiga ya fita ya fara kokarin duk yadda zaiyi ya yiwa mahaifinka Kurciya mai dauke da mutuwa da yazo mun da lamarin naki aminta da hakan karshe sai ya fita sabgata ya bi hanyoyinsa tare da shiga kungiyoyi domin tabbatar da burinsa.
A karshe ya yi sa'a domin kuwa an wayi gari an tashi babu Abdul-Rasheed babu labarinsa kuma bakin kowa a rufe babu wanda yake batunsa tamkar anyi ruwa an dauke,ya rufe bakin kowa ta yadda kowa zai manta da batunsa inko mutum ma yyi kokarin tunasa ko tada zancen karshe ya kan iya rasa ransa,Don dole aka naɗa shi sarkin al'adu na mokwa ya yin da ni kuma ya yi fatali dani daga cikin gidan tunda dai ni ba zai iya mun komai ba kar tasan kar ne,to

wannan shi ne dalilin da yasa ba ka jin ana batu ko labarin mahaifinka hatta kakarku da ta fara tuna shi take ficewa a hayyacinta domin ya riga ya yi aiki mai karfi akan hakan sannan yanzu abun da zaifi daure masa hankali shine bai san da cikinka ba kuma a tunaninsa yanzu mahaifinka baya raye tunda kurciyar mutuwa ya yi masa, mun yi artabu sosai  nayi kokarin hana shi aikata hakan amman na gagara yana amfani da shedanun aljanun da suka fi karfina ni kuwa ina ganinka jikina ya bani cewa kai Ɗan Abdul-Rasheed ne."

Idanun Farouq ya yi jajur
Ba don namiji bane kuma jarumi hawaye ba zai taba saurin tsayuwa daga idanunsa ba bare ƙin zuba.

Wata irin ajiyar zuciya ya yi
"Kenan dai yanzu ba asan inda mahaifina yake ba? Yana raye ko baya raye ?"

Baba ya ce,"Kwarai kuwa amman ina ji araina cewa yana raye,kuma yana rayuwa mai inganci da jin dadi,kai zaka nemo shi amman ka sani sai ka yi taka tsantsan da Abdul-Raheem mutum ne mai hatsari matuka yana kuma girmama al'ada da kiyayeta ba kadan domin ta hanyar yake samun aiwatar da munanan lamuransa nima zan taimaka maka iya yina har mu kai ga cin nasara domin akwai wani babban sirrin da na gano nake son sanar da mahaifinka in Allah yasa ka nemo shi."

Farouq ya dafe kai yana,"Na fahimta,tabbas na fahimta kuma ba makawa indai mahaifina na raye cikin duniyar komai nisa da fadin inda yake zan nemoshi da karfin ikon Allah."

Baba ya ce,"Allah ya baka iko amman ina kara jaddadda maka cewa ka yi a hankali domin kuwa cikin daren jiya ma na jiyoshi yana zama da manyan muƙarabbansa iblis,ifrit,da su zalambur,kuma duk akanka suke aiki."

Wani irin yanayu Farouq ya fara ji duk da cewa a zaune yake amman jiri yake ji idanunsa na kokarin rufewa.
Murya na rawa ya ce,"Baba bara in tafi zan dawo."

Baba ya ce,"zaka iya tafiya ko in rakaka dai?"

"Aa na gode zanje ka zauna."

Ya fada yana tafiya.
Har gari ya yi haske rana ta fito.
Tafiya Farouq ya dunga yi kamar ɗan maye,a hankali har ya shiga part din Javed.
Yana shiga kuwa ya faɗi a kasa tum tamkar wanda aka hankaɗa.
Da sauri Javed ya tashi ya karasa....
[02/06, 6:28 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!

*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAGE-20

Dakyar Javed ya yi kokarin daga shi ya shigar da shi ɗaki yana,"Subhanallah Oga me ya faru? Lafiya?"
Daga masa kai ya yi alamar eh yana ajiyar numfashi.
Raɗaɗi da azabar da kansa ke yi masa tamkar zai tsage hakan yasa shi saurin rike wajen,daga kan har gangar jikin ko ina ya dauki wani irin zafi tamkar wuta.
Javed da yaga lamarin kara girmama yake ya rasa yadda zaiyi da gudu ya fita ya kira BabanGanye.

Aiko yana zuwa ya tafa kan Farouq da jikinsa sannan ya ce,"Harda ciwon kai ne ko?"
Nan ma daga masa kan kawai Farouq ya yi ba tare da iya furta komai ba.
BabanGanye ya kalli Javed yana fadin,"Daman ko dazu na kammala dafa ganyen dogon yaro (Neem) da na ganyen ɗanyen allayahu wa inda daman su haɗi ne mussamman domin maganin ciwon kai da zazzabi mai tsanani ka ga ke nan anyi sara akan gaɓa In sha Allah yana sha nan da yan mintuna zai samu sauƙi amman in ce dai ya ci abinci?"

Javed ya ce,"Aa Baba bai ci ba gaskiya."

BabanGanye ya ce,"Dole sai ya ci abinci domin kuwa babu dama ya sha ruwan maganin nan ba tare da ya ci abinci ba akwai matsala ko yane ana bukatar ya ci wani abu tukunna."

Tashi Javed ya yi yaje ya haɗawa Farouq kakkauran ruwan shayi,ya tallafa masa ya zauna sannan ya samu ya sha ɗan kadan.

"Yawwa to da babu dai gwara babu dadi yanzu bara muga ko nan da mintuna biyar ne ruwan shayin ya dan sauka da kyau sai asha maganin,ka san fa ba sai maganin bature bane ake so aci abinci kafin asha,hatta namu ma na gida yana da ƙa'idoji,dokoki da kuma tsari."
BabanGanye ya faɗa.

Sai da ya dan hutu na mintuna kafin aka bashi ruwan maganin ya sha rabin kofi.
BabanGanye ya zuba masu wani a gora sannan ya ce,"Ga shi nan zuwa yamma zai iya kara shan rabin kofi,sannan kuma a tabbatar ka da asha ya zarce kwana uku duk da dai ma na san iya shan na yau ya isa zai samu sauki."

Javed ya ce,"Ok To Baba Allah saka da alkairi mun gode sosai."

"Ameen Allah kara sauki ko."
Ya fada yana kallon Farouq wanda idanunsa a rufe ma suke kam,haka kuma dayan hannunsa na kan kanshi ya kankame ban da ruwan hawaye babu abun da ke kwarara daga idanunsa.

Zama Javed ya yi kusa da shi yana,"Oga ko dai wani abu ya faru ne? BabaMalam dinne?"

Girgiza masa kai Farouq ya yi.
Ban da tuna maganganun Baba babu abun da yake yi mussamman "Aka samu cikinka ba ta hanyar aure ba...Ya yi wa Mahaifinka kurciya mai ɗauke da mutuwa."
Wa innan maganganu biyun ne suka dunga yawo a kwakwalwar Farouq.
"Me yasa Maah bata faɗa mun cewa bata aure aka same ni ba? Me yasa? shin yanzu mene ne matsayin rayuwata? ke nan ba musuluntar da mahaifiyata ta yi ba ne kadai zai zame mun za me mun kalubale ba harda kasancewata a matsayin wanda aka haifa ta haramtacciyar hanya? duk da cewa ban ta so da son duniya da abubuwan da ke cikinta ba amman babu shakka a yau na kara jin cewa dama ace ban kasance a cikinta ba, Astagfirrullah! Ubangijina na tufa ka yafeni amman a yau kai kadai ka san zafi da ƙunar da nake ji a cikin zuciyata,na so in maida komai ba komai ba in nemo mahaifina amman kuma yanzu ji nake na gaza ba zan iya ba! ba a haifeni ta aure ba, na gama zama a kasar nan ban ga amfanin kasancewata anan ba na hakura da komai domin sani ko nemo mahaifina baya da amfani gareni tafiya zan yi,tafiya zan yi."
Ya karasa laburta hakan a zuciyarsa yana ƙara sakin wasu zafafan hawaye wasu na bin wasu.

Cikin ikon Allah kuwa ciwon kan ya ragu masa cikin kashi ɗari bai fi saura kashi talatin ba,sannan zazzaɓinma ya tafi.
Javed na komawa daƙin ya ganshi zaune ya yi tagumi,komawa ya yi ba tare da ya ce masa komai ba ya dauko masa abinci.

"Oga ga abinci nan ka samu ka ci ka ga tun safe ruwan shayine kadai a cikinka." Javed ya fada yana kokarin zuba masa.

Cikin muryar damuwa Farouq ya ce,"Aa kar ka zuba please ba zan iya cin komai ba a halin da nake ciki yanzu kam bakina baya mun dadi komai ba dadi sannan ina ga gobe zan tafi indai na samu flight. "

Ajiye Abincin ya yi cikin sauri ya karasa kusa da Farouq,"Subhanallah Oga me aka yi ma? ko dai anyi ma wani abune a gidan nan? ka yi hakuri ka fadamun ko me ne ne Don Allah za a gyara."

Murmushin karfin hali ya yi ya ce,"Aa Maahnah ce bata ji dadi ba bata da lafiya shi ne duk hankalina ya tashi amman babu abun da aka yi mini a kasar nan ma duka."

Javed ya ce,"Ayyah dole ka shiga damuwa,Allah ya bata lafiya,amman dai in kaje ka ganta ta ji sauki zaka dawo ko?"

Farouq ya ce,"In sha Allah. " a zuciyarsa kuwa cewa yake ,"Ni bama kasar nan ba duniyar gabaɗaya ji nake tamkar in barta,in mutu in huta. "

Ranar wuni Farouq ya yi zuciyarsa cike fal da damuwa da ya fara neman flight kuwa cikin sa'a ya samu wanda zai tashi gobe da yamma hakan yasa ya kudurta aranshi cewa gobe da sassafe zai bar mokwa ya je Abuja domin anan zai hau jirgin.

Suna da meeting da 5stars wanda aka saba conference call tunda aka fara duk suka fahimci cewa Farouq na da damuwa domin ko yar tsokanar da ya saba yi ma bai yi ba kawai komai akace sai da ya bisu da Yes ko Okay.

Cikin zolaya Haidar ya ce,"Wannan fa ina jin sarautar ta motsa ne kodai a kira maka gimbiyar taka ne?" Ya fada ya kwallawa Zeeyter kira.

Zeeyter na zuwa ta kalli Farouq duk da cewar a waya ne amman tabbas jikinta ya bata cewa akwai babban lamari.
Ta ce,"Aa yanzu ku dai yau a yafe mana meeting dinnan,ku ci gaba da yi ni bara inje muyi na mu da friend."

Khalil ya ce,"To ai muma duk jikinmu ya yi sanyi anya zamu iya wannan meeting din ? Kawai dai a sauke na yau din ku je ku tattauna."

Farouq ya ce,"No ba komai fa a ci gaba kawai ban jin dadi ne."

"Aa kam an dakata ai kuma kar ka manta dukkaninmu ɗayane kuma ba zamu taba jin dadin kasancewa a halin da muka ganka ciki ba." Zahra ta fada.

Zeeyter ta ce,"Yawwa Taurari biyar dina da aka hanani zama ta shida yanzu bara mu je byee all,Oga muje."
Ta karasa maganar tana dagawa Farouq hannu.

Katse wayar suka yi duka.
Zeeyter ta kirashi privately
Ta ce,"Faɗa mun mene ne matsalar?"

Farouq ya ce,"Ko na faɗa wannan ba wacce za a iya mun maganinta bane."

"Ka manta cewa babu abun da yafi karfin Ubangiji ko da ace ya fi karfin mutum? Ai addua ma takobi ce mai karfi ko and ban yi tunanin cewa akwai abun da zaka gagara faɗa mun ba kamar yadda muka san damuwoyin juna. "

Numfasawa Farouq ya yi kafin ya ce,"So nake gobe in bar nigeria in koma malaysia ba zan iya zama ba kuma ko na zauna ma babu amfani."

Zeeyter ta ce,"What?? Ban gane ba fa ai ba ka gama abun da ka je yi ba ko kuwq an samu Baban ne?"

Farouq ya ce,"Aa."

"To me ne ya faru? Ko sai mun zo dinne dai,wani abu ake ma? Ka fadamun meke faruwa please na shiga damuwa."

Zayyana mata duk abun da ke faruwa Farouq ya yi sannan ya ci gaba da fadin,"kin ga ke nan zamana anan ba abun da zai janyo mun illa kaskanci da tozarci na tabbatar da cewa suka san cewa An samen ne bata hanyar aure ba sai anmun tozartar da ta zarce wacce aka yiwa mahaifiyata,da a zuciyata ina jin cewa zan iya daurewa in nemo mahaifin nawa amman yanzu na karaya ba zan iya ba,gida zan tafi na gwammace in ci gaba da rayuwa a haka har karshen numfashina in zan rayunma kenan."

Zeeyter ta ce,"Kar ka manta cewa komai yana da dalilin faruwarsa kuma ma kai ai gwanda kai ni fa da banma san ta ya aka haifenin ba kuma ban san ko da ɓarin tsinke ba na iyayena bare danginsu,shin na kasa komai? Na ce ba zan rayu ba? Zan gwama da kyarar mutane sam bata gabana,ansha yi mun gorin asali amman ko da wasa ban taba sa hakan araina ba bare ya dameni ko ya kawo mun damuwa tun suna yi har suka gaji suka dawo yabamun,saboda na yarda da Allah kuma na san cewa shiri da tsarinsa shine daidai ga rayuwata."

Farouq ya ce,"Nima na yarda da kaddarata amman dai tafiya gida shi ne mafita gareni a yanzu."

Zeeyter ta ce,"Okay amman ka yi hakuri zan kira Zahra ta zo muyi magana tare duka kafin sauran su shigo."

Kafin ya bata amsa ta inviting Zahra,tana yin joining kuwa ta fada mata duk abun da ke faruwa.

Zahra ta numfasa kafin ta ce,"Ba a fushi da tsarin Ubangiji kuma ba a fidda rai da rahmarsa ka sani cewa ka zo duniya ne da izinin Allah, ba tare da kuskure daga gare Ka ba. Ka kasance abin ƙauna a wajen Ubangijinka, kuma ba ka da laifi ko ɗan komai na abin da ya faru kafin zuwanka.

Allah Mai Rahama ne, kuma baya hukunta bawa sai da aikinsa. Idan iyayenka sun yi kuskure, ka bar shi a tsakaninsu da Allah – kai kuma ka gyara naka tafarkin."

Ka sani, Annabi Ibrahim (A.S.) ya ce: "Wanda ya halitta ni, kuma shi ne ke shiryar da ni." (Qur'ani 26:78)

Shi Allah ne ya ƙaddara zuwanka, kuma akwai wata hikima mai girma a cikin hakan. Kada ka ji ƙasƙanci, kada ka ji kuncin rai. Mutum mafi daraja a wajen Allah shi ne mai tsoronSa da aiki nagari — ba wanda aka haifa da aure ko ba tare da aure ba.

Ka dage ka ci gaba da zama na gari. ka tsayu cikin addu'a, ka yi ci gaba halin kirki. Ka zama misali ga duniya cewa Allah yana ɗaukaka bawa bisa kyakkyawan hali, ba bisa asalin haihuwarsa ba.

Idan duniya ta kallaka da ƙyama, ka sani Allah yana kallonka da rahama. Idan mutane sun rainaka, ka ɗaukaka kanka da ibada. Idan ka dage a kan gaskiya, ka fi dubban masu asali da nasaba – saboda nasaba mafi girma ita ce nasaba da Allah ka da wani raunan tunani ya sa ka fasa neman mahaifinka ka ci gaba da nemansa na tabbatar da cewa hakan zai kasance alkairine ba wa kai kadai bama harda shi da sauran al'umma."

Tana cikin maganar Zeeyter ta yi inviting su Khalil Da Deejerh.

Farouq ya ce,"Na yarda zan ci gaba da nemanshi amman dai yanzu ku amince mun in koma malaysia please,ba zan iya zama anan ba."

Khalil ne ya katse shi da fadin,".....

[17/06, 9:35 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs

- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!

*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-21

"Na riga na sa an yi rejecting ticket dinka yanzu So abun da ya fi shi ne kawai ka fito a asalin centuar dinka,ka fuskanci dukkkanin wani kalubale,ka ajiye rauninka na dan adam a gefe ka bayyanar da kwazo da jarumtarka,kar ka manta cewa ba asamun da ragwanci ko fidda tsamanin nasara ba,a ko ina muke kuma a kowani hali sannan a kowanni yanayi duk rintsi dadi da wuya muna nan daram ko da kuwa za ata jan mu ƙasa ne muna jin rauni hakan ba zai taɓa sanyawa mu nuna gazawarmu ba domin kuwa kowacce jarabawa da ubangiji zai mana muna daukanta matsayin haske ne ga rayuwarmu duka. "

Numfasawa Farouq ya yi yana ajiyar zuciya kafin ya ce,"Hakane kun tunatar dani abubuwa da yawa dana manta kasancewarmu tare babbar nasarace haɗakar ruhi mabambamta da suka sha gwagwarmayar rayuwa,zamu ci gaba,ba zamu taɓa fasawa ba har sai mun kai ga cin nasara." Ya karasa maganar yana sakin murmushi.

Zeeyter ta ce,"Ko kai fa, da har na fara tantamar cewa ko an canja muna kai ne in bazama nemo na asalin. "
Dariya suka yi duka kafin suka yi sallama.

Duk da cewa Farouq ba zai taɓa jin sanyi aransa kamar baya ba,amman tattaunawa da aminansa ya rage masa raɗaɗin da yake cikin zuciyarsa kashi saba'in cikin ɗari hakan yasa suna katse wayar ya tashi ya yi sallah raka'ah biyu ya nemi gafara wajen Ubangiji sannan ya roƙi nasara da kuma budewar hanya cikin gaggawa domin nemo mahaifinsa.

Javed dai ranar barci rabi da rabi ya yi gabadaya hankalinsa a tashe yake kan tafiyar Farouq hakan yasa asuba na yi kai tsaye ya kutsa dakin yana,"Oga zuwa karfe nawa zaka tafi kenan?" Jikinsa a sanyaye yake fadin hakan.
Farouq ya fito daga toilet kenan ga dukkan alamu alwala ya yi.
Farouq ya yi murmushi ya ce,"Na fasa In sha Allah sai an kammala komai kafin in tafi."
Tsabar farinciki Javed bai san lokacin da ya rungume Farouq ba yana,"Maah din ta ji sauki ko? Alhamdulillahi nikam ma in son ganinta kake asa tazo mana kawai."
"Umm kar ka damu yanzu dai muje sallah na ji ana shirin shiga." Farouq ya faɗa.

Mai Martaba ma daren ranar baiyi barci ba sunata faman bincike da tsubbuce-tsubbucensu. Cike da gajiyawa ya ce,"Cai ni fa na gaji,na fara karaya da lamarin nan,da gaske yaron nan yana so ya fi karfina, ban san me ya taka wanda ni ya gagareni ba."
Moli ya sheƙe da dariya kafin ya ce,"Oh ka dauka wasa ne da duk nake fada maka cewa za a sha wuya? Yanzu ai ka ga zahiri ko ni kaina na galabaita bare kai da kake bil adama haka ma yarana kaf sun fita a hayyacinsu har wa inda kasa sarki ya turo mana domin tallafawa sun gaji lamarin babu sauki sam kuma ga dukkan alamu in har muka ce zamu tsaurara za a samu matsala da har zata iya shafar rayuwarki."

Mai Martaba ya ce,"Wai wannan wane ne yake so ya ga bayana ne? Wane ne yake kokarin tona sirrinkan dana binne?"

Dago wani farin kyalle moli ya yi anyi rubutun ajami da jini a jiki yana,"Anyi nasarar samu wasu bayanan bayan shafi awanni ashirin da hudu muna fama." Ya karasa yana kyalkyalewa da dariya.

Da sauri Mai Martaba ya maida dubanshi ga Moli cikin zakuwa  ya ce,"Me aka samo? zamu iya koranshi dai ko?."

Moli ya daga kyallen ya sa shi cikin bakinsa hadiye yana wani irin tauna ya ce,"Wannan yaron jinin masarautar nan ne,kamar yadda jinin sarauta ke guduna a cikin jikinka haka shi ma ko ince ma nasa ya fi naka karfi domin bangarori biyune da shi,ba wanda ya isa ya koreshi a cikin gidan nan ko kasar nan ba zai taɓa yiwuwa ba domin jinin kasar ne kuma jinin gidan ne."

Cikin ruɗu Mai Martaba ya ce,"Ke nan Abdul-Rasheed na raye? Wannan yaronshi ne ko shi ne? Ke nan shi ya turo Ɗansa domin ya tona mun asiri? Yaushe ya yi aurenma? To ai baici ace ya haifi yaro kamar wannan ba bayan ɓatar da shi din da na yi, ko da ace yana Ɗa to ba dai wannan ba,to in ba haka ba ke nan shi ne ya dawo yaro? Ah ah."
Ya karasa maganar yana rike kansa da ya fara sara mishi yana juyawa.

Moli ya yi ihu kafin ya ce,"Duk bamu da amsar wa innan tambayoyin naka kuma ban ga kofar da zamu iya samo su ba,abu ɗaya ne bincike ya nuna cewa babu wanda ya isa ya fidda wannan yaron daga masarautar nan kuma hakan ma kasan sai da duk muka ki jiki mun kwana cur akan wannan yaron abun ma mamaki yake bani ta yadda yake da wannan power haka,ban taba samun bil adama haka ba,lallai na gasgata cewa akwai jinin sarauta mai karfi da ke guduna a jinin jikinsa yanzu sai dai muyi iya bakin kokarin mu wajen danne taurarinsa da kuzaharinsa yadda ba zai iya bamu kowacce matsala ba da zai daga ma hankali."

Mai Martaba ya ce,"Yawwa yawwa ni dai damuwata  a rufe bakinsa akaina kuma inma Abdul-Rasheed na raye a kara kaɗa hankalinsa ko da ma shi ya turo shi domin in ba hakan ba akwai matsala gaskiya akwai matsala."

Moli ya ce,"Kai dai kawai ka dage ka daure kuma ka ci gaba da zama kan tsarin da kake,mussamman batun sallar nan kar ka kuskura ka yi domin kana yi za a iya samun matsala sai dai ka ci gaba da yi kamar yadda kake ka je ka tsaya kamar kana yi amman baka komai."

"Yanzu ma na ji sun shiga,bara inyi sauri inje domin in ban fita ba za a iya zuwa nemana." Mai martaba ya fada yana saurin sanya rigarsa.

Take Moli da muƙarabbansa suka ɓace shi kuma ya fita masallaci.
An riga an tada ma kafin ya karasa haka yaje ya tsaya ba abun da yake illa ruku'u da sujjada in anyi ba tare da fadin komai ba.
Ana idar da sallar ya fito zai wuce ke nan suka haɗa ido da Farouq.
Ƙura masa idanu Farouq ya yi ido cikin ido yana yi masa kallon tuhuma.
Sai da jikin Mai Martaba ya amsa alamun rashin gaskiya ya bayyana a gareshi jiki na rawa ya yi saurin barin wajen.
A zuciyarsa yana saƙawa ,"Lallai ba makawa wannan yaron yasan wane ne ni,babu wanda ya taɓa yi mini kallon tuhuma irin haka sai shi amman ba komai koma miye saidai ya faru amman sai na rufe sirri na da kuma ganin bayan duk mai son tonawa,in aikin sihiri ya ƙi yiwuwa ai akwai na zahiri."
Ya faɗi hakan yana kai kawo.

Ya kasa zaune ya kasa tsaye yana ta saƙa da warwara.

♡♡♡
Farouq na zaune suna karyawa da Javed ya ce,"Oh Sorry ban faɗa maka ba gabadaya na sha afa SiftaCore fa sun ba mu date din ranar da zamu hadu dasu tun shekaran jiya suka kara yi mini Gmail kan cewa on 16th this month ka ga yau 15 gobe 16 kenan ya kamata yau ka tsaya tafiya Abujan gobe in Allah ya kaimu sai ka je ko."

Javed ya ce,"Ni kuma Oga? Aa kai dai ni ai kasan ban saba lamura da mutane haka ba kuma ma zai yiwuwa akwai tambayoyin da zasu ma ni ban sani ba."

Farouq ya ce,"Sai dai muje tare ai da hakan zaka koya gwanda ka saba."

Dariya Javed ya yi yana,"E na yarda muje taren dai in ba haka ba ai ni ba abun da zan iya tsinanawa."

Dariya duka suka yi.
Javed ya ce,"Ka ga ma bara inje in sanar da Mai Martaba tun yanzu kar azo asamu matsala."
Ya karasa maganar yana ajiye spoon kafin ya fice.

Yana zuwa ya sanar da Mai Martaba da mamakinsa Mai Martaba na jin cewa da Farouq za ayi tafiyan kuma da motar gida tuni ya amsa da furucin sai sun dawo abun yaso ya daurewa Javed kai saidai kuma farincikin hakan ya mantar da shi ya je ya sanar da Farouq kawai sannan suka wuce School.
Bayan sun dawo da dare suka kammala duk wani shirye-shiryensu na tafiya da duk wani document na su kafin suka kwanta da wuri kasancewar tafiyar safiya zasuyi.
Da wuri suka tashi suka shirya suka yiwa Hajiya Kaka da su Maah sallama kafin suka dauki hanya.
Suna cikin tafiya tsakiyan daji ya yi shiru motoci sun dauke sai su kaɗai lokaci guda suka wasu mutane sun zagayesu ta ko ina dauke da wuƙaƙe da bindiga.
Gabaɗayansu sun razana ban da salati babu abun da suke yi.

Fito da su daga cikin motar suka yi duka,a lokacin Farouq ya yi kokarin fara kai masu hari da duka.
Ganin da gaske Farouq na son fin karfinsu ya suɓuce masu hakan yasa wani cikinsu ya biga masa gefen bindiga akai.
Nan take ya fadi a wajen jini na zuba daga gefen kansa.
Shi kuwa Javed daman tun farkon faɗan aka turgudeshi ya sume.
Karasawa suka yi suna daga Farouq babu alamar numfashi a tattare da shi  ɗaya a cikin su ya ce,"wannan fa ya mutu kawai jan shi zamuyi muje mu sa shi cikin rafin cen."
Sun fara jan Farouq din kenan suka jiyo sautin karar motar jami'an tsaro da sauri suka.....
[18/06, 4:40 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-22

Suka fara kokarin tarwatsewa basu san ma lokacin da suka jefar da Farouq din gefe ba suna gudun ceton rai.
Sanya Farouq da Javed din suka yi a motarsu wani cikinsu kuma ya shiga motar su Farouq din zai tuka ya kaita Abuja, taimakon gaggawa suka fara basu kafin suka ci gaba da tafiya har suka isa cikin abujan kai tsaye asibiti suka nufa kafin su isa ma shi kam Javed har ya farfado dake masu yi masa wani duka lahani mai karfi ba,Farouq aka shiga da shi wajen likita shi ma din kuma cikin sa a duk da jinin da ke zuba daga kansa ana yi masa treating wajen ba jimawa ya farka yana salati.
Ganinshi da ya yi  a asibiti ya dawo masa da tunanin abun da ya faru.
Zai tashi da sauri Javed ya karasa yana,"Sannu Oga ka farka? Ya kan dai?"
Farouq ya ce,"Alhamdulillah, yanzu karfe nawa?"
Ya fada yana duba agogon hannunsa.
"Subhanallah ai yanzu ya kamata ace muna can wajen sune 3pm ya kamata mu hanzarta mu tafi."

Javed ya ce,"Haba dai Oga ai lafiya tafi komai da dai ka dakata tukunna sai mu basu report din matsalar da aka samu in munci sa'a ko zuwa gobe ne sai kara bamu lokaci. "

Farouq ya ce,"Aa ni bana jin komai daidai nake jin kaina muje kawai."
Ya tashi kenan sai ga Ɗaya cikin jami'an tsaron da suka kawosu ya shigo dakin yana.
"Ma Sha Allah Sannu da kokari."
Mika masa hannu Farouq ya yi yana,"Kune da kokari Godiya nake Sir don banyi tunanin kiran dana  muku ma ya tafi ba,mun gode sosai Allah saka da alkairi,yanzu nake so mu wuce gun kamfanin da muka zo daman."

Jami'in tsaron ya ce,"Alright Allah ya kara kiyayewa a dunga lura sosai." Ya karasa maganar yana bashi keyn motarsu.

Javed ne ya je ya biya kudin treatment din da akawa Farouq kafin suka bar asibitin.
Karfin hali Farouq yake yi kawai amman gabadaya jikinsa babu karfi.

Suna fita suka duba location din SiftaCore Technologies suka ga kuwa ashe babu wani tazara sosai tsakani da asibitin za a iya karasawa da kafa ma amman da yake suna da mota sai suka karasa cikin minti biyar.

Suna isa aka bude masu gate kasancewar an riga an san da zuwansu.
Daidai lokacin da suka yi parking motar adaidai lokacin C.E.O ya fita da kamfanin kuma.
Ciki suka shiga secretary ya hada su da manager sun tattauna sosai  sannan an nuna masu dukkanin computers din da aka tanadar masu dauka kawai zasu yi.
Farouq da Javed sunji matukar dadi da farinciki.

Ganin cewa sunyi yamma kuma basa son tafiyar dare zuwa mokwa saboda hanya hakan yasa suka bar computers din da nufin washegari zasu koma su karɓa sai su tafi da safe.

Hakan ne ya kasance suka yi sallama tukun suka je suka kama hotel sun kwana da safe misalin karfe goma suka koma.
Bayan sun gama da manager har Farouq ya shiga mota ya fito yana,"Sir in ba matsala ina so mu gaisa da C.E.O Please. "
Murmushi ya yi ya ce,"Alright ba matsala bara in masa magana ka zo muje. "
Tare suka je Farouq ya tsaya a kofar office din manager ya shiga ya yi ma ceo magana ya bashi izinin shigar Farouq kafin ya fito ya ce masa su shiga.
Da fara'a ceo ya karbi Farouq suka gaisa ya masa godiya sosai sannan ya nemi alfarmar da inda hali yazo masu cikin mokwa taron yaye ɗalibansu.
Shiru ya yi sai can kuma ya amsa da ,"Ba matsala In sha Allah zan duba indai akwai damar zuwan zamu zo ko ma bani ba manager zai zo."

Farouq ya ce,"Please Sir inda hali dai ku zo duk muna da bukatarku kasancewarku a wajen yana da matukar muhimmanci a garemu."

Murmushi ya yi ya ce,"Okay Za a duba In sha Allah. "
Suka yi sallama suka rungume juna kafin ya fita.

har cikin ransa ya ji mutumin ya birgesa mussamman da ya kasance babban mutum kuma masanin kwamfuta sannan uwa uba mai son mutane ga taimako.

Yana shiga mota yake shedawa Javed cewa ya nemi alfarma a wajen ceo domin zuwa wajen yaye dalibansu,ba karamin dadi da jin hakak Javed ya yi ba ya ji farinciki sosai.
Addua suka yi kafin suka hau hanya.
Dake Farouq sunyi magana da securities an sanya tsaro a hanya ba abun da ya faru  har suka isa cikin mokwa lafiya.

Suna isa kai tsaye School suka wuce,suka ajiye computers din sannan suka wuce gida,gabadaya sun gaji  suna shiga suka yi wanka sukai sallah sannan suka wuce part din

Hajiya Kaka domin Farouq ya ce ya yi kewarta kuma agunta yake so ya ci abinci.

Hajiya Kaka na ganinsu ta taɓe baki,"Ummm ai ni da so nake ma in turoma da takaddar saki hamsin da bakwai domin na lura baka auren."

Farouq ya karasa inda take yana kwantar da kansa a cinyar ta.
"Haba dai Amaryata ni na isa? Ai ban isa ba,ni da ke kinsan mutu ka raba takalmin kaza."

"Bawani nan mutu ka raba shine har zaka kwana kusan uku ne ma ko fi baka nemi ne ba yoo wannan ma ai a ƙa'ida ya ci araba auren ko kutu aka je."

Farouq ya ce,"Laifin Javed ne bai sanar da ke cewa bana da lafiya ba,har sai da BabanGanye ya dubani ya bani magani da sai dai kiji ance miki ki fara takaba kawai."

Hajiya Kaka na jin batun takaba da mutuwa ta marairaice.
"Ayyah ashe baka da lafiya shiyasa na dunga jini ba daidai ba,zuciyata na ta fadi mun Faruqu faruqu ashe ashe tana nufin baka da lafiya ne,ka san fa ni ko da Mai Martaba yake raye in bai da lafiya nima ciwon nake farawa,sannu ka ji ko batun takaba kam ai ba yanzu ba,fadamun me zaka ci? Me kakeso a kawo maka."

Farouq ya shagwaɓe,"wannan tuwon da ake miki mai dadin nan ni nake son ci."

Tuni Kaka ta kira mai aikinta tasa aka kawo masu tuwo shi kam Javed binsu da kallo kawai yake yana dariya.

Sai da suka gama ci suka sha hira akayi wasa da dariya da suka tafi sallar isha kafin suka wuce part dinsu.

Farouq na shiga dakinsa ya ga system dinsa na danger alamar an kara attacking dinsa.
Dauka ya yi yana fadin,"Yau kam koma waye ke wannan aikin sai na lalubo ba makawa."
Aiki ya shiga yi gadan gadan ya shiga nan ya fita nan.
Ya kira Zeeyter yana fada mata duk abun da ke faruwa ita ma ta dauko System dinta suna yi tare.
Dukufa details din mai yin hacking din kudin mutanen da suka fara magana da shi ya bata ta duba sai ta ga ai yana da alaka da mai bin diddigin sa dake gidan.
Har wajen karfe ɗaya na dare kafin suka fara samo  asalin location din.
Fita ya yi da system dinsa yana tafiya yana indicating har ya kai daidai wani daki a gidan wajen da ma bai taɓa shiga ba.
Daidai window din dakin ya tsaya dake wanda ake iya ja ne ya ja ya ɗaga a hankali,mace ya hango gaban system ta duƙufa tana dannawa......
[19/06, 5:46 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-23

Dagowar da zata yi suka suka haɗo da shi.
Suman tsaye ya yi yana mamaki.
Janinah ce,hannu yasa yana ƙara murza idanunsa.
Da gaske dai Janinah ce ba wata ba.
Jikinta ya bata ce ya gano ta hakan yasa ta zura masa ido kawai ba tare da ta ce komai ba.
Ya ce,"Zan iya  shigowa please?"
Girgiza masa kai ta yi alamar aa kafin ta ce,"Aa ka shigo ka dakeni."

"Ba zan miki komai ba,na yi alkawari, please  magana kawai za muyi." Farouq ya fada.
Kara girgiza kai ta yi ita dai bata yarda da shi ba.
Farouq ya ce,"Na rantse da Allah ba zan yi miki komai ba Janinah,da ace wani naniji na gani na yi mini wannan aikin tabbas sai inda karfina ya kare amman ke kam mamaki abun ma ya bani,ba zan miki komai ba magana za mu yi."
Ganin yadda yake magana yasata bude masa kofa ya zaga ya shiga.
Jikinta a sanyaye duk wannan tsiwar ta ta tayi sanyi kanta a ƙasa ta tsaya.
Karasawa gun system dinta ya yi kai tsaye.
Ita din ce kuwa ga dukka detail's din har ma ɗayan wanda yake chat da shi matsayin namijin nan.

Zama ya yi yana kallonta kafin ya ce,"Me yasa kike bibiyata?"

Kanta na kasa ta ce, " saboda kawai in bata ma dukkanin ayyukan da kake yi."

Farouq ya ce,"Me yasa kikeson bata mun ayyukan nawa?"

"Saboda ina jin haushinka,ka maraini ba wanda ya taɓa marina sai kai." Ta faɗa.

Farouq ya yi ajiyar zuciya.
"Yanzu daman duk kutsen da kikeso kimun ba ma damuwarki kwashe bayanaina bane,kawai damuwarki ki tarwatsa mun abubuwana kiji dadi kawai saboda na mareki?"

Ta girgiza kai.

Farouq ya ce,"Javed ya ce mun kinyi training din computer na yan watanni ban yi tunanin kina da kwarewa haka ba."

Shiru ta yi masa.
Farouq ya kara fadin,"ki sake jiki ki mun magana ba zan miki komai ba."

Janinah ta ce,"Bayan na gama na ci gaba da karatu online ne ba tare da sanin kowa ba ina yi ina bincike mussamman a bangaren Cybersecurity."

Farouq ya dauko System din nata ya zauna kusa da ita yana,"Shin a gidannan an san cewa kina charity? Kina diban kudin gwamnati kina yiwa al'umma hidima?"

Ta ce,"Aa babu wanda ya sani."

"To me yasa?"

Ta ce,"Saboda in an sani Mai Martaba zai iya hanani kuma bana bukatar asan ni wace ce,domin a zahiri kallon yarinya mara tarbiya ake yi mun hakan kuma baya damuna domin daga ni sai ubangiji ne suka san abun da ke raina da abun da nake aikatawa sai kuma kai da kasani yanzu,hatta wa inda nake aiki da su basu taba ganina  ko conference meeting za ayi  da rufaffiyar fuska nake zuwa masu kuma a matsayin namiji hakan kuma na yi ne domun rufe duk wata hanyar da zata nuna ni wace ce."

Da mamaki Farouq yake kallonta ,"Me yasa kika zabi wannan hanyar to domin taimakon al'umma?"

Janinah ta ce,"Saboda Al'ada ta rufe dukkanin wata kofar nasarar ga duk wata ya mace da ke rayuwa cikin wannan masarautar,na san cewa ba zan iya aikata komai da zahiri na ba hakan yasa na yi amfani da badini na domin aiwatar da muradaina cikin sauki,duk da cewa ba za su iya rayuwa a fili kamar yadda sauran mata ke samun wannan yancin ba ina jin dadin rayuwarsu a ɓoyen domin sun zam bango abin jinginar al'umma da dama wanda har ya kai ga a halin yanzu ina da gidan marayun da ni na gina kuma nake kula da dukkanin rayuwarsu kai ne na farko da ka sani kuma kai ma din don ban da yadda zanyi ne ka riga ka gano komai in da zaka bar mun dukkanin buruka su ci gaba da rayuwa a ɓoye da na ji dadi kuma na gode maka domin ana sani a masarautar nan kashina ya bushe kuma kofofin nasarata sun kulle kenan a kowacce hanya."

Farouq ya ce,"Ni in ban baki goyon baya ai bana nuƙusar da ke ba,kuma In sha Allah na miki alkawarin cewa zaki ci gaba da karatu ko a kasar nan ko ba a kasar nan sannan zaki fito a jarumar macenki ba tare da tsoro ko shakka ba,zaki zam yar al'ada da gargajiya mai capacity. "

Dariya Janinah ta fara tana,"Wayaga yar gargajiya mai capacity."

Farouq ya ce,"Eheen to yanzu me zan yi ki daina jin haushin nawa adaina bi mini diddigin system?"
Dariya ta kara yi tana,"An daina ai yanzu tunda asiri ya tonu."

Ya kalli agogon hannunsa yana,"Dare yyi past 3 bara in tafi kije ki kwanta zamu karasa magana gobe."

Janinah ta ce,"Ok Gudnight amman sai na yi sallah zan kwanta."

Farouq ya ce,"Hakan ya yi kyau nighty night. "
Ya fada yana fita a dakin ya kulle mata kofa.

Komawa dakinsa ya yi ya bawa Zeeyter labarin Janinah da komai ta yi mamaki matuka,suka tattauna kafin suka yi sallama,shi ma sallah ya yi tukun ya kwanta.

♡♡♡Yana tashi zaiyi sallar asuba ya yi gamo da laya a tsakiyan gadonsa.
Ganin bai san mene ne ba ya ajiye suna dawowa daga Sallah yake nunawa Javed.
Karba ya yi ,"Ikon Allah wannan ai Layar sihiri ce,a ina ka gani?"

Farouq ya ce,"Kan Gadona ina tashi na gani,Layar Sihiri kamar ya?"

Javed ya numfasa,"E abun ne da ake amfani da shi domin sihiri ko tsafi atakaice dai domin cutar da mutum."

Farouq ya karɓa yana dubawa gabadaya zagaye take da wasu irin rubutu da baza su iya karantuwa ba,murmushi ya yi ya tafi duniyar tunani.
Maganar Javed ce ta katse shi yana fadin,"Ni yanzu babbar damuwata kar ya kasance wannan layyar domin ka aka turota kuma ma in ya kasance ai ba wanda ka sani ko ya sanka da har zai nemi hanyar cutar da kai,abun nan akwai sarƙakiya inaga ya kamata mu kaiwa Mai Martaba a sanar da shi tun wuri adakatar da koma waye."
Ya karasa maganar yana kokarin karba agun Farouq.

Kautar da hannu Farouq ya yi yana,"Aa kar ka fadawa kowa please,babu wata matsala  kuma zata komawa duk wanda ya turota da kanta."

Javed ya ce,"Anya? Kar a samu matsala fa."

"Aa na ce ma karka damu ni dai kamun alfarma karka bari kowa ya ji." Yana faɗan hakan ya shige ɗaki.

Zuwa ya yi ya adana tukun ya ci gaba da sabgoginsa.

Sun je DigitalCraft sun gama lamuransu sannan suka koma gida,suna komawa Farouq zama ya

yi ya suka fara chatting da Janinah tana bashi hakuri kan abubuwan da ya faru tsakanin ita da shi.
Sun sha hira sosai kafin ya mata sallama kan zaiyi aiki.
Karfe Takwas da rabi ranar ya yi sallama da Javed ya shige daki acewarsa yana so ya kwanta da wuri domin zai tashi ya yi aiki.
Hakan ya kuwa kasance yana zuwa ya yi addu'a ya kwanta.
Sai karfe Biyu daidai ya farka yana tashi ya yi fara salatul tasbihi bayan ya idar ya roƙi Ubangiji da ya maidawa dukkanin mai binsa da sharri kansa,ya yi adduoi sosai ya yi karatu har sai da aka kira sallar asuba yana zaune kan sallaya.

♡♡♡Barci Mai Martaba ya ke yi cikin nishaɗi da kwanciyar hankali,tamkar a mafarki yaji saukar abu a goshinsa,zabura ya yi ya farka a firgice......

*SAI ANA MUN AFWA DA RASHIN TSAYIN PAGES AN KOMA SCHOOL YANZU LAMURAN SAI A HANKALI,ZAMU RARRAFA HAR A KAMMALA IN SHA ALLAH*
[21/06, 1:38 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials

- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!

*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-24

Yana kallon gabansa ya ci arba da wannan layar sahirin da ya turawa da Farouq,hakan yasa shi ƙara firgita yana ja da baya.
"Me wannan yaron yake nufi dani ne? Ya dawo mun da abuna? Ya dawo mun da shi? Wato ƙaiƙayi koma kan masheƙiya? Aa ba zai yiwu ba,sai ya koma dole ne,Moliiiiii."Ya faɗa da karfi yana dauko tulun ya bude.
Tuni Moli ya bayyana yana,"Wannan kiran fa tamkar ana kokarin zare mini rai?"
A fusace Mai Martaba ya ce,"Wannan fa? Kana gani ya dawo mun da abun da ka tura masa ka na gani? Me hakan yake nufi?"

Wani irin kallo ya bi Mai Martaba da shi sannan ya daga hannunsa wani haske ya janyo masa Layar sihirin zuwa hannunsa.
"Lallai wannan Yaron ya zarce tunanin duk mai tunani,har ya yi karfin da zan yi ajiya ya dawo da ita? Ba shakka yana ji da kanshi amman in yasan wata ai bai san wata ba."

Mai Martaba ya ce,"Ina layyar an andanata wajen da ba ma zai ganta bane to?"

"Kwarai kuwa,amman taurin kai da karfin da ke tattare da shi yasa layar ta gaza samun mafaka dole ta fito ya ganta kuma ya dawo mana da ita,kar ka damu wannan fadan yanzu ba naka kai kadai bane harda ni kuma zan dau mataki."

Farouq na tashi ya je ya duba inda ya ajiye layar bai gani ba.
"Alhamdulillahi ai babu abun da ya fi karfin Ubangiji. " ya furta yana sakin murmushi.

Wani irin shiri da shaƙuwa ne ya fara wanzuwa tsakanin Farouq da Janinah domin indai zai kasance a bangaren Hajiya Kaka to ita ma tana nan suna tare,har yana ƙara koya mata abubuwa da dama.
Tun Javed da su Hajiya na mamaki har sun daina sun zubawa sarautar Allah ido.
Kilishi kuwa da ta fahimta tuni hankalinta ya tashi ta fara nemo kofar da zata shiga ta fita tasan meke tsakanin Farouq da Janinah.

Zaune suke a falon Hajiya kaka su kadai Janinah da system dinta Farouq na mata bayani suna wani abu,a fusace Kilishi ta shiga Part din tana fadin,"Wai ke Janinah ba cewa na yi a kira mun ke ba? Kina nan kina shirme wani bare yafi danginki ko? Da ina jin labari ban gasgata ba ashe da gaske dai hakan na faruwa?"

Kallonta Janinah ta yi kafin ta ce,"Aa Aunty Kilishi zasu fita ne yana sauri shiyasa na tsaya ya karasa nuna mun abu sai in tawo,ki yi hakuri. "

Tsaki ta yi ta na karewa Farouq kallo sama da ƙasa kafin ta ce,"Wuce muje ki bar duk wani shirmen abu anan."
Zata kara magana Farouq ya dakatar da ita da fadin,"ki je da dare in mun dawo ma karasa."
Yana karasa fadin Hakan Javed na shigowa.
"Yane Oga kun kammala?"
Farouq ya ce,"Eh mu je."
Wani irin kallo Kilishi ta bishi da shi zata fita,shi kuwa ya sake mata murmushi.

Suna zuwa part dinta ta fara balbale Janinah da fada.
"Kin san dai wannan ba muharraminki bane ko da har kike shige masa,saboda kin ga Arham bai da rigima da tashin hankali yasa kike abun da ki ka ga dama ko? To in shi ya bar ki ni ba zan bari ba,ba zai taba saɓuwa ba domin ni ba zan jure hakan ba dole ki fita a harkar bakon ban daga yau yoo ma ban da rashin zuciya mutumin da ya wulakantakin yanzu zaki na kulawa ? Daga yau na hana na taka miki birki kar inji kar in kuma."

Janinah ta ce,"Shin lamuran gidan nan sunyi tsamarin da har sai an zaba min wanda zan kula? And batun Arham kuma na aure shi? Daga ke har shi baku da iko da ni a halin yanzu bare ma ko na aureshi shi ke da iko dani ba ke ba."

Tsayawa Kilishi tayi tana kallon Janinah.
"Iyee? Janinah ni kike faɗawa hakan? ni ce nake magana kike mai da mun da martani a yau? Kanwar
Mahaifinki kuma Mahaifiyar Mijin da zaki aura? Anya Wancen yaron bai yi miki wani abu ba kuwa?"

Janinah ta ce,"Ya mun me? An fada miki kowa irinki ne mai bakar zuciya? Kuma wallahi ba fashi sai na ci gaba da kulashi domin ina karuwa da kasancewa da shi fiye da ke da kike daurani a hanya mara kyau,sannan batun aure kuma bar ganin cewa Mai Martaba ya amince in na so babu musu zan iya kin auren Ɗan naki ba yadda aka iya dani."
Tana fadan hakan ta fice daga part din cikin sauri.

Cije yatsa Kilishi ta yi,"Lallai akwai matsala gagaruma,ba a banza na ji tsanar yaron nan,zai iya hure mata kunne ma ta ce shi take so,shi zata aura ban da matsala da Mai Martaba amman akwai bukatar in rufe kofar nan tun kafin ta bude tafi karfinmu dani fa shi."

Fita ta yi kai tsaye ta wuce Fadar Mai Martaba tana zuwa ta fashe masa da kuka gabansa kafin ta ce komai.

Umartan yan zaman fadar ya yi da su basu waje zasu tattauna.
Bayan sun fita ya ce,"Lafiya dai? Mene ne ke faruwa?"

Kilishi ta ce,"Ina so ayi auren Janinah da Arham yanzu ba sai an jira ya kammala karatun ba,domin na lura wancen bakon Javed din na daf da hure mata kunne na lura ma kamar soyayya suke."

Tana fada Mai Martaba ya maimaita cike da firgici,"Soyayya? Janinah da bako? Soyayya fa."

Kilishi ta ce,"Kwarai kuwa,domin dalilin hakan yasa yanzu ta gama mun rashin kunya ta ci mutuncina ta zageni ta fice abunta."

Mai Martaba ya ce,"Ah lallai abubuwan da yawa zaki ce mun,kin san cewa ban yarda da kasancewar bakon nan a gidan nan ba? Domin jikina na bani cewa shi din wani tsaiko ne da zai iya tona sirrinmu na shakarun da suka shuɗe kuma alamu ya nuna lallai shi jinin gidan nan ne abun da ya fi tada mun da hankali ma kenan."

Zare Ido Kilishi ta yi tana,"Jinin gidan nan? Sirrin masarauta? na Mai Martaba da Abdul-Rasheed tare?" Ta karasa maganar jiki a sanyaye zufa na keto mata.

Mai Martaba ya tashi yana kai da kawowa,"Kwarai kuwa,rabona da in samu barci cikin kwanciyar hankali tun ranar da yaron nan ya iso cikin gidan nan."

Kilishi ta ce,"Innalillahi wa inna illahir raji'un mun shiga uku,to ma shi din wane ne?"

"Har yanzu mun gagara sani anata faman bincike amman amsar dayace yana da matukar tsari da karfi  sannan jinin gidan ne kuma jinin sarautar da ke jikinsa ma duk tafi tamu karfi."

Kilishi ta ce,"Ya illahil Alamina Allah gamu gareki yanzu dai asamu ayi gaggawar auren nan kuma mu dukufa nemo hanyar da  zai gagara aikata komai garemu."

Mai Martaba ya ce,"Babu matsala batun aure kam, zan yi masa gargadi na zahiri ma ki zuba ido a daren yau daga shi har Janinan,amman kema kiyi naki kokarin abangarenki wajen ganin munci nasara."

Kilishi ta girgiza kai.
"In sha Allah daga yanzu ma kuwa ina fita daga nan."

Tana tafiya tana sakawa a zuciya,"Kenan dai wannan yaron yana son dakile shirina nima in ko hakan ne ba zan taɓa fari ya ci nasara ba,daukan mataki ya zam wajibi a gareni. "

♡♡♡♡Farouq sunata shirye-shiryensu na yaye dalibai

Javed kuwa soyayya ta yi zurfi tsakanin shi da Ameemah domin kullum suka tashi da kanshi yake kaita gida kafin ya dawo su tafi da Farouq.

Misalin Karfe takwas na dare Mai Martaba ya sanar da cewa yana bukatar kowa a babban falo kuma ya ce harda Farouq a wannan zaman.

Tunda Farouq ya ji ance harda jikinsa ya bashi cewa wannan zaman dominsa za ayi.
Suna zuwa kuwa kowa ya gama hallara saura su.
Neman waje suka yi suka zauna shi da Javed ana kallon kallon.....

[22/06, 5:39 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN KARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

Mai Martaba ya yi gyaran murya yana,"Fatan kowa na cikin lafiya,cikin aminci da kwanciyar hankali." Ya ɗan tsawaita kafin ya ci gaba da magana.
"Na san cewa ba lallai Al'adu,tarbiya da riƙon addininmu ya zama iri ɗaya dana yan ƙasar waje ba,domin yawancinsu da suke musulman suna amsa sunan kasancewa a addinin musulunci ne kawai wanda in an bibiya ko ibadar ba iyata suka yi ba bare aje ga sauran lamura don haka zan yi tunatarwa."
Nan ma ya ɗan yi shiru ka fin daga bisa ni ya ci gaba da magana wanda daman a ƙa'idarsa ba wanda ya isa ya tanka in yana magana har sai ya ƙare ko ya bada izinin yin hakan.

"Addininmu ya haramta kasancewar mace da namiji tare wa inda suke ba muharraman juna ba,wanda na ji labarin cewa wannan ƙwamacalar ta fara afkuwa a wannan masarautar tsakanin baƙon da ya zo daga kasar waje da Janinah,kila shi a gunsa hakan ba komai bane domin sun saba mafiyin hakan wanda sam mu kuma ba zamu dauka ba domin muna da riko da addini da kuma al'ada dakatar da hakan ya sanya ni yin wannan kiran da gaggawa,duk da cewa Janinah ta san haramcin hakan ta danne saninta don haka hukunci ba zai taɓa barinta ba har sai ladabtar da ita tunda tasan cewa akwai baiko akanta wanda ana daf da daura mata aure nan da wata guda sannan daga yau har ranar ɗaurin auren zata kasance a dakin ajiya na tsawon kwana wata guda ba tare da ta fito ko da farfajiya bane sai dai duk wani bukatunta ta yo su a ciki shi kuwa baƙo indai yana son ci gaba da kasancewa cikinmu ya zame masa wajabi da ya bi dokokinmu na addini da al'ada domin mu ba ma rayuwar yahudawa anan."

Kuka Janinah ta fara tana rungumar Mahaifiyarta.

Abba Malik ya ce,"Ayi hakuri Ranka Ya dade amman zan yi magana,Janinah ce 'Ya Mace ta farko a jikokin masarautar nan,ba laifi don an haneta ga kula wanda ba muharraminta ba,amman kuma batun auren nan yinsa ake kawai ba tare jin amincewarta ba sannan kuma kulleta a dakin ajiya ma sam ba mafita bane hakan tamkar danne hakki cikin hakkin ne,ina rokon alfarmar da abarta ta ci gaba da rayuwa yadda ta saba sannan batun aurenma abari ta gama samun fahimta da shi Arham din kafin ya kammala karatunsa ka da ya kasance cewa masarauta na kokarin danne hakkin 'Yara matan da ke cikinta kuma.....

Mai Martaba ne ya katse shi da fadin,"Wannan umarni ne ba shawara ba kuma dole ne abi ba tare kaucewa ko musawa ba daga yau Janinah zata fara rayuwa a dakin ajiya aure ma kuma babu fashi, a ko ina mace take cikin wannan masarautar bata da ikon kanta sannan baiwa ce ga mijin da zata aura domin karshen rayuwata zata kare ne cikin yiwa miji da yaran da zata haifa hidima."

Kuka Janinah take har tana shashsheƙa.

"In ni na zam Baiwa gareka da yaranka 'Yata ba za ta taɓa irin wannan rayuwa mara galihun

ba,Janinah zata auri Arham ne kawai in har zuciyarta ta amince da ta aure shi,auren so da ƙauna da kuma daraja juna,sannan batun ɗakin ajiya ma babu inda 'Yata zata domin ba laifin sata ko na zina aka kamata da yi ba."Mammah ta faɗa tana share hawayen da ke kwaranya a fuskar Janinah.

Gabadaya Falon shirun sa'o'i ya yi na mamaki tare da kasa gasgata cewa shin Mammah ce take magana ? Kuma cikin kakkauran lafuza haka?,shi kansa Mai Martaban kamewa ya yi domin a rayuwarshi da ita ko cikin idanunsa bata taɓa iya kallo ta yi masa magana bare kuma bijirewa umarninsa.

Kilishi ce ta katse shirun nasu da fadin,"Ah lallai Yiniyetsu kin samu sake,yaushe har kika samu yancin yin magana irin haka gaban Mai Martaba har ma da bijirewa umarninsa?"
Ta tsaya gaban Mammah tana nuna mata hannu.

Bige hannun nata Mammah ta yi tana,"A daidai lokacin da na ga ana kokarin dakilewa yata rayuwar 'Yanci daraja kima da mutuncinta na 'Ya mace."
Tana gama fadan hakan ta ja hannun Janinah suka fice a falon.

Murmushi Farouq ya yi ya tashi zai fita daidai setin mai martaba ya ce,"masu karya da addini sune asali da tushen yahudawa."
Yana fadin hakan ya fice.

Gabaɗaya kowa ya bar falon aka bar daga mai martaba sai kilishi da yake daman ba Hajiya Kaka a zaman.

Kilishi ta karasa gaban Mai Martaba tana fadin,"Lallai lamura sunyi sanyi na kara gasgata cewa akwai babban al'amarin da ke kokarin dumfaro mu,wai har Yiniyetsu ce ke iya jayayya da furuncinka kuma take musayan yawo dani? Matar da ko ni karan kaina bata taɓa tankamun ba bare kai. "

Shiru mai Martaba ya yi na tsawon lokaci kafin ya ce,"Ada ana yaƙin ne a ɓoye yanzu kuma na zahiri da zahiri za ayi sannan zan fara ne daga cikin gida,sai ta yi dana sanin fara yin fito na fito da hukuncina sannan shi ma wancen karamin mara kunyar yana daf da cin kashinsa."

Yana karasa fadin hakan ya  shige dakinsa.
Ita ma Kilishi a fusace ta yi bangarenta,kai tsaye dakin Arham ta yi,ya cire kaya yana sa na barci ke nan.

"Kai kam wani lokacin sai in dauka cewa tamkar bani na haifeka ba,ba don a cikin masarautar nan aka yi nakuda da haihuwar taka ba tabbas zan iya musawa,shin ke ko kishin mazan nan baka da shi? ban taba gani ka nuna damuwarka kan lallai sai ka auri Janinah ba, Anya ma kana son abun da nake so maka kuwa?"

Murmushi Ya yi kafin ya ce,"Mama Ina son Janinah amman soyayyar da nake yi mata ba ita zata sa inyi kokarin dakileta ko tauye mata hakki ba,a yau in Janinah ta ce bata sona wallahi Allah zan hakura da ita domin ni ba zan iya rayuwar jahilcin da ake yi a wannan masarautar ba,ana rayuwa da sunan bin addini da al'adar gargajiya amman  kuma tsantsar jahilci ake nunawa kuma.....

Kafin ya karasa ya ji saukar mari a fuskarsa.
Cikin fushi Kilishi ta ce,"Ka yi mini shiru, na ce ka yi mini shiru  kuma daga kai har Janinah ko kuna so ko kuna ƙi ya zama dole ku mallaki juna. " tana faɗa ta fice daga dakin tana ja mishi kofa da karfi cikin fushi.
[24/06, 4:40 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*

Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-26

Janinah suna shiga ɗaki da Mammah ta zaunar da ita gefen gado tana fadin,"Kar ki sa wata damuwa aranki,ba zan taɓa bari ki yi rayuwa irin tawa ba muddin ina raye ko da kuwa ace numfashi zai bar jinin jikina sai na tabbatar da cewa kin samu ingatacciyar rayuwa sannan ana girmama ra ayi da darajarki na mace a gidan aurenki,don haka ka da tursasa zuciyarki kan lallai sai ta so Arham in dai bakya son shi to na miki alkawarin cewa ba za ki taɓa aurenshi ba sannan Dakin ajiya ma ina kara jadadda miki cewa in dai zaki kasance a ciki to sai dai in har dani nima domin na yarda da cewa ba za ki taɓa aikata mummunan abun da suke son fara binki da shi ba  hatta a cikin littafi mai tsarki an bayyanar da daraja da kimar mace
Suratul Baqarah, Aya ta 187
Ubangiji yana fadin
"...Su mata sutura ce a gare ku, ku ma sutura ne a garesu.
Wanda hakan na nufi
Sutura a nan na nufin tufafi ko riga, wanda ke nuni da cewa:
Miji da mata suna kusa da juna kamar yadda tufafi ke kusa da jiki.
Suna kare juna daga sharri da cuta, kamar yadda tufafi ke kare mutum.
Suna lullube juna, suna ɓoye aibu da raunin juna.
Suna zama ƙawata da cika juna, kamar yadda tufafi ke ƙawata mutum.
Wannan ayar na nuna irin girmamawa, soyayya, kariya da haɗin kai da ya kamata ya kasance tsakanin ma'aurata. Musulunci ya ɗaga darajar aure da zaman gida, yana mai jaddada hakkoki

da nauyin juna a tsakanin miji da mata.
Musulunci ba ya nufin mace ta zam Baiwa ga mijinta haka kuma musulunci baya nufin a dunga tauye hakkin mace.

Da na yi aure ido a kulle amman yanzu tunda na fahimci darajar mace a musulunci ba zan taɓa bari kiyi rayuwa irin tawa ba lokaci ya kure gareni amman ke ba zai kure miki ba domin ko da ace kowa zai juya miki baya ni ina tare da ke,ki san kanki kuma ki so kanki kafin kowa hatta kasuwanci bai haramta ga 'Ya mace ba muddin za ta kiyaye dokokin da mutuncinta,ki sa aranki cewa zaki rayu irin rayuwar da kike so ne kawai Janinah ba wacce ake so kiyi ba."
Mammah ta karasa maganar tana rungumar Janinah.

Farouq da Javed kuwa tunda suka koma bangarensu harkar shirye-shiryen taronsu suka fara ba tare da sun ko daga maganar abun da ya faru a falon Mai Martaba ba domin kuwa washegari ne zai kasance ranar.

Hakan yasa gari na waye ma da sassafe suka bar gidan domin ganin komai ya gudana cikin tsari.
An fara taro,sun gayyaci manya sosai har sun cire tsammanin zuwa Ceo din SiftaCore Technologies kamar daga sama kuwa sai ga shi,shi da manager.
Javed ne ya je ya taresa da sauri ya ba shi wajen zama kasancewar Farouq na tare da mutane.
Ya yin da za abawa Dalibar da tafi kowa hazaƙa award Wacce ta kasance Ameemah ce Ceo aka kira domin ya damka mata.
Bayan ya bata aka bashi damar yin jawabin shawarwari da kwarin gwiwa ga daliban da aka yaye.
Da fara'arsa ya tsaya gabansu yana fadin,"Assalamu Alaikum warahmatullah,

Ina taya ku murna da kammala wannan muhimmin mataki na rayuwa akan na kammala samun horo a bangaren na'ura. Wannan ba ƙaramin nasara ba ce, kuma hakan yana nuna irin jajircewa da ƙwazonku wajen neman ilimi da ci gaban duniya ne gabadaya.

Na ji matukar dadi da farincikin kasancewar wannan makaranta domin 'Ya'Ya mata hakan ba karamin tallafawa zai yi wajen samun yin amfani da baiwar da kowacce a cikinku take da shi.

Ga wasu yan shawarwari gareku:

Kada kuce za ku tsaya anan – Ilimin kwamfuta yana iya canzawa kowace rana. Ku ci gaba da koyo, ku nemi takardun ƙwarewa (certifications) kamar CompTIA, Cisco (CCNA), Microsoft, Google, ko Adobe bisa ga fannin da kuka fi sha’awa,atakaice dai ina kara baku shawarar cewa ku kasance a kullum kuna bibiye da yanar gizo domin daukan darusa wannan tushe ne aka muku wanda kuma ina da yakin cewa tushe ne mai kyau da zaku iya amfani da shi wajen inganta rayuwarku da ma sauran al'ummar dake kewaye da ku.

Ku  Yi amfani da abinda kuka koya  Kada ku bar ilimin ku ya tsaya a takarda. Ku fara yin

practice sosai: Ku taimaka mutane ko kungiyoyi da basu da masaniya sosai akan kwamfuta. Haka zai ƙara ƙwarewar ku kuma ya buda muku ƙofofi.

Ku kasance masu kyawawan dabi'u domin kuwa Fasaha ba zata taimaka ba sai da ɗabi'a mai kyau: gaskiya, amana, da himma Jajircewa. Wadannan suna kara darajar ku fiye da takardar shaida.

Sannan Ku nemi abokan hulɗa masu amfani (networking)  Ku hada kai da sauran masu ilimi a fannin, ku shiga ƙungiyoyi ko online communities domin samun sabbin dabaru da damar aiki.

Ku yi aiki da niyyar taimakawa  Duk inda kuka samu dama, ku nuna ƙwarewarku ta hanyar taimakon jama'a, makarantu, ko ƙananan kasuwanni. Wannan na iya zama matakin farko zuwa ga kasuwanci ko guraben aiki.

A ƙarshe, ku kasance masu tawali'u da godiya. Ilimin da kuka samu wata kyauta ce daga Allah, don haka ku yi amfani da shi ta hanyar da zata kawo cigaba a rayuwar ku da al'umma baki ɗaya.

Ina rokon Allah Ya kara muku ilimi da basira, Ya buda muku ƙofofin nasara a fannoni daban-daban na rayuwa.

Allah ya albarkace ku da mu gabadaya.
Na gode."

Tafa masa suka shiga yi daga nan aka ci abinci an rabawa system dinta taro ya tashi cikin aminci.
Ceo zai tafi Farouq da Javed suka je masa sallama.
Yana miƙawa Farouq hannu su gaisa kai hannun da Farouq zai yi idanunsa suka sauka akan zoɓen da ke hannunsa,da sauri ya riƙe hannun yana taɓa zoben ya ce,"Zoben nan? Zoɓen Maah."
Cike da yanayin mamaki daga Ceo har javed suke kallon Farouq ya fara wani abu tamkar zautacce.
Dubawan da zaiyi kuwa suna ya ga an rubuta Mariam&A.
Dafe kai Farouq ya yi ganin cewa yana kokarin fita a hayyacinsa.
Ya ce,"Father....sai kuma ya yi shiru."
Ceo ya ce,"Father?" Cike da mamaki.

Durkusawa kasa Farouq ya yi ya daga hannunsa sama yana fadin,"Alhamdulillah,Alhamdulillah,Alhamdulillah. "

Ya dago ya kallishi kafin ya ce,"Mu koma daga ciki please."

Ceo ya ce,"Ciki? Me ya faru?"

Farouq ya ce," Please abu na ke so in nuna ma."

Shiga ciki suka yi duka suna mamakin sambatun da Farouq yake da kuma yanayinsa da ya canja daga ganin zobe kawai.
Hoton daidai zoben hannun Mammah ya ciro yana nuna masa wanda aka rubuta Abdul-Rasheed&M,Sake baki ceo ya yi ya kasa magana can ya ce,"Mariam?."

Ya fada yana kallon Farouq.
Farouq ya girgiza kai ,"Yeah ni din yaronta ne."

Ceo ya ce,"So you are my son?   Where's Mariam? Ina fatan tana raye."
Ya fada suna rugume juna.

Javed da Manager sai kallon kallo.
Farouq ya ce," Maah na lafiya kullum tana nan dauke da wannan zoben irin naka wanda shi ne ya tabbatar mun da cewa kaine mahaifina domin kuwa ta ce mun da kanku kuka je kukasa aka yi muku ku biyu sannan naka an rubuta  Mariam&A nata Abdul-Rasheed&M tana matukar kaunar zoben duk da cewa ka gujeta a lokacin da tafi bukatarka."

Numfashi Ceo ya ja kafin ya ce,"Ta ya zan guje bayan ni kaina ban san a wacce duniyar nake ba lokacin da muka rabu? Sannan daga baya na je har cen Netherlands din nemanku Iyayenta sun tabbatar mun da cewa su kansu basu san inda take wanda a lokacin na je daukanta ne mu tafi china tare,ba yadda na iya haka na tafi domin a lokacin zuciyata bata son ko da zance ne na nigeria bare tunanin dawowa a karshe bayan na samu abubuwan da nake bukata na fara jin sha'awar dawowa gida nigeria wanda hakan bai samu ba sai da na dage da adduoi kafin na samu ikon zuwa cikin garin nan kuwa kawai alkawarin da na yi ma ne ya  sa ni dauriyar zuwa dole amman jina nake kamar akan ƙaya ban da burin da zarce ace in ga na fita ,Yanzu ina mariam? A ina kake da zama? Kar dai ta dawo da ku nan? Kenan gidanmu sun karbeku?"

Ya jero masa wa innan tambayoyin.
Farouq ya ce,"Maah na Malaysia bayan ta koma Netherlands Iyayenta sunki karbanta karshe shine ta dawo malaysia har ta haifeni,bata san duk abun da ke faruwa da kai ba hasalima na dawo kasar nan ne domin nemanka wanda a yanzu ina zama ne  a gidanku amman babu wanda ya san ni wane ne."

Javed ya ce,"Oga ni fa ban gane wannan jawaban naku ba please ku fahimtar dani kaina ya fara daurewa na shiga ruɗani."

Farouq ya kalleshi ya ce,"Wannan mahaifina ne kuma shi din Yayane ga mahaifinka Mai Martaba ya bar gida tun yana da karancin shekaru,ba za ka gane komai a yanzu ba sai mun koma cen gida."

Javed na kallon Ceo sai a lokacin ya ga tsantsar kama tsakaninsa da Mai Martaba wanda abun da zai sa in ba an fada ba mutum ba zai gane bane shine banbancin yanayin shiga da kuma gyara domin kowa yaga ceo yasan cewa dan gyaye na karshe wanda hakan kan iya ɓoye shekarunsa tamkar saurayi.
Numfasawa ya yi domin ya ma rasa abun faɗa.

Ceo ya kalli Javed yana,"Ke nan wannan yaron Abdul-Raheem ne?"
Farouq ya girgiza masa kai.

"Ikon Allah, alamu ya nuna kasan abubuwa da dama har ma wa inda ni ban sani ba garin ya ya?" Ceo ya fada.

Farouq ya yi murmushi,"Baba Malam   Shi ya sanar da ni komai."

Bude Ido Ceo ya yi yana fadin,"Yana raye?"

Farouq ya ce,"Kwarai kuwa,kuma yanzu ma wajenshi zamuje domin Ka dawo gida kowa sai ya san da zamanka kuma sai na kwanta ma yanci da hakikinka."

Ceo ya ce,"Aa ba za ayi haka ba,Ni bana son tashin hankali kai ma barin gidan zaka yi,ba dai ni kazo nema ba? Ai gani nan ka sameni ko? To tafiya zamuyi. "

Farouq ya ce,"Ka yi mini alfarma matsayin Ɗanka kuma ka yi mini alkawari ba za ka ƙi aminta da duk abun da zance ba ina so ka yarda dani,duk abun da zanyi bana zalinci bane ko na cutar wani illa tsantsan gaskiya da adalci,sannan na tabbatar da cewa mahaifiyarka zata fi kowa farinciki da ganinka."

Har cikin ransa yana jin tsoron duk wani abu da zai haɗa shi da Abdul-Raheem to amman kuma yana matukar kaunar Hajiyansa sannan baya so ya yi abun da zai bakanta ran Ɗansa wanda ya fidda tsammani da kasancewa da shi,ba yadda ya iya haka ya amsa.

Kai tsaye wajen Baba Malam suka wuce,shi ko Mai Martaba tunda ya ga tarwatsewar tulunsa yasan cewa tabbas wani babban lamarin ya kara dumfaro shi.
A firgice ya tashi yana sambatu.
"Tabbas in dai Abdul-Rasheed ya shigo gidan nan an tabbatar mun da cewa dukkanin sihirin da na yi zai tarwatse,na shiga uku,shi ne? Yana rayen dai kenan? Aa." Ya tashi yana kai kawo.
Wata irin busa da ya jiyo anyi ne ya kara tarwatsa masa tunani a hanzarce ya fito tare da dukkanin mutanen gidan ana cincirindo.

Wata irin iska da guguwa ce suka fara tashi....
[26/06, 6:34 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhIT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON

ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-27

Suna zuwa daidai gidan Baba Malam suka tsai da motar,dake yana zaune akan tamburma ya shingiɗe da bango,idanunshi na kansu ganin suwaye haka.
fitowar da Abdul-Rasheed zaiyi kuwa mamaki ne ya kasa ɓoyuwa a fuskar Baba Malam,tashi ya yi yana fadin,"Abdul....Abdul..Rasheed ko...ko..dai...ida..nuna..ne." ya karasa faɗa yana ƙarasawa gareshi tare da shafa shi domin tabbatar.

"Babu shakka Mutum ne dai gabana ba Aljan ba." Ya furta.

Murmushi Ceo Abdul-Rasheed ya yi yana fadin,"Baba Malam ni ne,mu je mu zauna."
Ya faɗa yana rike masa hannu suka ƙarasa taburmar suka zauna duka.

"Lallai Ubangiji ba azzalimin bawanSa bane,ko da ban fidda yaƙinin cewa za a ganka ba,amman ban taɓa tunanin cewa zan ganka cikin aminci kamar haka ba, a zato da tunanina amman da ke Allah na tare da bayinsa ga ka a halin da ban taɓa hasashe ba."

"Ai kuwa wannan duk kudirace ta Ubangiji da karfin ikonsa tare da kariyar da yake bawa BayinSa." Ceo ya faɗa.

"Lallai kam ba bu shakka. "Ya tsagaita maganar yana kallon Farouq kafin ya ce,"Lallai ka cika Ɗa na haƙiƙa,ka cika Ɗan da duk wani uba zai yi alfahari da kai Maddalla da samun irinka."

Ceo ya ce,"Ya sheda mun cewa agunka ya samu dukkanin bayanan komai da komai nima banyi tunanin cewa zan riske ka araye ba ko dayake ma kwata-kwata araina kimanin shekarun da suka shuɗe ban taɓa jin sha'awar ko tunanin dawowa cikin garin Niger ba,amman da yake Allah ya riga ya tsara komai sai gashi na zo ta dalilin bikin yaye dalibai wanda kuma hakan shi ne silar bayyanar Umar a gareni."

Baba Malam ya ce,"Alhamdulillah Alhamdulillah ba abun da za mu ce da Allah sai godiya garesa,na tabbatar da cewa a yanzu bayyanarka ya amsa cikin garin niger da jahar mokwa da

kewayenta,kai tsaye yanzu abun da ya rage maka shine sanya kafafunka a cikin gidan mahaifinka."

Yana faɗan hakan Ceo ya ji gabansa ya yi wani irin mummunan faduwa.
Kallonsa Baba Malam ya yi ya ce,"Ka tsorata ko? Ka da ka damu kafarka na shiga cikin gidan dukkanin wani tsoro da firgici ya kare."
Tashi suka yi suka nufi gidan kaitsaye.

♡♡Dokunan da ke gidan Sarkin al'adu ne  suka fara tada wannan ƙurar,suna yin wata irin ƙara da kuka mai tada hankali, wanda ke kara tabbatar da faruwar wani babban al'amari,
ba su daina wannan kukan har sai da Yarima Abdul-Rasheed ya sanya kafafunsa a cikin gidan,tare suka yi shiru suka daina tsalle tsalle,sulalewa sukai suka zauna a ƙasa.

Shi kuwa Abdul-Rasheed a lokacin ya ji tamkar an zare masa ilahirin wani nauyi da ya dauka na tsawon shekaru a tsakiyan kansa,kwakwalwarsa da gangar jikinsa,wani irin karfi da jarumta ya ji yana riskarsa tare da duk wata izza da kamala ta jinin sarauta.

Gabadaya mutanen cikin gidan sun yi cincirindo a katafaren filin gidan cike da zaƙuwa tare da damuwar ganin lamarin da ke daf da afkuwa.

Bayyanar Yarima Abdul-Rasheed ne ya ƙara gigita Hajiya Kaka,Mai Martaba Abdul-Raheem,Abba Malik,da Kilishi.
Mussamman Hajiya Kaka ji ta yi kamar ana dawo mata da wasu lamura da suka faru a rayuwarta ta baya.
Muryarta na rawa jikinta na ruwa ta daga hannu tana nuna shi da fadin,"Ya....ri..ma."
Tana karasa faɗan hakan ta faɗi warwas a ƙasa sumammiya.
Da sauri Abdul-Rasheed ya ƙarasa gareta yana fadin,"Subhanallah Hajiya."
Dakatar da shi Mai Martaba ya yi yana fadin,"baka da izinin taɓata akan me ba mu san kai waye ba."
Kautar da Kai Yarima Rasheed ya yi yana faɗin,"In kai ba ka san ni wane ne ba,ita tasan ni wane ne."
Ya bangajesa yana daukanta sannan ya kalli Farouq yana,"Ku dauko mota akaita asibiti."
Abba Malik ma ya karasa hawaye na zuba a idanunsa ya kasa furta komai.
Kilishi kuwa sai kame-kame.

Mai Martaba ya ce,"Ba a zuwa asibiti a cikin gidan nan muna da masu lura da komai don haka ba mai fidda ta."
Ya karasa maganar yana umartar dokarai da kar su bar kowa ya fice daga Masarautar.

Yarima Rasheed zaiyi magana kenan Baba Malam girgiza masa kai yana fadin,"Aa kar ka damu a shiga da ita ciki nan dinma zata samu waraka In sha Allah. "

Hakan kuwa ya kasance,ana shiga da Hajiya Kaka ciki Mai Martaba ya kara umartar dakarai kan cewa a kara tsaurara tsaro kuma kar abar kowa ya fita sannan kar kowa ya fita kafin ya shige ciki shima.

BabanGanye da tawagarsa ne kan Hajiya Kaka.
Ya bata jikon magani cikin ikon Allah kuwa ta farka.
Tana farkawa ta fara kuka tana rungumar Yarima Rasheed "A kullum ina jinka araina amman na rasa dalilin kasa furta komai dangane da kai kuma ban da dukkanin amsoshin tarin tambayoyin da suke danƙare akaina ,na kan ji cewa tamkar wata rayuwace wacce na yi a cen wata duniyar ba wannan ba kuma innace zan zurfafa kan tunaninka na kan fita a hayyacina."

Rungumeta shi ma ya yi ya ce,"Na dawo gareki Hajiyata,In sha Allah daga yanzu ba za ki kara gagara samun sukuni akaina ba, haka kuma dukkanin wani shamaki da ke tsakaninmu ya kau har abada zamu ci gaba da rayuwa a tare kamar farko."

Jammal babban yayansu Javed ne ya ce,"Mu kam dai an bar mu cikin duhu,a fahimtar da mu meke faruwa Don Allah."
Dukka sauran ma suka girgiza kai alamar suma suna da bukata.

Kallon Baba Malam Yarima Rasheed ya yi ya ce,"Baba Malam wannan bayanin naka ne."

Idon Mai Martaba na kan Baba Malam ya kuresa.
Murmushi Baba Malam ya yi yana kawar da kansa kafin ya ce,"Wannan Wan Mahaifinku ne Abdul-Rasheed domin kuqa su yan biyune sun taso tare sannan wannan da kuke gani shi ne wanda akayiwa laƙabi da Yarima Rasheed tun yana yaro kasancewar an hasaso cewa shi ne mafi cancantar zamowa magajin sarkin al'adu ga kakanku Marigayi Mai Martaba sai dai kuma a lokacin da ya kamata ya hau karagar mulki adaidai lokacin lamura suka dunga tasowa marasa dadi wanda a karshe ma an nemesa an rasa kuma bakin kowa ya rufe babu wanda ke tunanin nemansa ko jin duniyar da yake sai yanzu da Ubangiji ya dawo da shi mu ka gan shi cikin wannan hali da yanayi mai ky....

Kafin ya karasa Mai Martaba ya katse shi da fadin,"Baka faɗa masu cewa Arniya baturiya ya bi ba domin babu wani batun ya ɓace,saboda soyayyar kafira arniya ya bar gidan iyayensa tubabbiya."
Yana wa innan maganganun wani zafi Farouq yake ji a cikin ransa zuciyarsa na bugawa da gudu gudu.

Yarima Rasheed da Baba Malam ne suka dakatar da shi da ido da hannunsu.
Sannan Yarima Rasheed ya ce,"Ai wa inda basu da addini ake kira da arna kafirai kuma suna nan a ko ina har ma anan sannan a wajen Ubangiji ba ruwanShi da wannan tubabbiyace ko an haifeta a musulunci zuciya da aiki kawai yake duba."

Cikin Daga murya ya ce,"Dakata,me ka sani a musuluncin? Har kai kanka yanzu kana kallon

kanka a musulmi ne a yadda kake? Ni ina tantama ma da kyar in ba tajaka kun kafirci duka ba.......
[28/06, 1:55 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhIT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT

INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-28
domin ko a yanayin shigar ma kadai ya isa ya bayyanar da cewa ka jime da ficewa daga cikin addininka tunda daman cen ba so kake ba ."

Tsilif cikin bacin rai Farouq ya zo ya tsaya gaban Mai Martaba yana nuna ma shi yatsa,"Shin an ce maka addinin musuluncin ta shiga ake gane haƙiƙaninsa? na ba zan yi mamakin jin hakan ba domin yau na ƙara tabbatar da cewa kai ɗin kasurgumin jahi....
Kafin Farouq ya ƙarasa Yan fada suka dakatar da shi suna riƙeshi da fadin,"Ahir dinka,Mai Martaba ba tsaran ubanka ba ne bare kai,hattara dai."
Bige su Farouq ya yi ya zame jikinsa,za su yi kokarin ƙara rike shi Mai Martaba ya dakatar da su,"Ka da ku damu da wannan rainon kasar waje irin ta tsagera ne."
Ya kalli Farouq din shi ma yana nuna masa hannu,"Ina umartarka da ka fita a cikin lamuran dangina,na yi maka duk wani kashedi da ya kamata amman tamkar ana ƙara maka karfi? To a yau za ayi na karshe,ka fice ka bar gidan nan da kafafunka ko kuwa in sanya a fiddaka."

Murmushi Yarima Rasheed ya yi ya tsaya gaban Farouq yana faɗin,"Shi ba bare bane,sannan ba zai taɓa barin gidan nan ba muddin ina cikinsa domin shi ɗin mallakina ne,Ɗana ne."

Kallon kallo aka fara yi.
Da sauri Abba Malik ya je ya rike hannun Farouq yana faɗin,"Ɗanka ? Ɗanka ne? Babu shakka ranar da na fara ganin yaron nan jikina ya bani cewa shi din jinina ne,wani gurbi ne a garemu." Yana ƙarasa fadan hakan ya rungume Farouq.

Hajiya Kaka ta ce,"Yarima, Umar Ɗanka ne?"
Girgiza mata kai ya yi yana faɗin,"Kwarai Hajiya jikanki ne."

Miƙawa Farouq hannu Hajiya Kaka ta yi ya ƙarasa ita ma ta rungumeshi,Maganar Mai Martaba ce ta Dakatar da su da fadin,"Duk wannan shirine,Karya ne,ya je ya samo Ɗa ne kawai a kasar waje ya turo mana shi domin leƙen asiri daga karshe ya zo ya ce Ɗansa ne da tunanin cewa zasu ƙwaci sarauta da dukiya kuma mijin kafira ba zai taɓa jan ragamar sarautar Gidan Al'adun

Mokwa ba."

Murmushin takaici Farouq ya yi ya ce,"Kai Sarauta da dukiya ta dama,kuma batun da kake ta yi na danganta Mahaifiyata da Kafirci ya isheka,domin babu kafiri sai mai mai dangata musulmai da kafirci,Na lura da cewa shekara da shekaru kana nan kafe kan bakar dabi'arka na tsangwama,kyara da tozarci ga tubabbu babu haufi kuma bana tantama a yanzu Ilimin addini da kare hakkokinsa da mahaifinka take da shi sam baka da makamancinsa,Ubangiji da kanSa ya furta cewa"وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ حَقًّا ۚ لَّهُم مَّغْفِرَةٌ وَرِزْقٌ كَرِيمٌ"
Waɗanda suka yi imani kuma suka yi Hijira suka yi jihadi a kan hanyar Allah, da kuma waɗanda suka karɓi baƙuncinsu suka yi taimako waɗannan su ne haƙiƙanin muminai, suna da alƙawarin gafara da kuma arziƙi mai girma."
Shin kai kana ɗaya daga sahunsu?
Kwatanta wa inda suka kasance akasin masu karɓar baƙuncinsu mene ne makomarsu?
Haka Ubangiji ya ƙara fadin"
وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۢ بَعْدُ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ مَعَكُمْ فَأُوْلَٰٓئِكَ مِنكُمْ ۚ وَأُوْلُواْ ٱلْأَرْحَامِ بَعْضُهُمْ أَوْلَىٰ بِبَعْضٍ فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمٌ
Kuma waɗanda suka yi imani bayan haka (Hijira) kuma suka yi Hijira kuma suka jihadi tare da ku waɗannan suna cikin ku. Kuma ma'abota zumunta ('yan'uwa na jini) su ne suka fi cancantar gadon junansu a cikin littafin Allah. Allah Masani ne ga dukkan komai."

Bara in tambayeka ma akwai wasu ayoyin muminai da Ubangiji ya kawo cikin Littafi mai tsarki ka san me suke faɗa?
Faɗa mana tunda dai kana jin kanka a matsayin wanda ya fi kowa sanin addinin musulunci."

Gajeran tsaki Mai Martaba ya yi yana fadīn,"Mamaki nake,kai din har waye a musulunci za kana tunanin akwai abun da ka fini sani,babu shakka muminai uku su ne, masu zalintar kansu,masu matsakaita,masu yin kyawawan ayyuka."

Murmushi Farouq ya yi kafin ya ce,"Ko wannan jawaban naka kadai sun isa su ƙara tabbatar da cewa babu abun da ka sani dangane da musulunci domin kuwa a cikin ayoyin Allah Ya kasa muminai kashi uku:

Kashi na farko: Su ne waɗanda suka yi imani a karon farko tun Manzon Allah yana Makkah, kuma suka yi Hijira tare da shi zuwa Madina, suka halarci yaƙe-yaƙe kamar Badr da Uhud da sauransu.

Kashi Na biyu: Su ne Ansaru waɗanda suka yi imani bayan kuma suka karɓi baƙuncin Manzon Allah Sallallahu Alaihi Wa Sallam tare da Muhajirai kuma suka taimake su, dukkanin waɗannan Allah Ya tabbatar musu da haƙiƙanin imani, sannan ya yi musu alƙawarin gafara na duk abin da suka kasance a kan shi kafin imani, da kuma arziƙi mai girma da yake jiransu.

Kashi na uku:
Su ne waɗanda suka yi imani daga baya, daga cikin mutanen Makkah, waɗanda suka musulunta bayan Manzon Allah Ya yi hijira kuma suka yi hijira suka bi shi suka yi jihadi tare da

shi, to su ma Allah Ya tabbatar da cewa suna cikin muminai, kuma za su samu abin da suka samu na gafara.

Shin ko anan ka ƙara tabbatar da kima da darajar gami da alfarmar da Ubangiji ya bawa Tubabbu wanda wa inda aka haifa cikin musuluncinma basa da shi?
Ba ma nan ba hatta hadisai Manzon Allah ya faɗi,"

1. عن عمرو بن العاص رضي الله عنه قال:
قال رسول الله ﷺ:
"الإسلام يهدم ما كان قبله، والهجرة تهدم ما كان قبلها، والحج يهدم ما كان قبله."

رواه مسلم (121)

Ma'ana: Musulunci yana shafe dukkan abin da ya gabata (na zunubi), Hijira tana gogewa, Hajj ma haka.

Ma'ana duk abin da mutum ya aikata na zunubi daga ranar da ya musulunta duk an shafe zunubansa ya dawo tamkar jariri sabuwar haihuwa.

Ka ga wannan ma wata falala ce da wanda aka haifa cikin musulunci ba shi da ita. "
Haka kuma ya ƙara da fadin,"

2. عن أبي هريرة رضي الله عنه قال:
قال رسول الله ﷺ:
"من أسلم من أهل الجاهلية ثم حسن إسلامه، لم يؤاخذ بما عمل في الجاهلية، ومن عاد في الجاهلية أُخذ بالأول والآخر."

رواه البخاري (6924) ومسلم (120)

Ma'ana: Wanda ya musulunta daga jahiliyya, kuma ya kyautata Musuluncinsa , ba za a hukunta shi da abin da ya aikata a baya ba.

Sannan

3. عن أبي هريرة رضي الله عنه قال:
قال رسول الله ﷺ:
"الناس معادن كمعادن الذهب والفضة، خيارهم في الجاهلية خيارهم في الإسلام إذا فقهوا."
رواه مسلم (2638)

Ma'ana: Mutane kamar ma'adanai ne — kamar zinariya da azurfa. Zaɓaɓɓunsu a jahiliyya, su ne zaɓaɓɓunsu a Musulunci — idan sun samu fahimta.
Ina fatan cewa ka fahimci cewa tubabbu ba sa daga cikin makaskanta a wajen Ubangiji kuma duk wanda ya ƙarbi baƙuncinsu yana da alfarma mai girma wajen Ubangiji saɓanin wanda ya yi

kokarin hura masu wutar komawa cikin duhun da suka tsira daga shi.
Ka yiwa kanka adalci ka fito daga rayuwar duhun da kake ciki domin a halin yanzu kai ne babban kafiri na hakik.....

Kafin ya karasa Mai Martaba ya yi wata kara yan umartar Dakaranshi da su kama Farouq su kai shi daƙin duhu.
"Za ka san wa ka kira da kafiri,za ka yi danasin kasancewar ka a duniyar nan ma gabadaya ba kasar nan ba kuma zaka fadamun kai waye."

Yarima Rasheed ya karasa yana fadin,"Ba wanda ya isa ya hukunta shi don ya fadi gaskiyar kuma kowanni Ɗa ba zai taɓa zuba idanu ana ciwa iyayensa mutunci ba."

Mai Martaba ya ce,"Ni ke da iko a wannan masarautar kowa na ciki wanda zai shigo da zai fita karkashina yake,don haka ba wanda ya isa ya ja dani."

Yarima Rasheed ya daga hannu zai kaiwa Mai Martaba mari Baba Malam ya dakatar da shi da fadin,"Aa a yanzu shi ke da karfin iko ka da ka jawa kanka matsala."

Wani irin kafirin Murmushi Mai Martaba ya yi yana fadin,"Ai da ka barshi, da ka barshi yau da zaiyi bankwana da hannunshi."
Ya kalli Dakaran cikin dagun murya ya ce ,"Ku Dauke shi....
[01/07, 7:20 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace

- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-29

Haka suka cinciɓi Farouq tamkar wani daurin kaya,kai tsaye basu direshi a ko ina ba sai ɗakin duhu,daƙin da ya kasance babu ko hanya bare alamun haske;babu abun da mutum yake iya hanga sai dai duhu,buɗe ido da akasinsa duk ɗaya a wannan daƙin.

Bayan sun shigar da shi Hajiya Kaka ta kalli Mai Martaba ta ce,"Kar ka manta fa wannan Yaron jinin kane,bai kamata ka aikata hakan ba."

"Ba jinina bane,domin ni ba zan haɗa jini da Kafirai ba,sannan in an bibiyama a yawon banzansu aka samo shi."

Mai Martaba na faɗan hakan ya yi tafiyarsa.

Yarima Rasheed ya rike Hannun Hajiya Kaka kafin ya ce,"Kar ki damu Hajiya,ka da duk abun da zai yi ya dameki domin ya aikata mafiyin hakan ma sannan na tabbatar da cewa bai isa ya yiwa Farouq komai ba,duk abun da ya sameshi to sai dai in har ubangiji ne ya kudurta hakan."

Tsaki Kilishi ta yi ta ce,"Wa inda suke cikin addini na gaskiya kuma suke bin Ubangiji sune kadai Ubangiji ya ke karesu amman wa inda suka dau wata hanyar daban kam ai sai kallo,ba su ma fara ganin komai ba."

Wani irin mummunan kallo Abba Malik ya bita da shi yana fadin,"Ki san me zaina fitowa daga bakinki domin ba da sa'o'inki kike ba."

Binsa da kallo ita ma tayi sama da ƙasa kafin ta ce,"Ina ji da kaina fiye da yadda kake ji da kanka kuma da sannu zaka zam bawana anan zan ga ko akwai batun sa'anni."
Tana fadan hakan ita ma ta fice kai tsaye ta yi bangarenta.

Gabadaya ficewa suka yi jiki a sanyaye Janinah kuwa mai za ta yi ban da kuka,da gudu ta karasa jikin Hajiya Kaka ta rungumeta tana,"Yah Farouq,mutuwa ake a dakin nan Hajiya Kaka kisa a fito da shi,in ba haka ba wallahi mutuwa zaiyi,zai mutu."
Shafa bayanta Hajiya Kaka ta yi kafin ta ce mata,"Ba zai mutu ba In sha Allah Janinah ki yi haƙuri. "

***Mai Martaba na shiga Part dinnan ya kira dakarai ya kara sheda masu cewa a sanya tsaro a dakin duhun nan sannan ka da a bashi abinci ko da kuwa ruwa ne,duk wani guri da zai iya samun sassauci ko na yin numfashine a ƙara rufewa domin yana so nan da kwana biyu zuwa uku kawai ace ya mutu ne a cikin dakin yadda babu mai tuhumarsa sai dai ayi hakuri don dole.

Daga nan suna tafiya kuma ya kira Moli,a tattaunawarsu Moli ke sheda masa cewa ashe lokacin da  Mariam ta zo Nigeria ma tana dauke da cikin Farouq domin ba ta hanyar aure aka sameshi ba sannan kuma Yarima Rasheed bai aureta ba har rana ita yau,hasali ma rabonsu da ganin juna tun ranar da ta bar nigeria.
Ya kara da cewa,"Na sha wuya matuka kafin na samo wa innan bayanan suma din sai da na hada da aiki da Jinnun wajen Baba Malam,ka san su da taurin kai iya abun da na samu ke nan."

Kai da kawowa Mai Martaba ya fara yi kafin ya fara wata irin dariyar mugunta,"Oh ya tabbata dai yaron ma Ɗan shege ne,ba a haifesa da aure ba amman har yake so ya yi takara dani,oh ta zo ma gidan sauki ai kenan wannan mummunan fanten da ke kewaye da shi ma ai kadai ya isa ya hana shi samun sarauta wannan ko da ma na barshi a raye ai rayuwarshi bata da wani cikakken amfani Ɗan Shege har ya shiga gonata?"
Ya ci gaba da kyalkyale dariya.

Moli ne ya dakatar da shi yana,"Amman akwai matsala fa,akwai alamun allura na daf da tono

garma."

Take ya dakata da dariyar cikin damuwa ya ce,"Aa! allurar nan ba zata taɓa iya tono wannan garmar ba, domin kuwa ramin da na binne mai zurfe ne kuma garmar tana da matukar kwari."

Jan Numfashi Moli ya yi kafin ya ce,"Hmm ina tabbatar maka da cewa ka yi kokarin kara rufe wannan garmar da kyau."

Mai Martaba ya ce,"Na fahimci inda ka dosa,babu wannan matsalar shikenan na san me zan yi."

Yarima Rasheed kuwa tunda suka bar Dakin Hajiya Kaka suna tare da Baba Malam,da Abba Malik har ma da Javed domin hankalin Javed ya matukar tashi,shi babbar damuwarsa a san yadda za ayi a fito da Farouq.
Suna ta tattaunawa,Yarima Rasheed ne ya dunga rarrashinsa kan cewa duk abun da ya faru Ubangiji ne ya kudurta kuma hakan ne daidai.
Da haka suka rabu kowa ya je ya kwanta,Asalin Part din Yarima Rasheed da ke kulle Abba Malik yasa aka bude masa suka shiga da ke ana yawan gyarawa babu datti baki anan suke sauka.

Shi kuwa Farouq tunda aka sanya shi cikin dakin ban da adduoi babu abun da yake karantawa hakan yasa tun yana jin firgici da tsaro har ya samu nutsuwa.
Sai a lokacin ya tuna da cewa rabonsa da abinci tun safe,hanjin cikinsa suka fara cakudewa,suna har gitsewa tare da karo da juna.
Har dare ya yi bai ma sani ba,kuma ya kasa ko da runtsa ido ne tsabar yunwa.
Tsakiyan dare wajen karfe biyu ya jiyo sautin murya na masa magana.
"Yaah Farouq,ga abinci,ka karba ka ci." Daga jin muryar za ka fahimci cewa mai maganar ta sha kuka kuma tana cikin yanayi na matukar damuwa.
Mamaki abun ya basa ya ce,"Janinah, ke ce?"
Cikin muryar kuka ta ce,"Eh."
Haske ta kunna tana miƙa masa dake ta saman ginin ta haura ta fasa wani ɓari.
Yana karɓa ta ji sautin takun mutane an fito da gudu ana kunna haske.
"Zai gudu......
[05/07, 8:37 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI

SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-30

Mannewa ta yi ta cikin wani lungu ta ɓuya,su ka gama haske-haskensu ba su ganta ba,hakan yasa suka leƙa dakin  suka hango shi zaune idanunshi a rufe,hakan yasa su ajiyar zuciya,Ɗaya cikinsu ya ce,"Kila ma Mage ce ta wuce muka zata mutum ne."
"Da alama kam." Suka amsa da hakan kafin kowannensu ya ci gaba da tsayuwa inda yake,daman barci ne ya ɗan kwashesu.

☆☆☆Gari ya waye
Misalin karfe Goma Yarima Rasheed ya fito daga bangarensa cikin shigar sarauta,kai tsaye wajen Hajiya Kaka ya fara nuna ya gaidata tasa mi shi albarka kafin ya nufi fadar Mai Martaba,Yana shiga ganinsa cikin yanayi na shigar sarauta ya firgita Mai Martaba ba tare da ya ankare ba ya tashi yana sakin baki.
Murmushi Yarima Rasheed ya yi ya ce,"Ka yi mamaki ko? Kadan ma ka gani,na zo in jadadda maka cewa yadda kake da karfin iko a gidan nan haka nima nake da shi duk da cewa a yanzu ka fini amman da sannu za ka dawo tafi kafafuna,kar ka damu batun tsare Ɗana da ka yi ba zan ja da kai ba,domin ko ba komai kana matsayin uba ne gareshi sannan kuma shugabansa a wannan masarauta,abun da nake so ka sani shine iko,mulki,izza da duk wasu dokokinka ba za su taɓa aiki ko tasiri akaina ba,inma ka manta yanzu ka tuna ko da ace bani bane mafi cancantar zamtowa Sarkin Al'adu to matsayin Ɗan Sarkin da nake ba za ka iya kawarwa ba,bare ma dukka biyun suna nan kuma sun dawo."

Kasa furta komai Mai Martaba ya yi,shi ko Yareema Rasheed ya na gama faɗan abun da ke ransa ya fice daga cikin fadar,Baba Malam da Manager suka bi biyansa,dukkanin Hadimai da ma'aikata gidan suna ganinsa suka fara cincirindon durkusawa suna miƙa masa gaisuwa,bakin gate kuwa tun kafin su ƙarasa aka yi gaggawar buɗewa ana rusuna masa.
Har suka shiga mota suka fice daga gidan.

Kai tsaye gidan Hakimin Mokwa suka je wato mai wakiltar Sarkin Bida.
Sun yi gaisuwar mutunci,Baba Malam ya gabatar da Yarima Rasheed gareshi,ya ji dadin ganinsa matuka kafin daga bisa suka wuce Bida.
Dake tun daren jiya Yarima Rasheed ya shirya zama da Sarkin ta hanyar tura masa saƙo kuma ya aminta kasancewar daman yana yawan tura kayan tallafi ga mabuƙata zuwa ga fadar,shiyasa ko da ya nemi ganin Sarki bai samu tsaiko ba.

Suna tafiya suna hira,motarsu na shiga cikin garin Bida Yarima Rasheed ya tamkar an caka masa wani abu a tsakiyar kansa,wata irin ƙara ya sake yana dafa kansa can kuma sai ya fara karanto,"Innalillahi wa inna illahir raji'un,Hasbunallahu wa ni'imal wakil."
Tsaida motar suka yi gefe duka suna tambayar ko lafiya ganin yadda lokaci guda jikinsa ya dau

zafi ga kuma wata irin zufa da ke keto masa.

Manager ya ce,"Sir ko dai za mu nemi asibiti mafi kusa ne?"

Girgiza masa kai ya yi alamar aa ya ci gaba da Adduoinsa can kuwa ya ji ya dawo daidai kafin ya ce,"Mu tafi ba komai In sha Allah. "

Baba Malam kallonsa kawai ya yi yana murmushi ba tare da ya ce komai ba.

Masarautar suka nufa
Sai da aka kaisu wani ɗaki suka huta,suka ci abinci suka yi sallah kafin aka kai su Fadar Mai Martaba.
Suna shiga idanun Mai Martaba akan Yarima Rasheed,Murmushi ya yi ya miƙa masa hannu yana su gaisa yana faɗin,"Yarima Rasheed."
Girgiza kai Yarima Rasheed ya yi cikin yanayin mamaki ya ce,"Ka sanni kenan? Kai ba ka manta dani ba Yallaɓai?."
Murmushi ya yi kara yi kafin ya ce,"Ko da ace za a iya yiwa kowa na garin niger katanga da wasu lamura ai ban jin cewa za a iya yi mun,ina yaronka? fatan yana lafiya?"

Nan fa Yarima Rasheed ya ƙara rikicewa.
."Shi ma ka san shi ke nan? to taya?" Ya karasa maganar yana kallon Baba Malam.

Baba Malam ya ce,"Ka kwantar da hankalinka kamar ka manta gabanwa kake zaune? Sarkin Bida ne ai babu wani abu daga gareshi na mamaki domin karfin ikonsa ya zarce tunanin dukkanin mai tunani. "

Mai martaba ya yi murmushi kafin ya ce,"Na san Farouq Ɗanka ne,kuma na jima da zaman jiran zuwansa domin shi ne kadai zai iya saita Sarautar gidan Al'adun mokwa ta dawo kan tsari,aranar da na fara ganinshi aka tabbatar mun da cewa shine hakan yasa na dauki rawani da ya kasance sak wanda mahaifinka ke sanya ma na ba shi,afakaice saƙo ne na bayar da ɗan uwanka domin ya gyara zama kan cewa zalincinsa ya kusa zuwa karshe."

Yarima Rasheed ya ce,"Ka san da cewa Abdul-Raheem shi ne ya kashe mahaifinmu mai martaba?"

Gyara zama ya yi kafin  ya ce,"Babu shakka na sani."

"To amman ka yi shiru kuma?"
Yarima Rasheed ya faɗa.

"Ban da iko da karfin fitowa kai tsaye da batun duk da cewa zan iya daukan mataki da kaina,amman aa,na tabbatar da cewa akwai wannan ranar kuma ita nake ta jira, Yaronka ya fi

mu dukka wannan karfin."
Mai Martaba ya faɗa.

Yarima Rasheed ya ce,"To amman kuma yanzu yana nan a kulle ya kulle shi a dakin duhu."

Mai Martaba ya girgiza kai,"Ba zai iya yi mishi komai ba,kasancewarsa a dakin duhu ko fitarsa ba zai ragesa da komai ba sai dai ma ya kara fahimtar rayuwa da karfin iko, kuma zai fito cikin lafiya In sha Allah."

Yarima Rasheed ya ce,"Allah yasa mu dace."

"Ameen,amman ni na jima da gano dacewarma,yanzu kawai ku koma sannan ku tanadi duk wata hujja da kuke da ita,sannan kar ku bari ya fahimci komai a kowanni lokaci zan iya zuwa daga yau zan shirya fara shirya komai domin duk da kasancewarsa ƙaramin matsubbaci akwai bukatar shiri akansa,in ba hakan ba sai asamu matsala."

"Ma sha Allah mun gode kwarai sosai Ranka Yadade Allah ya kara girma da sutura."
Baba Malam ya fada.

Yarima Rasheed ya ce,"Allah ya kara tsawon kwana da lafiya mai albarka muna godiya kwarai."

Mai Martaba ya ce,"Kar ku damu,amman dai ku daina tafiya babu tsaro,yanzu ma zan baku jami'in tsaro daya ya biku gwanda adunga kiyayewa domin Abdul-Raheem ya wuce duk inda kuke zato."

Da haka suka yi sallama,ya sa aka basu jami'in tsaro daya ya shigar motar kafin suka dauki hanyar komawa mokwa.

Suna isa gidan Baba Malam suka fara sauka,aka ajiyeshi sannan Yarima Rasheed yasa manager da ya sa a kawo masu kayan abinci da duk wani abu da yake da bukata shi da iyalansa, ya umarci jami'in tsaron da ya koma sannan shi kuma ya dau mota ya koma gidan al'adu.

☆☆☆Mai Martaba ya Sarkin Al'adu ya kasa zaune ya kasa tsaye,
Kai da kawowa yake, ita ma Kilishi a bangarenta kai da kawowa take kawai.
Da ta kasa hakura afusace kawai ta shiga Bangaren Mai Martaba domin ya kasa zaman Fadar tun da Yarima Rasheed ya zo ya fada masa maganganun nan ya gagara gane komai.

Tana shiga ta ce,"Wai kai wani irin mutum ne, shin ka zama Mace ne da ba za ka iya daukan mataki akan wancen wawan ba? Kar ka manta fa tun da cen ba ishasshen wayo gareshi ba amman yanzu ka barshi har yana iya tada mana hankali? Ba ma wannan ba ga dukkan alamu fa so yake ya karbi mulkin nan, kana gani? Ka zuba idanu  kana gani ba wani matakin da zaka iya dauka?"

Tsawar da ya yi mata ne yasa ta dawowa cikin hayyacinta.
"Ke kin fini son sarautar nan? Kin san tun ina da shekaru nawa a duniya na fara wannan shirin? yayin da ake yiwa Ɗan shekara goma kallon yaron da bai san me yake ba,ni a lokacin na jima da gama fara shirina,kuma ba wanda ya isa ya tarwatsa mun komin tsanani ko da kuwa zan rasa raina ne sai dai kowa ya rasa,ki fice mun da gani tun kafin ranki ya yi mugun ɓaci."
Ya faɗa a fusace yana nuna mata bakin kofa.

Daren ranar gabadaya yan gidan taruwa sukai a falon Hajiya kaka illa Mai Martaba da Kilishi da suke can suna fama da tasu damuwar.
Sai da dare ya raba kafin kowa ya koma part dinsa.
Janinah kuwa damuwarta kawai hanyar da zata bi ta kaiwa Farouq abinci.
Ta zo zata bashi kenan daya daga cikin masu gadin suka kamata.
Aka sanar da Mai Martaba dukkanin yan gidan kowa ya fito aka yi cirko-cirko.

Cikin fushi Mai martaba ya bada umarnin cewa ita ma a turata ciki tunda har tana tausayinsa ai sai ta tayashi zama.

Hakan kuwa aka yi.
Maamah da sauran matan sai kuka.
Cikin karfin hali ta kalli Mai Martaba ta ce,"Amman ka cika azzalumi na karshe."
Ta tafi tana kuka.

Ko kallonta bai yi ba ya gyada kai ya juya ya tafi abunsa shi ma.

Kilishi kuwa wani irin kumburi ta fara tana nishi a zuciyarta tana fadin,"Lallai rasa ran yarinyar nan daidai yake da wasa da rayuwar sarautar Arham,ba zai saɓu ba,ba kuma zan lamunce ba."
Ta kudurta aranta itama tana tafiya.

☆☆Farouq ya ce,"Tausayina ya sa kin jefa kanki cikin matsala, ban ji dadi ba,kuma ban so faruwar hakan ba,ki yi hakuri ki yafe mun nine sila."

Janinah ta laluba hannun Farouq ta rike,"Zamana cikin duhu da yunwa tare da kai ya fi mun zamana cikin haske da abinci Ya kai Ɗan Uwana,bana jin tsoro ko fargabar komai indai zan kasance a tare da kai,ban yi nadama ba,kuma ba zan taɓa nadama ba."

Hira suka dunga yi har barci ya kwashe Janinah.

☆☆Da asubar fari aka fara yekuwar Rasuwar Baba Malam,Yarima Rasheed ya fito da sauri yana kara maimaitawa,"Baba Malam?"
Ba shakka sunanshi ya jiyo ana sanar da cewa za a sallace shi.

[06/07, 2:52 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH

KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-31

Zuwa ya yi shima ya shiga sahu suka sallace shi bayan sun dawo ya gidan Baba Malam ya koma.
Yana zuwa ya tarar da Iyalansa nata kuka,Yaransa da Matarsa wacce karfi ya gama barin jikinta.
Yarima Rasheed bayan ya gama yi masu gaisuwa ya ce,"Amman jiya fa ƙalau muka dawo da shi gida,bai nuna mana wata alamar rashin lafiya ba."
Matarsa ta ce,"Tabbas ya shigo lafiyarsa ƙalau cikin yanayi na farinciki ma irin wanda zan iya cewa na jima ban ga annashuwa a fuskarsa kamar jiyan ba tamkar wanda aka yiwa albishir da gidan aljanna kuma har ya kwanta yana cikin ƙoshin lafiya,asuba ta yi,mun saba shi ke tashinmu sallah yau muka ji shiru har na tashi,hakan yasa na je dakinsa in duba ko ya makara ne tunda jiki da jini kila gajiya tayi yawa ashe shi ya jima da barin duniyarma akan shimfiɗarsa,yanzu irin mutuwar da ake kenan zaka rabo da mutum lafiya yanzu anjima ka ji ance ya bar duniya,Allah Ubangiji ya ji kanka ya gafarta maka Malam."
Ta karasa maganar tana share hawayen da ke zuba a idanunta.

Yarima Rasheed ya amsa da,"Amin amin,Allah ya kara hakuri,bara inje."
Ya masu sallama sannan ya fice zuciyarsa cike fal da sake-sake domin bai gamsu cewa Baba Malam Mutuwa ya yi kawai ba babu shakka akwai sanadi.
☆☆☆☆
Cikin fushi Kilishi ta kara nufa Bangaren Mai Martaba.
Zaune yake ya yi tagumi yana tunani a bakin gado.
Hankada kofar ta yi kawai ta shige ba tare da ko sallama ba.

"Alkawari dai kayane kuma kasan nima na sha wahala wajen tabbatuwar burinka tare da nufin nima za ka cika mun nawa,nina rufa ma asiri kuma baka goyon bayan kashe mahaifinmu sannan ka kore Ɗan uwanmu,ka sheda mini cewa mulki daga kanka zai dawo karkashina ga duk Ɗa namijin da zan haifa,hakan yasa muka shirya haɗa auren Janinah da Arham domin tafiyar komai cikin sauki amman yanzu na lura ita kanta yar taka ma so kake ka kasheta,to ni wallahi Allah na yi rantsuwa babu kaffara ko da ace yarka ta bar duniya batun zama Sarkin al'adun Arham babu fashi,ni bai dameni ba duk yadda zaka yi ka je ka yi domin tallafar mulkin

nan in ba haka ba kuma ko da allura ta tono garma kai ka sani kuma ina kara tunatar da kai cewa kamar yadda zaka iya komai akan Sarauta nima zan iya kila ma mafiyin hakan."
Tana gama faɗin hakan ba tare da ya ce mata komai ba ta fice abunta.

Dafe kanshi ya yi yana juyawa tare da bin ficewarta da kallo kawai.

☆☆5stars sunji shirun Farouq ya yi yawa,mussamman Zeeyter ta damu,Zoe kuwa har Khalil ta kira tana tambaya shin lafiya kuwa domin wayarsa akashe,dake sun karbi wayar sun kashe kafin suka sa shi a dakin duhun.
Maaah kuwa da ta kira su sanar da ita cewa sukai aikine ya masa yawa amman yana cikin koshin lafiya suka dai yi mata jawabin da zai kwantar mata da hankali duk da cewa ita dai jikinta ya bata cewa akwai matsala lallai Farouq na cikin wani hali.
Ganin ba yadda zata yi hakan yasa kawai ta dage ba dare ba rana ta na yi masa adduoi kamar yadda ta saba.

Number Javed suka nemo cikin record dinsu.
Suka fara bibiyarshi,da farko dai yaki fada masu komai amman daga karshe da ya fahimci su din su waye kuma Farouq na yawan bashi labarinsu hakan yasa ya laburta masu dukkanin abun da ke faruwa.
Lokaci guda suka shirya zuwa nigeria,Khalil ne ya kira Zoe domin daukan private jet,Khalil da kanshi ya je ya dauko Maah kan cewa Farouq ne ya ce a daukota,Deejerh da Xavier,Haiydar da Zeeyter dukkanin su sun hallara a malaysian daga nan suka nufo nigeria kai tsaye.

Sun sauka a Abuja sun kama hotel sai da suka kwana tukunna washegari suka dauki motoci biyu suka shiga cikin Niger da ke tun acen Haiydar ya masu ordern mota.

Suna shiga cikin Mokwan ma Hotel suka kama sannan suka kira Jeved suka sheda masa inda suke.
Javed ya sanar da Yarima Rasheed komai hakan yasa suka tafi tare.

Dukkaninsu suna zaune a falon hotel din,suna shiga Yarima Rasheed na hada ido da Maah ya kame kam bakinsa na rawa ya ce,"Ma....ri...am."

Ita ma ta ce,"Rasheed."
Dukkanin su suka yi shiru suna kallon juna,Zeeyter da Zahra ne suka tashi suka rike Maaah suka zaunar da ita sannan Khalil ya je ya rungume Yarima Rasheed yana fadin,"Welcome Dad."
Murmushin karfin hali ya yi kafin ya ce,"Thank you."
Shi ma ya zaunar da shi,Khalil ya ce,"Duk da cewa ku ne gaba damu kuma Iyayenmu amman muna neman alfarmar komai ya wuce please,mun san komai,kuma kowa cikinku ba ya da laifi akan barin kowa babu shakka wannan tsarin ubangijine,babbar damuwarmu a yanzu shi ne mu maida hankali kan fito da Farouq tare da taimaka masa kan tabbatar da kudirinsa na alkairi. "

Cikin zaƙuwa Maah ta ce,"Ina yake? Me ya faru da Umar? Me ya sameshi? Don Allah ku faɗa

mun."

Zahra ta rike hannun Maah kafin ta ce,"Maah In sha Allah Farouq na cikin koshin lafiya, Sarki Abdul-Raheem ne ya sa aka kulleshi a dakin duhu na tsawon kwanaki amman In sha Allah zai fito kuma cikin aminci da ingatacciyar lafiya. "

Ajiyar Zuciya Maah ta yi kafin ta daga hannunta sama tana fadin,"Ya Ubangiji na ya Allah kafi kowa sanin gwagwarmaya da kalubalen da wannan bawa naka ya fuskanta tun kafin zuwansa duniya da zuwansa yarintarsa,girman sa da yanzu,Ina Roƙanka da bashi ikon ganin haske saɓanin duhun da aka sanya shi,ka haneshi da jin yunwa,kishir ruwa da duk wata azaba dake tattare da inda yake,Allah ka kare mun shi ka ƙara masa kwarin gwiwa da karfin zuciya."
Ta karasa faɗan hakan tana goge hawayen da ke zuba daga idanunsa.

Rungumeta Zahra ta yi tana shafa mata baya.

Yarima Rasheed ya ce,"In sha Allah babu abun da zai same shi,sannan abun da yasa ba za ku je gudan yanzu za a iya samun matsala,a tsakanin daren jiya da asubar yau aka kashe Baba Malam wanda muke samun bayanai agunsa,shi kadai ne ya san komai,don haka ko da na ji mutuwarsa ban aminta da mutuwar ba a gaskiya nafi gasgata cewa kasheshi aka yi kuma domin taimaka mana da yake ne amman kuma abun da ba a sani ba shine akwai wanda yafi Baba Malam din don haka komai zai tafi daidai kuma sai an daukanawa Baba Malam fansa da ikon Allah,zaku ci gaba da zama anan tukunna in bukatar ku ta tashi zan sanar da Javed ya faɗa maku ku zo domin aikine ja a gabanmu babba ba karami ba."

Khalil ya ce,"Babu matsala muna nan kuma zamu bada goyon baya ɗari bisa ɗari sai mun tabbatar da kasancewar komai daidai kafin mu bar kasar nan da ikon Allah sannan muna tare Jami'in farin kaya na ɓoye." Ya nuna Xavier kafin ya ci gaba da fadin,"Zai fara yin binciken dukkanin abubuwan da ke tafiya ta ƙasa tare da tsaurara tsaro gudun samun kowacce irin matsala."

Yarima Rasheed ya ce,"Ma sha Allah na ji dadin hakan kuma nima zan haɗashi da wa inda zasu iya tallafa masa,Allah ya bamu sa'a. "

Bayan sun gama tattaunawa tafiya suka yi suka bar Maaah da Yarima Rasheed a falon domin su tattauna.

Dukkaninsu sunyi shiru kowa da abun da yake saƙawa a zuciya,lokaci guda kuma duka suka haɗa baki da fadin,"Shine....
Sai kuma suka yi shiru.
Murmushi Yarima Rasheed ya yi ya ce,"Ki ƙarasa ki faɗa."
Girgiza kai ta yi ta ce,"Aa ka yi maganar ka tukunna."
Ya ja numfashi kafin ya ce,"Shin kin san da cewa na koma ƙasarku ban sameki ba? Me yasa baki nemi ni ba? Me yasa baki zauna a gunda kika san zan iya ganin ki ba?"

Maah ta ce,"Ban yi tunanin zaka nemeni ba ganin yadda aka rabamu hakan yasa ko da dana koma gida Iyayena suka ƙi karbana da Addinin musulunci na gwammace da na bar ƙasar dukanta domin in samawa kaina da Ɗana sabuwar rayuwa."

Yarima Rasheed ya durkusa gabanta yana fadin,"Ki yafeni Mariam, duk nine sila,ni ne silar faruwar komai, Don Allah ki yafe mun na san na yi kuskure babba a rayuwata ki yafemun. "

Murmushi ta yi kafin ta ce,"Kuskure kam dukkaninmu munyi domin da ace ban yi sanadiyar da zaka sha giya ba,da duk komai bai faru ba,amman kuma Bawa baya taɓa wuce kaddararsa sai dai ya ķasa karbanta yadda ta dace,sannan kasancewata da kai ko ba komai ya zame mun alkairi domin kuwa gani ina rayuwa mafi dadi da yaƙini wato rayuwar musulunci sannan Farouq duk da cewa ba ta hanyar aure aka sameshi ba amman kuma ya zam alkairi gareni da ma dumbin al'umma masu yawa tabbacin shi Ubangiji mai rahama ne kuma mai jinƙai sannan mai ƙarban tuba,don haka ka tashi ka zauna jima da yafe ma kamar yadda nake sa ran cewa Ubangiji ya yafe muna muma."

Tashi ya yi ya zauna yana fadin,"Ba shakka hakane amman na ji dadin dauwamarki cikin addinin musulunci sosai da ace wasu ne duk abubuwan nan ya faru da su tuni zasu fice."

"Rashin karfin Imani da karban kaddara ke kawo hakan kuma ai aduk inda zaka kasance dole akwai kalubale muddin kana rayuwa cikin duniya."
Maaah ta fada.

Yarima Rasheed ya ce,"Hakane kam, abu mafi dadi shine da baki yarda zoben alkawarinmu ba kamar yadda nawa yake nan."
Kallon zoben suka yi duka suna Murmushi,ya ci gaba da fadin,"Sannan kuma na ga Farouq ya taso da sanin Computer yana abubuwa tamkar ni."

Maah ta ce,"Ai ance kyan Ɗa ya gaji ubansa hakan yasa tun yana jariri nake kwaɗaita masa so da kaunar na'ura hakan yasa ya ginu cikinta tun daga yarinta har girma karshe ma sai ya nuna mun ya fini sonta."

Kallon agogon hannunsa ya yi ya ce,"Oh lokaci ya kure,bara inje zakuji duk abun da ke tafiya. "

Sallama suka yi fita ya samu Javed da Manager suka tafi.

Suna shiga cikin gidan.....
[10/07, 3:23 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa

Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .

MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-32

Suka ga anyi cirko-cirko an fito da Janinah tana numfashi sama-sama.
Masu maganine kewaye da ita sunata faman kokarin ganin sun ceto rayuwarta.
Da sauri Yarima Rasheed ya karasa yana fadin,"Subhanallah me ya faru?"
Abba Malik ya ce,"Wallahi Janinah ce ba lafiya yanzu masu gadin dakin suka sanar da mu kan cewa Farouq na ta kwala kira,da kyar take numfashi gabadaya yanayinta ya sauya jikinta kuwa duk ya gama sakewa."
Karasawa inda take Yarima Rasheed ya yi ya dauketa yana ,"Wannan ina ga akwai bukatar aje asibiti."
Yana fada sai suka fara kallon kallo.
Mammah kuwa ban da ruwan hawaye babu abun da take ta kasa zaune ta kasa tsaye.

Kallon Abba Malik Yarima Rasheed ya yi ya ce,"Ku dauko mota muje asibiti mana ko baku ji bane?"

"Ai Mai Martaba ya haramta zuwa asibiti a cikin gidan nan sai dai masu maganin gargajiya su duba mutum kawai." Abba Malik ya fada.

Tsaki Yarima Rasheed ya yi cikin ɓacin rai Ya ce,"Yarinya sai suma take tana farkawa da wani irin numfashi ku tsaya wasa ai sunyi iya yinsu tunda abun ya gagara dole ne akaita asibiti akan wata dokarshi sai a bari yarinya ta rasa ranta?" Ya karasa maganar yana daukan Janinah a hannunsa.

Muryar Mai Martaba ya jiyo yana faɗin,"Ka da ka yi gigin fita da wannan yarinyar daga cikin masarautar nan in dai masu magani ba za su iya ba sai dai amaidata cikin dakin da take ta mutu acen domin ni duk wanda ya shiga gonata babu ragi tsakanina da shi ko da kuwa ɗan cikina ne."

Kallonshi Mammah ta yi tana hawaye kafin ta ce,"Ban taɓa tunanin rashin imani da tausayinka ya kai har haka ba,to wallahi ko da ace hakan shi zai zam sanadiyar mutuwar aurena sai dai ka sakeni amman ina goyon bayan a fidda 'Yata akaita asibiti. "
Ta karasa maganar tana tsayawa gaban Yarima Rasheed.

Yarima Rasheed ya ce,"Ba ruwana da wata dokarka domin bata shafeni ba, sannan a yau zan fita da Janinah asibiti ne a matsayin Mahaifi gareta kuma Yaya ga wanda ya haifeta." Yana fadan hakan ya bude mota yasa Janinah ciki Mammah ma ta shiga ciki sannan Abba Malik ma

ya shiga suka fice daga Masarautar.

Bin kowa da wani kaskantaccen kallo Mai Martaba ya yi sannan ya ja dogon tsaki ya tafi.
Yana zuwa wayarsa ya dauka yana ,"Kana ji ko sun fita daga gidan nan zasu kai Janinah Asibiti ko da ace yanzu baka samesu ba a hanyarsu ta dawowa ka tabbatar na ji labarin cewa dukanninsu numfashi ya bar gangar jikinsu,kar ka ragawa kowa hatta  Yiniyetsu da Janinar kai koma da waye ka gansu ba ka da matsala kawai ka sanya aga bayansu."

Daga cikin wayar aka amsa shi da fadin,"Kar ka damu Ranka Yadade an gama wannan karan dai kam In sha Allah ba za asamu wata matsala ba,za ka jiyo sakamako mai kyau kawai ka zauna cike da jin cewa komai ya kammala."

Katse wayar ya yi kawai ba tare da ya ce komai ba,ya jefata kan kujera,sannan ya zauna.

☆☆General Hospital Mokwa  suka kaita,suna zuwa kuwa aka karbeta aka fara yi mata taimakon gaggawa.
Likitoci na kanta na tsawon  awa biyu wannan ya shiga wancen ya fita,har suka samu nasarar ceto rayuwarta.
Likita ya sanar da Yarima Rasheed cewa Janinah na bukatar hutu sosai sannan ta sanya damuwa aranta wacce take barazana da ranta haka kuma akwai yanayin takura a tattare da ita don haka tana bukatar hutu da kulawa sosai.
Bayan ya gama yi masa bayani an rubuta masu magunguna sannan aka sallamesu duk da cewa shi likitan ma bai so sallamarsu aranar ba acewarsa ya so ace ta kwana ko da uku ne ta dan huta tukunna,Yarima Rasheed ya sheda masa cewa ba matsala a gidanma zata samu fiye da yadda suke zato.

Ana fito da Janinah ta kalli Mammah tana fadin,"Mammah ina Yah Farouq? Shi ma an fito da shi? Yana ina? Ku kaini in ganshi wallahi bai yi ma Mai Martaba komai ba,bai aikata laifin komai ba."

Yarima Rasheed ne ya katseta da fadin,"Yayanki na lafiya Janinah yana gida,ki kwantar da hankalinki kuma ki nutsu mu tafi gida."
Hakan yasa ta yi shiru ba don ta gamsu ba kawai ta dunga binsu da kallo tana sake-sake a zuciyarta.

Suna cikin tafiya suka ji mota ta fara masu misbehave tana kokarin jefa su cikin rafi,duk kokarin Abba Malik ya yi don ganin sun kauce abu yacitura,ga wasu motoci daya a gabansu ɗaya a baya duk sun ƙi basu space sannan kuma inda suke waje ne da ba cika wucewa sosai ba ya yi bayan gari.

Sun fara galabaita dukkaninsu,tun suna iya addua har sunyi shiru sun fidda tsammani domin motar har ta haye gadar tana kokarin fadawa cikin rafin.

Kamar daga sama suka ga motar ta kame ƙam jikin wani dutse bayan duk sun gama sadakarwa sun mutu.
A hankali suka fara bude idanunsu.
Juyawan da Abba Malik zaiyi ya ga tarin jami'an tsaro tare da Xavier kamar an zubosu.
Wa innan masu motoci biyun kuwa fara neman hanyar tserewa suka yi,suna yi suna taresu da kyar suka samu suka gudu.

Bayan sun tafi aka kira babbar mota ta janyo tasu Yarima Rasheed suka fito duk sun gama galabaita mussamman Janinah da daman ba lafiya gareta.

Xavier ya ce,"Fatan dai dukkaninku babu wanda ya ji rauni?"

Abba Malik ya ce,"E kam Alhamdulillahi. "

Ya ci gaba da fadin,"Sun gudu amman In sha Allah za a kamasu domin turosu akai."

Yarima Rasheed ya ce,"Lallai kam sannunku da kokari muna godiya Allah saka da alkairi ."

Murmushi Xavier ya yi ya ce,"Ai Ɗa baya bukatar godiya daga wajen Mahaifi. "
Shi ma murmushin ya yi kafin ya ce,"Wannan haka yake,To Ubangiji ya yi muku albarka duka. "
Da Amin ya amsa aka basu wata motar da jami'ai biyu suka nufi gida domin tasu ba zata yi aiki ba.

Mai Martaba nata zirga-zirgan jiran sakamako,sautin gate da aka bude ne ya bashi damar bude labule yana leƙe ta window.
"Su ne suka dawo." Abun da ya furta kenan cikin yanayi na rashin kwarin gwiwa.
Haka kuwa ya ga duk sun fito,Mammah rike ta tallafe Janinah wata irin kwafar takaici ya yi yana dafe kansa.
Waya ya dauko cikin sauri ya kara a kunne yana fadin,"Wannan wani irin iskanci ne? Sau biyu ina saka aiki kwanan nan amman shiru baka iya yin komai? Wannan ai shashanci ne."

Da ga wayar aka amsa da fadin,"Haba Yallaɓai  kai dai kasan shekara da shekaru muna tare ba a samun matsala sai wannan karan kuma ba wai gagara mukai ba kawai dai na lura kamar yadda muke shiri akansu haka suke shiri akanmu domin yau da kyar muka samu tsiratar da rayuwarmu da saidai kaji asirinmu duk ya tonu amman dai ka yi hakuri da ikon Allah idannunmu na kansu duk har sai mun aiwatar da muradinka."

"Duk yadda za ayi nidai kawai ka aiwatar kuma wanda zaku fi sa idanu akai Rasheed ne kawar da numfashi a jikinsa shi ne samun zaman lafiya na da ku dinma gabadaya. " Maimartaba ya fada yana katse wayar.
[12/07, 9:40 am] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-33

A bangaren Hajiya Kaka aka aje Janinah tukun su Rasheed suka fita,Mammah na fita kawo mata abinci  Janinah ta kalli Hajiya Kaka ta ce,"Hajiya Kaka an fito da Yah Farouq? Yana lafiya?"
Taɓe baki Hajiya Kaka ta yi cikin yanayin damuwa ta ce,"Aa kuma ma bamu san halin da yake ciki ba."
Shiru Janinah ta yi,take hawaye suka fara ambaliya  a fuskarta,zuciyarta ban da zafi babu abun da take yi mata,duk da cewa Mai Martaba mahaifinta ne ba yadda za ta yi da shi amman har cikin ranta ji take babu wanda ta tsana a duniya yanzu sama da shi.

Cikin dare kamar daga sama suka fara jiyo dirowar  mutane cikin gidan,fuskokinsu a rufe,bangaren ka aka fara sanyawa makulli aka rufe sannan bangaren su Junaid ta yadda ba za su taɓa iya fitowa ba.
Wasu irin manyan maza ne masu kirar samudawa,wajen Yarima Rasheed suka fara nufa suka daukoshi tamkar daukan amarya suka direshi gaban Mai Martaba sannan suka kulleshi tamkar dabba,Murmushin mugunta Mai Martaba yake yana binsa da kallo sannan suka je suka dauko Mammah da Abba Malik ma duk suka dauresu.

Kallon Mammah mai martaba ya fara yi yana faɗin,"Karshen alewa ƙasa,ina yanzu ke kina ganin cewa kinfi karfin bin umarni na? Kin fi karfin inyi magana kiyi shiru? Ina faɗa kina faɗa? Idanunki cikin idanuna? To ki sani ni bana tuna alkairan mutum ko ya yamun kuskure rufe idanu nake take in dau mataki."

Mammah ta ce,"Sai dai hakan ya zam silar katsewar numfashina amman ina kara fada kuma zan fada a ko ina ba zan taɓa bari 'Yata tai rayuwa irin wacce na yi ba,ba zata zam baiwa ba kuma ba zata zama tamkar tsummar goge takalmi ga mijinta ba,sannan ba za ayi mata auren dole ba har sai da amince....
Kafin ta karasa maganar ya buga mata wani katon karfe aka har sai dai ganinta ya dauke ta fara ganin dishi-dishi da wani duhu-duhu azaba na ratsata, har cikin kwakwalwarta sai da ya amsa.
Mai Martaba ya ce,"Ni Sarkine ba iya na al'adu ba,sannan duk wanda zai rayu a cikin wannan gidan zai rayu ne cikin karkashin ikona don haka duk wanda ya ce zai bijire mun zan iya hallaka rayuwarshi zuwa lahira da ga ke har 'Yarta ki da wa inda kuke goyawa baya duk sai kunyi dana sanin bijire mun."

Cikin Muryar Kuka Mammah ta ce,"Baka isa ka yi muna abun da Ubangiji bai mana ba,kuma ina ji a jikina cewa ƙarshen zalincinka ya zo."
Cikin fushi ya buga mata kafarshi a bakinta sai da ya fashe jini ya fara zuba ya ce,"Ki yi mun shiru nan domin rayuwarki bata da amfani a yanzu."
Komawa ya yi gaban Yarima Rasheed yana dariyar mugunta,"Rasheed ke nan,ka manta ni wane ne ko? Ka manta cewa tun lokacin yarinta bana raga maka bare yanzu? Ko kana tunanin dukiyarka ce zata iya sawa kafi karfina a yanzu? Ka yi makahon tunani,ka dawo ka karfi sarauta ko? To haramiyarka  domin ba zaka taɓa samu ba shi kuwa wancen Ɗan naka Shege tunda na fahimci ba zai iya gadon sarauta ba,tunda a garin yawon tambaɗa da tazubar aka sameshi na fita a sabgarsa ba don yana son shiga mini hanci ba da tuni na barshi domin ko a hakan ma kadai rayuwarshi watsatsiyace shiyasa kawai na turashi wancen dakin har ya gaji ya mutu in ya yi mushe sai ma jefar cikin rafi."

Cikin Karfin hali Yarima Rasheed ya ce,"Duk da kasancewar mun sameshi ta hanyar da bata dace ba amman yafi yara dubu da aka haifa ta hanyar da ta ce inganci ɗaya daga ciki kuwa harda kai." Ya karasa maganar yana nuna Mai Martaba.

Cikin Fushi Mai Martaba ya tashi tsaye yana zagaye Yarima Rasheed can kawai yana daga wani katon karfe ya sake mishi a baya sai da jini ya fara fitowa ta cikin bakinshi idanunsa suka rufe.

Dariya Mai Martaba ya ci gaba da yi kafin ya ce,"Ni kuwa da kake gani ai nafi yara miliyan ma ba ɗari ba,domin ni kadai gayya."

Cike da azaba Yarima Rasheed ya ke fadin,"Ina Mai Tabbatar maka da cewa Ɗana ba zai barka ba ko da ace ni ka kasheni to ka san da cewa tamkar ka ƙarawa kanka nauyi ne ba wai sauki ba,Farouq ne maganinka kuma zaiyi maganinka ba makawa."

Mai Martaba ya tallafo fuskar Yarima Rasheed ya ce,"Wai kai ko kunya ma baka ji? da ɗan shegen kake alfahari da taƙamar zai iya yi mun wani abu? To bari ka ga yanzu zansa a ciro mun shi duk in gama daku anan kafin zuwa safiya labarinku ya kau a duniyar nan."

Abba Malik ne ya yi magana,"Haba Don Allah, wai kai wani irin azzalumin mutum ne mara imani mara tausayi da jin kai."
Wani zazzafan mari ya kai masa wanda sai da hannayensa sukai shata a fuskar kafin ya ce,"Ni Mutum ne mai son sarauta wanda zai iya komai akan mulki domin har ubana na kashe domin inyi sarauta don haka inna kasheku ba komai bane."
Ya karasa maganar yana umartar daya daga cikin yaran nasa da su dauko mishi Farouq.
Hakan kuwa ya kasance zuwa suka yi suka fito da Farouq daga dakin duhu suna shiga da shi hasken dakin ya kanne masa ido tuni ya rufe ba tare da ya fahimci suwaye ba kuma meke faruwa ba.
Durkusar da shi suka yi shima suka ɗaure.

Mai Martaba ya riƙo gashin kan Farouq yana faɗin,"Kai Ɗan shege ga shegen mahaifin naka nan kuma shi ne ya janyo maka mutuwa cikin azaba domin ada na so ace ka yi mutuwar sauƙi ne cikin wancen dakin."

Janye kansa ya yi ya fisge idanunsa a rufe ya ce,"Kar ka kara kuskuren kira Mahaifina da Shege domin shi ba shege bane kuma bai haifi shege ba, in ma akwai shege to babu wanda ya fika."

Mai Martaba ya janyo kan Farouq yana sheƙe masa wuya,"Ayyah ashe dukan ku haka kuke da taurin kan ko? Ah lallai Maddalla,ba za kuyi mutuwa cikin sauki ba har sai nasa dukkanin ku an gama jigata mun ku."

Ya faɗa yana komawa kan kujera ya zauna,umarni ya bawa masu kirar samudawan da su fara jibgarsu har sai jikin kowa ya yi la'asar.
Hakan kuwa aka yi,ita kam Mammah da ta ji bugu tuni ta sume a wajen suka bar ta kanta.
Jibgar Farouq,Yarima Rasheed da Abba Malik suka dunga yi har sai da suka jijji masu raunuka duka,sun gama fita a hayyacinsu domin ko magana basa iyawa sai jini da keta ambaliya daga gaɓobinsu.
Bindiga yasa aka miƙa masa yana faɗin,"Da hannuna zanyi wannan aikin domin samun nutsuwar zuciya da ruhina."
Daga bindigar ya yi ya seta daidai setin Yarima Rasheed yana ja........
[12/07, 3:26 pm] Xayyeesherthul-humaerath🍂: *CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊
*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace

- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA  TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-34

Suka jiyo wata karar harbin bindigar daga waje.
Yarima Rasheed da su Farouq sun gama sadakarwa Mai Martaba ya harba ashe ba shi bane. A zabure ya tashi yana,"Su waye? Ba na hana shigowa gidan nan ba tare da amincewata? Cikin wannan daren ma?"  Ganin Xavier suka yi da tawagar shi ta jami'an tsaro da su Khalil har da Maah.

Tuni masu kirar samudawa suka fara neman hanyar guduwa,cikin kankanin lokaci aka nemesu aka rasa,dibi-dibi Mai Martaba ya fara yana,"Ku kuu kuu su waye wa innan? Yana nuna su da yatsa yana baya da bindigar da ke hannunsa.

Fara kunce daurin goron da aka yiwa su Farouq suka.

Ƙara Mai Martaba ya yi ya kira dakaranshi suka tsaya a bayansa sai a lokacin tsafin barcin da ya dasawa sauran yan gidan ya fita,a tare duka suka farka cikin razana kowa yana kokarin bude kofa amman sun kasa.
Hakan yasa Xavier yasa jami'an suka bibbige kofofin kowa ya fito,gabadaya a falon Mai Martaba suka haɗu kowa na kallon kallo,ga mutane da basu taɓa gani ba kuma gasu Mammah cikin wali hali.
Da sauri Janinah ta rungumi Mammah tana fadin,"Me ya sameki? Mai Martaba ne ko? Na san shi ne shi ne." Ta karasa maganar tana rungumeta tana kuka.

Hajiya Kaka na zuwa ita ma wajen Yarima Rasheed ta yi ta rugumesa ta kasa fadin komai sai kuka.

Zoe kuwa gun Farouq ta wuce tana cire dankwalinta ta daure masa gwiwar hannunsa da jini ke kwarara,har a lokacin baya gani sosai.

Cikin karfin Hali Mai Martaba ya ce,"Ko ma ku su waye,zuwanku ba zai haifar da komai ba ko ince ba zai taɓa hanani cika muradina ba,babu shakka sai na kashesu dukanninsu kuma babu abun da aka isa ayi mini."

Maah ce ta kallesa cikin karfin hali bayan ta shafa kan Farouq ta ce,"Ina mamakin da kake iya tutiyar cewa kai musulmi ne amman kuma kake rayuwar da wasu Christian din ma basa yi,dukkanin wani musulmi an san shi da tausayi,adalci da kuma gaskiya amman kai ko guda ɗaya ban ga hakan a tattare da kai ba."

Dariya ya yi yana karewa Mammah kallo.
"Oh har da su jaɓa a cin ɗanko? Ai sai ki ce mun ga ki nan kinzo Arniya,kafira kodayake shiyasa daga shigowarki na ji kamshin gidan ya sauya ya kamata ace ko da hakan in fahimci cewa akwai kafira a tare da mu."

Murmushi Maah ta yi kafin ta ce,"Ko ada da nake ba cikin addinin musulunci ba ni ba kafira ba ce kuma ba arniya ba ce domin wa inda ake dangatawa da wa innan sunayen sune marasa addini ni ko ina da shi,bare ma yanzu da nake cikakkiyar musulma, kai fa akanka ne ma nake tantamar cewa kafi kama da kafiran domin rayuwarka sak tasu ce,kana shiga cikin rigar addini kana yin baɗala da sunan kai musulmi kuma jagora,musulmi na kwarai baya shirka kuma baya danne hakkin kowa,ka tozartani a lokacin da na fi bukatar tarairaya cikin addinin Allah ka wulaƙantani duk da cewa ni tubabbiyace baka duba hakan ba illa danganta tuba da tuban muzuru,ka nuna mini cewa duk wa inda ba a haifesu a musulunci ba ko da sun tuba ba za su taɓa zamtowa ɗaya da wa inda aka haifa ciki ba,bayan kuma Ubangiji bai ce hakan ba hasalima ya yiwa wa inda suka tuba rangwamen da wa inda aka haifa ciki basu samu ba,irinka ne masu hana al'umma rayuwa cikin addinin Allah."
Ɗaya daga cikin dakaran ne ya yi mata tsawa da fadin,"Hattara dai,ba ayiwa Mai Martaba

kakkausan lafazi."

Dakatar da shi ya yi da hannu yana,"Bar ta barta ta fadi dukkanin abun da ke ranta."

Ci gaba da magana Maah ta yi,"Irinka ne masu cirewa mutane kwaɗayin zama cikin musulunci,irinka ne ke sawa adunga yi wa musulunci da musulmai mummunan zato da kallon da bai dace ba,irin kane masu dasawa mutane shakku akan musulunci,da ace zuciyata ba ta gama aminta da rayuwar musulunci akan shi ne rayuwar gaskiya ba da tuni ka jima da sawa in koma ruwa,na tabbatar da cewa Allah na gani kuma yana ji ba zai taɓa barinka haka ba domin shi ba azzalumin bawansa bane."

Dariya ya yi kafin ya ce,"Babu shakka na ji dadin zuwanki nan domin kema zaki shiga sahu,wa innan jami'an tsaron kuma kun san sarai baku da ikon taɓani ka dakatar dani domin ina da mulki a hannu har sai Mai Martaba sarkin bida ya amince don haka zaku iya tafiya ku barni in aiwatar da muradaina ko kuma kuma ku shiga sahu."

Xavier ya ce,"In su yan nigeria ne ni ba dan nigeria bane sannan zan iya aiwatar da komai da na yi akanka ba tare da an dakatar dani ba laifukanka suna da yawan gaske ya kamata ace a yanzu kana kokarin nemawa kanka mafita ne."

"Mafita? Mafita? Ai indai Sarauta na hannuna to babu wata matsala da zan rasa mafitarta."
Karasa maganar ya yi yana yana gyara bindigar da ke hannunsa ta baya.
Karfe biyar in asuba kenan daidai.
Sautin kiɗan sanarwar zuwan Sarkin Bida ya jiyo wanda hakan ne yasa shi gaggawar jefar da bindigar baya.
Sarkin Bida da tawagarsa tare da Hakimin Mokwa ne suka shiga gidan.

Mai Martaba na ganinsu ya fara kame-kame.
Da sauri yaje ya taro Mai Martaba yana fadin,"Ranka Ya dade barka da zuwa,lafiya? Da asubar nan."
Murmushi ya yi kafin ya ce,"Lafiyar ke nan."
Ya karasa ya zauna sai da ya karewa kowa kallo kafin ya ce kalli Yarima Rasheed ya ce,"Wato abun da ke faruwa ke nan?"

Kafin Yarima Rasheed ya amsa karaf Mai Martaba ya ce,"Ranka Yadade wallahi wasu yan ta ad....

Kafin ya karasa ya dakatar da shi da hannu kafin ya ce,"Ku fara cire masa rawanin da ke kansa."
Nan fa Mai Martaba ya kara ruɗewa sanyi ake amman shi zufa yake yana daga riga yana fiffita.

Sai da aka warware masa tas kafin Mai Martaba Sarkin Bida ya ce,"Daga yau kai ba sarkin

al'adu bane,kuma ba zaka kara kasancewa wani sarko ko mai sarauta ba domin kuwa ka riga da aikata abun da zai rabaka da sarauta tun farko."

Abdul-Raheem ya ce,"Ranka Yadade ni ban aikata komai ba sai dai in sharri ake so ayi mini kuma nasan wannan aikin Rasheed ne yana bakinciki dani tun muna yara kuma yanzu ma yana so ya kwace mun sarauta."

Mai Martaba Sarkin Bida ya bada umarni aje a shigo da wani.
Aiko Abdul-Raheem na ganinsa ya razana bai san sanda ya furta ba,"Dr Imam."
Suna kallon kallo.
Murmushi Sarkin Bida ya yi kafin ya ce,"Yanzu ka gasgata abun da nake nufi ko? DR Imam ya sheda mini komai yadda ya tallafa maka ku ka yi sanadin kashe Marigayi Mai Martaba Sarkin Al'adu wato mahaifinka wanda a karshe ka bashi kudi mai yawa da sharadin zai bar nigeria kuma hakan ne ya kasance,munyi bincike mun gano inda yake kuma ya kara tabbatar mana da komai don haka baka cancanci zama sarki ba,daman asalin sarauta ta Abdul-Rasheed ce ka yi masa kurciya Allah ya dawo da shi don haka shi zai amshi abunsa."

Kasa magana ya yi yana wani irin huci.
Yarima Rasheed ya ce,"Amman Mai Martaba ina neman wata alfarma ni daman ko ada cen bana da sha'awar sarauta da ace baiyi saurin aikata hakan ba ma ni zan iya bar masa amman yanzu in ba damuwa abarwa Farouq madadina."

Ka da bakin Abdul-Raheem ya ce,"SHEGEN? Wanda aka haifa ba ta aure ba?"
dukansu sai suka fara kallon-kallo......

*Yau har page biyu kuka samu,Gaskiya na ci kyauta 😌*
*CENTURE*

NOBLE WRITERS ASSOCIATION

Labari/Rubutawa
Aisha Sani Abdullahi
Xayyeesherthul-humaerath

The End Of A 5-Stars Chronicle
# Yel#Freeya#Vixeen#Centure.

*We're offering affordable advertising opportunities for your business. Contact me at 08103080717*

PAID ADVERT
*Saudahtu Collections&Data Services*
Your one-stop shop for all your fashion needs! 😊

*What We Offer:*
- Abayas
- Hijabs
- Shoes
- Shadda lace
- Normal lace
- Fabrics
- Bed sheets
- Materials
- Kitchen essentials
- Home decor
- s dresses
- English wear
- And many more!
*Visit Us:*
Aliyu Mustapha, Yola and Kano Dorayi
*Get in Touch:*
Call/Text: 08036600240
*Nationwide Delivery Available! 🚚*
You can join our group
https://chat.whatsapp.com/EKg8iYM65EcCLY6KZIQhlT
*Stay Stylish with Saudahtu Collections!*

PAID ADVERT
INA MATA MASU NEMAN MAGANIN INGANTA NISHAƊINSU DA MAI GIDA, INA MASU SON ZAMA TAURARI AGIDANSU ?MAZA GARZAYO GUN YAR SOKOTO DA IZNIN ALLAH KAYANKI SUN TSINKE A GINDIN KABA

INA MASU FAMA DA INFECTION KUZO GA MAGANI DA YARDAR ALLAH

AMAREN GOBE, KU MA BAN MANTA DA KU BA .
MUNA DA GARIN MAGANI KALA-KALA GUMBA KALA-KALA KAZA, DANBUN KAZA TSIMI SA TABAJE DA DAI SAURAN SU. DOMIN KANKARO MIKI MUTUNCI A WURIN YALLAƁAI SAI AN GWADA AKAN SAN NA KWARAI KUMA SIYAN NA GARI MAI DA KUDI GIDA.

DOMIN ƘARIN BAYANI KU KIRA WANNAN NUMBER 08159450159 KO TA WHATSAPP

PAGE-35

Mai Martaba Sarkin Bida ya kalli Yarima Rasheed ya ce,"Hakane?"

Girgiza masa kai ya yi alamar E.
Numfasawa Sarkin Bida ya yi kafin ya ce,"To ka ga indai hakane kuwa Ɗanka bai da hurumin

gadon sarauta sai dai kai din ko kuma aba wani."

Khalil ne ya katse su da fadin,"Ranka Yadade ina so inyi magana in an bani dama duk da cewa bana ɗaya daga cikin ahalin wannan gida."

Sarkin Bida ya ce,"Ba matsala Bismillah za ka iya magana."

Khalil ya ce,"Duk da kasancewar gadon sarauta ta haramta ga Farouq amman za a iya bashi rikon kwarya na sati ɗaya ko ƙasa da hakan domin tabbatar da komai ya yi daidai daga nan in ma mahaifinsan ne zai karɓa ko wani sai abada amman na tabbatar da cewa in dai Farouq ya kasance a kujerar nan ko da na kwana ɗaya ne abubuwa da dama zasu setu."

Gyaɗa kai Sarkin Bida ya yi alamun ya ji dadin jawabin Khalil ka fin ya ce,"Babu shakka na ji dadin hakan domin ko ni jikina ya jima da bani cewa shi kadai ne zai iya gyara gurɓacewar da masarautar nan ta yi kuma ina goyon bayan hakan ya yi sarauta na sati ɗaya sannan bisa adalci an bar masa zaɓin kan wanda ya dace domin ba don akasin da aka samu ba shi ne mafi cancantar jogarar masarautar gabadaya."

Karaf Kilishi ta ce,"Haba Ranka Yadade nima fa ya kamata ayi mini adalci ga Ɗana nan Arham shi ya fi kowa cancanta tunda dai nima jinin gidan ce ai sai adunga duban hakki kar a tauyewa kowa."
Wani irin kallo Sarkin Bida ya bita da shi kafin ya ce,"Ki yi mini shiru kin taɓa ganin in da mace ta gaji sarauta ne? Bare ke kanki ma mai laifi ce ina nan dawowa kanki ba wai kin ga anyi shiru ba,ai ina sane da cewa komai tare kuke aikatawa."

Abdul-Raheem ya ce,"Kwarai kuwa Ranka Yadade wallahi da ita munafuka da ita muke shirya komai."

Tsiru-tsiru Kilishi ta yi kafin ta ce,"Wallahi karya ne,ni dai na san akwai sa hananuna ayiwa Rasheed Kurciya amman wallahi babu hanuna a kashe Marigayi Mai Martaba. "

Kuka Hajiya Kaka ta fara tana fadin,"Amman ku dai na yi asarar haihuwarku na yi dana sani kun cutar dani kun cutar da zuciyata Abdul-Raheem saboda kawai abun duniya ka kashe mahaifinka kuma kuka haɗa baki kuka cutar da Ɗan uwanka,Allah na tuba ka yafeni da laifin da na yi ka bani wa innan 'Ya'Ya marasa tausayi."

Sarkin Bida ya ce,"Ki yi hakuri Hajiya Allah ya riga da ya kaddara hakan sai dai kawai su dinne suka zam sanadi Kilishi indai Rasheed ya yafe mata shikenan shi ko Abdul-Raheem dole a hukunta shi bisa ga kisan da ya yi."

Durkusawa Kilishi ta yi gaban Yarima Rasheed tana kuka,"Ya kai Ɗan Uwana ka yafe mun wallahi Abdul-Raheem ne ya kwaɗaita mun son sarauta kan cewa in mun koraka wata duniyar

ni da shi zamuyi abun da muke so ka yafe mini Don Allah na tuba."

Murmushi Yarima Rasheed ya yi ya ce,"Ki tashi Allah ma muna yi masa laifi kuma yana yafe mana."

Nan ta fara yi masa godiya domin tasan cewa indai aka ce za a hukuntata to kiyamarta ta tsaya.

Sarkin Bida ya ce,"Ba zan bar nan gurin ba har sai na naɗa Umar a matsayin Sarkin Al'adu na sati guda don haka adauko mun rawanin da na bashi. "

Cikin hanzari Javed ya je ya dauko,take kuwa aka naɗawa Farouq rawanin yayin da duk wani abu da ke rayuwa cikin gidan al'adu ya dawo karkashinsa.

Wani irin baƙin ciki ne ya tokare Abdul-Raheem a zuciya wanda ya kasa riƙewa take ya zama tamkar zautacce sai wasu irin sambatu yake yi.

Sarkin Bida ya tambayi Farouq,"Shin kana da wata bukata da kake so ayi ma?"

Farouq ya ce,"Eh domin ina so kar atafi da Tsohon Mai Martaba a kasheshi inda hali abar mana shi asanya shi a dakin tsaro ganin cewa ya riga da ya zauce wannan ma kadak wata ishara ce da kuma hukuncin ubangiji. "

Jinjina kai Sarkin Bida ya yi kafin ya ce,"E to a hakikanin gaskiya dai babu hukuncin da ya dace dashi a yanzu fiye da na kisa kamar yadda Allah ya umarta amman kuma kamar yadda kace kai ma kasancewarsa zautacce sakaya ce ta Ubangiji,ba zan musa maka ba domin ko a hakan aka barshi ya riga da ya gama yin asara don haka zaka iya ajiyeshi kamar yadda kake so."

Hakan kuwa akayi dakarai ne suka daukeshi suka sa shi dakin ajiya yanata sambatu da wasu tsalle tsalle da kyar suka kulle kofar suka fito.

Mai Martaba Sarkin Bida ya  gama miƙa ragamar komai a hannun Farouq kafin ya bar cikin garin Mokwa.

Suna tafiya Farouq yasa aka kiya Wani babban Doctor ya zo duka ya dubasu aka wankewa wa inda suka ji rauni gurin sannan aka yi masu allurau aka basu magunguna.

Zahra,Zeeyter,Zoe da Deejerh ne suka shiga gyaran gidan tsaf da kansu  ko da Janinah ta ce zata tayasu ƙi suka yi suka ce bata da lafiya, sai da suka gyara gidan tsaf ko ina ya yi kalkal suka baɗe da turaren wuta.

Dakin Mai Martaba Abdul-Raheem Su Farouq suka nufa sai da suka cire dukkanin wani abu da ya shafi tsafi suka zubar duk wani abu suna cirewa Abdul-Raheem yake ƙara ficewa a hayyacinsa.

Tafiya Xavier ya yi kasancewar an fada masa cewa an fara gano wa inda suke zargi da kisan Baba Malam da kuma binsu Farouq zasu kashe.

Jamaal,Junaid da Javed suna biye da su Farouq suma suna tayasu aikin.
Bayan sun kammala an seta komai Farouq ya kira meeting din gaggawa da duk wasu ma'aikatan gidan ya faɗa masu sabon tsarinsa,sunji dadi matuka domin babu takura da tsanani kamar irin na Abdul-Raheem hakan yasa kowa ya tashi yana cikin farinciki.

BAYAN KWANA UKU
Masu bincike nata bincike,Farouq ya gama seta komai da gyara komai da ke wakana a gidan ya kira zama kan kowa ya faɗa in akwai abun da yake da muraɗi.

Javed ne ya fara magana kan cewa yana so ya auri Meemah yasan cewa ba a aminta da auren wa inda ba jinin sarauta ba bai sani ba ko za a lamunce masa.

Tuni Farouq ya ce,"Wannan tsarin da ne,a yanzu kowa na da damar zabar matar da zai aure muddin ta kamata don haka Abba Malik ya je ya nemo maka auren da kake so."

Javed ya yi farinciki da jin hakan sosai sai kuma Janinah ta ce,"Ayi hakuri kar aga kamar na yi rashin kunya,amman na lura kamar an manta da batun nawa auren ko?"

Dariya suka yi duka.
Farouq ya ce,"Haba dai waye ma ya isa da mantawa da batun auren Kanwata,yanzu me kikeso? Kuma wa kike so ki aura?"

Kunya ta ji ta rufe ido ta ce,"Uhumm Arham mana amman daman cen muna son junanmu kawai tunanin su Auntu Kilishi da Mai Martaba ne yasa na ke ja baya kuma ni ina so ci gaba da karatu. "

Farouq ya kalli Arham ya ce,"To Oga ka ji fa na san daman kai ma kana son abarka to amman shin ka yarda da cewa zaka barta ta ci gaba da karatunta? Domin ni na jima da yi mata wannan alƙawarin. "

Arham ya ce,"Ranka Yadade ai karatu baya hana aure kamar yadda aure baya hana karatu zan ji dadi nima in ta yi karatun don haka babu wata matsala ta bangarena."

Yarima Rasheed ne ya ce,"Ma sha Allah  gaskiya na ji dadin hakan kunga yanzu ke nan muna da shirin bukukkuna har biyu to saura kai ma babban Yaya a fito da mata ko."

Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Tukunna dai amman In sha Allah Very Soon."

Karaf Hajiya Kaka ta ce,"Aa fa ni baza amun kishiya ba ni kadai na isheshi ehee."

Dariya Farouq ya yi ya ce,"Yawwa shikenan ma fada masu yan matana."

Sun sha hira sosai tukun suka watse.
Dake bangare guda aka bawa 5stars Farouq na shiga ya tarar da Zoe zaune ta ƙura idanu gaban tv tana kallon Dr.Zakir Naik yana lectures akan Rahamar da ke cikin musulunci.

Zama ya yi kusa da ita yana,"Ah Madam sannu da kallo."

"Welcome Sir,an gama zaman fadar ne?"

Ya gyaɗa mata kai.
Murmushi ta yi ta juyo tana kallonsa kamar zata yi magana kuma sai ta fara wasa da zoɓen da ke hannunta da Farouq ya lura tana son yin magana sai ya juya shi ma yana kallonta suna kallon kallo.

Daidai lokacin Zeeyter ta fito daga daƙi kenan ta gansu Murmushi ta yi tayi masu gyaran murya. Suka ankare kafin ta koma ta kulle kofa.

Farouq ya ce,"Kamar kina son yin magana ne."

Girgiza kai ta yi alamar e sai ta kara da,"Amman ina jin nauyin fada saboda addininku."

Farouq ya ce,"Saboda Addininmu kuma? Aa ni dai yanzu fada muji."

Zoe ta ce,"Ina so in fada amman ina tsoro saboda ance wai ku musulmai kuna wulaƙanta mata indai sune suka fara... sai kuma ta yi shiru.

Farouq ya ce,"ki faɗa mana,indai sune suka fara me?"

Sunkuyar da kai ta yi ta ce,"Suka fara cewa suna sonku kuma suna so ku auresu."

Farouq ya kalleta cikin ido kafin ya ce,"Kina Sona?"
Ta girgiza kai.
Murmushi ya yi ya gyara zama kafin ya ce,"Da farko dai ba haka bane abun da kika ji mutane na faɗa kan cewa wai in mace ce ta fara cewa tana son namiji yana wulaƙantata domin mu a addinin musulunci ma ana daraja mata sosai fiye da zatonki sannan ko Manzo Allah S.A.W matarsa ta farko ita ta fara neman cewa ya aureta kin ga kuwa ba haram bane hasali ma tamkar sunnah hakan yake garemu a karshe kuma ina miki albishir da cewa nima sonki kuma zan aureki."

Don farinciki Zoe bata san lokacin da ta rugume Farouq ba ƙaƙam tana wani irin lumshe idanu. Janye jikinsa ya yi yana,"Ki bari a Nigeria ba a cika haka ba fa yanzu sai a mana wata fassarar."

Dariya ta ce,"Oh Sorry amman da ni da nake so inyi kissing dinka ma."

Farouq ya ce,"wannan sai bayan aure."

Zoe ta ce,"Tom sannan kuma akwai abu na biyu Ina so in musulunta tun ba yau ba,kuma tun da ka fara koyamun sallar nan kusan kullum sai na yi da dare amman matsalar shine ban iya karatun ciki ba duk da cewa iya ba  ina koyan wasu da adduoi kuma ina da Application din Deen Body da kuma true ilm ina karuwa da su sosai"

Farouq ya ce,"Babu matsala,nine mijinki kuma nine malaminki zan koyar da ke komai kuma anjima zamuje masallaci a musuluntar da ke,amman ina fatan ba za mu samu matsala agun family dinki ba ko?"

Zoe ta ce,"Kasan babana da Maman sun mutu,Auntyna kuma bata da matsala sai dai na sanar da ita ma kan cewa ina so in musulunta kuma in aureka,ta amince mun ita ce ma ta bani goyon baya ta ce ita bazata hanani bin addinin da yafi kwanta mun arai ba kuma tana tare dani akomai."

Farouq ya ce,"Ma sha Allah,amman ina so ki bani labarin dalilin da yasa kika ji cewa kina son shiga musulunci."

Zoe ta gyara zama kafin ta ce,"Ina yawan bibiyar islaminc lectures a Deen Body da true Ilm sannan na yi bincike akai sosai wanda na fahimci abubuwa masu yawa."

Ta tsawaita da maganar kafin ta ci gaba da fadin,"Musulunci shi ne addinin da ya koya mana cewa rayuwa ba wai kawai duniya bace, amma wata hanya ce zuwa ga babban sakamako Aljanna.

Kuma a Musulunci mace tana da matsayi na musamman sosai. Allah ya ɗaga matsayin uwa har ya ce ‘Aljanna na karkashin ƙafafun iyaye mata.’ Kowane Musulmi yana ganin mace a matsayin gata da amana, ba wani kayan wasa ko raini ba.

Kuma a duk lokacin da wani ke cikin damuwa ko tashin hankali, akwai adduoi masu yawa da aka tanada da mutum na karantawa zai samu nutsuwa.

Musulunci ya koya cewa: ‘Kada ki taɓa ganin ke ba ki da amfani. Kina da daraja a idanun mahallici, kuma yana so ki dawo gare Shi domin ya cika zuciyarki da natsuwa da farin ciki.’

Kuma Allah Ko da Alqur’ani ya na cewa: “Ku tuna Ni, zan tunaku. Ku gode mini kada ku kafurta.” Wannan yana nuna Allah yana son bauta mai cike da kauna, ba tsoro kawai ba.

A Musulunci babu banbanci tsakanin fari da baƙi, talaka da mai kudi, mace ko namiji  kowa dai

Allah yake duba zuciyarsa da ayyukansa.

Haka kuma Tawakkali da Aminci
Musulmai suna dogara ga Allah (SWT) a dukkan al’amura kuma hakan yana basu kwanciyar hankali da karfin zuciya, musamman a lokacin damuwa. Wannan yana birge mutane masu neman natsuwa a zuciya.

Akwai wasu ayoyi biyu ma da suka kara bayyanar mun da cewa a cikin duhu muke rayuwa. Suratul Ma’idah (5:75) ta ce:

"Almasihu ɗan Maryam ba komai ba ne face Manzo. Lalle an riga an yi wasu Manzanni kafin sa. Kuma mahaifiyarsa mace ce mai gaskiya. "

Sannan shi da kan shi Almasihu a Suratul Maryam (19:30) ya ce,"

> قَالَ إِنِّي عَبْدُ اللَّهِ آتَانِيَ الْكِتَابَ وَجَعَلَنِي نَبِيًّا

Lalle ni bawan Allah ne, Ya ba ni Littafi kuma Ya sanya ni Annabi,ka ga kenan hakikanin gaskiyar cewa shi ba Allah bane kamar yadda muke ɗauka,shi annabin Allah ne.

Da kuma
maganar da Yesu (Almasihu) ya faɗa a Bible lokacin da aka daura shi akan cross.

In Matthew 27:46 and Mark 15:34, Jesus said,"
My God, My God, why have you forsaken me?
Ya Allahna, Ya Allahna, don me ka yashe ni?"

Dana bincika a Musulunci kuwa,
Babu irin wannan magana saboda Qur’ani ya ce Isa bai sha wannan azaba ba kuma Allah bai taɓa yashe shi ba.

Sannan kuma yadda kuke rayuwa tsakaninku aminai biyar na matukar birgeni anan na kara gasgata cewa tabbas hakan koyarwar addininkune kuma Zeeyter ta bani labarin cewa dukkanin ku ba yan uwa bane hasalima a yanar gizo kuka hadu amman kuke rayuwa da son juna da kuma goyon bayan juna fiye da wasu yan uwanma tun farkon haduwata da ku kuka fara bani sha'awa nake jin cewa dama nima a cikinku nake,kuma ina da wani friend da yake Christian ada amman yanzu ya zama Muslim tunda ya shiga Prison a London ya ga yadda musulmai ke da hadin kai da kaunar juna ga rikon ibada tuni ya shige cikinsu shi ma ya musulunta, harda shi a masu kwadaita mun cewa in shiga musulunci yana yawan bani labarai masu dadin sauraro,kuma ga ku da son kyauta domin an kwadaita maku cewa wanda kuka bada shi ne naku ku bada kadan Ubangiji ya ninka maku masu yawa ni dai ina son wannan addinin sosai kuma ma kasan miye?"

Farouq ya ce,"Aa sai kin fada." Cikin zaƙuwa.

Zoe ta ce,"Duk lokacin da nake cikin damuwa na yi wannan sallar na yi addu'a sai inji dadi araina mussamman in na karanta suratul fatiha dinnan ita kadai kuma na iya ina son surar sosai tana mun dadi tun ina sauraro kawai har na ji na haddaceta sannan kuma
Qur'an Application da Omar Sulaiman suna yi yana bada komai dalla-dalla mussamman ga wanda ke son musulunta.
Ko kai da kake musulmin ma zan so ace ka sauke wa innan Applications din Deen Body,True Ilm,Qur'an Application na su Umar Sulaiman na tabbatar da cewa zaka ji dadin kuma zaka kara kaunar addininka."

Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Tabbas dukkanin abubuwan da kika fada gaskiya Musulunci addini mai dadi kuma mai daraja,na ji dadi sosai ba kadan ba."

Ya karasa maganar yana tashi ya ce,"Kin ga wannan daddan labarin ba zan iya barinsa haka ba yanzu zanje in sanar."

"Alright byee,Love you." Zoe ta fada tana murmushi.
Amsata mata ya yi da,"Love you too." Shi ma yana murmushi ya fice da sauri.

☆☆☆Bayan anje Masallaci Zoe ta musulunta suka koma daki.

Suna zaune duka suna cin abinci da dare.
Zeeyter ta ce,"Muna da biki fa afara shiri."
Kallonta duka suka yi cikin yanayin tuhuma.
Haiydar ya ce,"Bikin wa kuma?"

"Friend da Zoe saura kiris ni kawai ma a daura mana anan kafin mu tafi." Zeeyter ta fada.

Khalil ya ce,"Ma sha Allah ga dawowa cikin musulunci ga aure,ni daman na so hakan araina ashe abun na tafe."

Deejerh ta ce,"Maddalla yanzu dai yan mata zasu huta da yaudara."

Dariya duka suka yi.
Farouq ya ce,"Tunda aka ce miki innayi auren kasuwata mutuwa za...
Yana cikin fada suka hada ido da Zoe ya yi shiru dariya suka kara kyalkyalewa.

Ana saura kwana ɗaya Farouq ya cika sati akan kujerar sarauta aka daura aurensa da Zoe,Janinah da Arham,Javed da Meemah.
Simple wedding aka yi ba taron jama'a zallan yan gida ne aka ci aka sha aka yi murna kawai.
A daren ranar Farouq ya sheda cewa Jammal ne zai karfi sarautar al'adu domin Abba Malik ma

ya nuna baya so kuma da ya duba sai ga Jammal ne mafi cancanta.
Hakan yasa aka naɗa shi.
Hakan yasa a ka sanar da sarkin Bida domin acen zasu je ayiwa Jammal naɗin.

Wani abun mamakin da farincikin kuma a daren ranar aka sanar da cewa Aunty Heedaya matar Abba Malik na dauke da cikin yan biyu bayan tsawon shekaru.
Farinciki ta ko ina ya kewaye gidan.

Washegari kuwa da sassafe suka nufi bida domin yiwa Jammal naɗi anyi raye-raye anyi waƙe-waƙe basu kwana ba aranar suka koma mokwa cikin dare saj ga Xavier ya zo da labari mai dadi an kama Naƙif wanda ya kasance shi ne shugaban yan ta'adadan da Abdul-Raheem ke amfani da shi suna kashe mutane sannan an samo sauran yan uwansa wanda suka kasance suna kasashen waje Adams tsohon  Mijin Zahra da kuma Zaid Uncle din Deejerh kowannensu Xavier yasa an kamasu a inda suke har ma akaisu gidan yari,dukkaninsu team guda ne da suka addabi rayuwar al'umma kuma suke safarar miyagun kwayoyi da mata.

Kowa ya yi farincikin jin labarin sosai mussamman Zahra da Deejerh domin yanzu sun tabbatar da sun samu yanci rayuwarsu babu barazana.

(MASU KARATU KILA BAKU FAHIMCI DALILIN SAKO SU BA KO? TO KU KARANTA YEL,FREEYA,VIXEEN zaku fi fahimta domin wannan Chronicle novel ne CENTUAR shi ne na karshen.)

Ko da aka je duba Mai Martaba Abdul-Raheem ya gama yayyaga kayan jikinsa har fatar jikinsa ya dunga ci karshe sai gawarsa aka gani hakan yasa aka yi masa wanka aka binnesa.

Zaune dukansu a falon Hajiya kaka ana hira,Hajiya Kaka ta katse su da fadin,"Yarima yanzu kai ba za ku yi aure ba haka duk zaku zauna?"
Ta karasa maganar tana kallonsa shi da Maah.

Murmushi Yarima Rasheed ya yi ya ce,"Ban jin cewa Mariam zata amince da aurena kuma ban ga laifinta ba sannan dukanmu muna farinciki a rayuwar da muke yanzu Alhamdulillahi ga Farouq muna gani ina ganin ko a haka ai mun dace."

Hajiya Kaka ta ce,"To ai shikenan  na ji tana batun komawa malaysia,Allah ya tabbatar da alkairi, Ina fatan zumuncinmu ba zai kare haka nan ba. "

Maah ta ce,"In sha Allah ai an zama ɗaya Hajiya."

Yarima Rasheed ya ce,"Yawwa daman ina son sanar da ku cewa na maida hakkin mallaka na kamfanina ga Farouq domin na san inna bar duniya ba ya da gadona."

"Ma sha Allah hakan ya yi sosai kuma na ji dadi Ubangiji ya kara tabbatar da alkairi. "
Godiya suka yi masa da fatan alkairi

Daga nan sun sha hira sosai har dare.

Zoe da Farouq kuwa ranar ɗaki ɗaya aka kwana ana shan soyayya.

Washegari da safe suka haɗa General Meeting na 5stars wanda Khalil ya kira.
Shi ne ya fara jawabi da fadin,"Bana so mu bar kasar nan ba tare da mun ƙara aikata wani abun kwarai din ba domin garin nan ya birgeni matuka mai zai hana mu fidda wata hanya da za a samarwa da wasu aiki kuma."

Farouq ya ce,"Gaskiya wannan Idea ce mai kyau nima na fara tunanin hakan domin ka ga garin suna da kyan noma sannan akwai kayan ma adanai."

Zeeyter ta ce,"Oganni zan iya yin magana?"

Farouq ya ce,"Bismillah mana Madam ai ba sai kin tambaya ba. "

"Yoo wai ai ina tsoron sa bakine a maganar dangi kar amun gori tunda dai anki amaida lamarin 6stars ko ni ba tauraruwa ba ce oho." Ta fada.

Dariya suka yi duka Haiydar ya kalleta ya ce,"Haba dai a dukkaninmu kawai muna amsa sunan ne amman kece asalin hasken boyen da ke haskaka mu Uwargida."

Farouq ya ce,"Tabbas Gimbiyata."

Taɓe baki ta yi ta ce,"Yawwa ga shawara mai zai hana ayi PPP public-private partnership  ina nufin haɗin gwiwa tsakanin gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu kamar dai mu kenan sai ayi akan harkar noma da kiwo,kun sanni da shige shige garin bincikena na ga garin nan suna da wannan tsarin kuma gaskiya abun ya birgeni."

"Nice Idea Our Yel gaskiya na ji dadin wannan batu,to ku ya kuke gani?" Khalil ya fada.

Dukansu amsawa suka yi da suna goyon baya.

Farouq ya ce,"Amman ko za ki iya mana karin bayani kan tsarin su?"

Zeeyter ta gyara zama ta ce,"Public-Private Partnership (PPP) wata hanya ce da ake amfani da ita domin haɗa ƙarfi tsakanin gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu wajen gudanar da manyan ayyuka da kuma samar da kayayyakin more rayuwa. Wannan tsarin yana taimakawa

wajen rage nauyin kashe kuɗi ga gwamnati da kuma samar da ingantattun ayyuka ga al'umma.

Gwamnati tana bada dama ko ƙasa,
Kamfani yana saka jari da gudanarwa,
Ana amfani da aikin don amfanin al'umma.

Misalan PPP

Gina hanyoyi,Wutar lantarki,Asbitoci,Noma da kiwo kamar yadda kuka ce akwai kyan noma anan da sauransu.

Ga kadan daga Fa'idodin PPP

Rage nauyin gwamnati wajen kashe kuɗi.
Samar da ayyukan yi ga jama'a.
Inganta inganci da ƙwarewa a ayyukan more rayuwa.
Rage talauci a ƙasa.
Yin ayyuka bisa tsari da sauransu.

Zahra ta ce,"Maddalla da ke."

"Me zai hana mu dau bangare biyu to na noma da kiwo? Ai ina ganin za a iya yinsu a tare." Haiydar ya fada.

Deejerh ta ce,"Gaskiya ya yi sosai hakan ma in akayi."

Khalil ya ce,"Zai fi tafiya da yanayin garinma fiye da tunaninmu."

Farouq ya ce,"Yes kuma mu namu ma ina tunanin abu uku zamu haɗa tunda muna da wadatattun filaye akwai wani wanda yake Na gidan nan akwai ma'adainai zamu haɗa har dashi a fara haƙowa."

Zahra ta ce ,"Ma Sha Allah to yanzu suwaye kuke ganin zamu fi maida hankali a dauka aikin?"

Haiydar ya ce,"Mata,Mata irin wa inda suke da matukar bukata,ma ana wanda mazajensu basa sauke nauyin da ya rataya a wuyansu ko wa inda mazansu suka rasu da dai sauransu domin hakan ma tamkar wata hanyace da za a budewa mata a nuna masu hanyar da zasu tashi su nemi na kansu da kuma nuna darajar sana'a ga 'Ya mace na tabbatar da cewa zamu samu lada ko awajen ubangiji."

Dukaninsu sun amince da shawarar da suka yanke,Farouq da Haiydar zasu yi kokarin wajen shigar da batun gwamnati shi kuma Khalil ya fara tsara yanayin ginin da zasu fitar.

Ko da Farouq ya sanarwa da Abba Malik da Yarima Rasheed sun yi farinciki sosai kuma sun basu goyon baya ɗari bisa ɗari,hakan yasa ma suka shige masu gaba wajen tabbatar da komai ya tafi daidai,cikin wata guda kuwa suka kammala komai da gwamnati.

Ginin da zasu yi ne kadai ya  rage shi ma suka fara don Khalil ya riga ya gama tsarawa,Javed ma ya yi masu kokari sosai da shi aka dunga shiga da fice hakan ma yasa Suka yanke shawarar cewa in sun tafi shi zai dunga lura da wajen duk da cewa suma zasuna zuwa lokaci bayan lokaci.

Cikin ikon Allah aka kammala komai aka dauki mata aiki kamar yadda suka tsara, anyi nasarar fara haƙo zinare sannan an fara kiwo da noma.

Nomar shinka da alkama har sun fara fitowa saboda kular da suka samu domin da kansu suke yin taki, a cikin matan da aka dauka aiki aka ware wasu aka koya masu yadda zasu na yin ingataccen taki na gargajiya.
Sai da suka tabbatar komai ya tafi daidai kafin suka fara shirin tafiya.

Janinah da Ameemah an maida su School duka suna university sannan Farouq ya kara karfafa mata kan Foundation dinta yanzu an santa an san ita ke gudanar da komai.

Gabadaya 5-Stars Malaysia suka nufa domin wai acen zasu ce su yi shagalin auren Farouq da Zoe tunda aure kawai aka daura a Nigeria.
Hakan ne kuwa ya kasance duk da Farouq ya so hana Zoe daukansu a Jet dinta ganin ita Amaryace ta ce aa ita kam da kanta zata kaisu.

Sunyi sallama da Mokwa Janinah da Hajiya harda kukan rabuwa da Farouq  ya masu alkawari ba zai jima ba zai dawo ya gansu.

Kafin su isa Malaysia Maah ta haɗa masu tarba sosai domin tana matukar kaunar Zoe mussamman da kasance kamar ita da ta musulunta.

Suna zuwa washegari gari aka fara shagalin biki.
Zeeyter da Haiydar ba wasa sun tiƙi rawa son ransu anyi wasa anyi dariya sannan anyi farinciki.
Bayan an kammala biki kafin kowa ya koma sai da suka yi saukar Qur'ani  suka yi Adduoi sosai sannan suka yi sadaka ta mussamman kafin kowa ya  kama gabansa.

Zoe na kwance a cinyar Farouq ta ce,"Ka san mene ne?"
Farouq ya girgiza kai.
Tashi ta yi ta zauna kafin ta ce,"Da ace a duniya za asamu irin 5stars da rabi da kwatan

matsalolinta sun ƙare ko ma duka matsalolin a nemesu arasa,dukaninku kowa na da labari mai ban al'ajabi da tausayi amman saboda jajircewa da rashin cire tsammani da rahmar ubangiji ji yadda kuka zama abun alfahari ga duniya,ni dai ina fatan nima na zama jajirtacciya kamar yadda Marubuciya Aisha Sani Abdullahi ta ce "Namiji kokari garesa mace kuwa jajircewa gareta zan so haɗa dukkanin biyun,domin  yin aiki tuƙuru,har in kai ga cin nasara a rayuwa." To nima hakan biyun zan haɗa duk waje guda domin inyi koyi daku."

Murmushi Farouq ya yi ya ce,"Da farko ki fara yarda da kanki,kuma kiji aranki cewa za ki iya duk wani abu da kika sa a gaba,duk rintsi duk wuya,domin nasara binta ake tana gudu sai an dage kuma an tsammaci cimmata duk tsanani sai adace."

Rugumesa ta yi kafin ta ce,"In sha Allah  ai ma nasan ko da na yi kokarin sarewa ba za ka taɓa barin hakan ya faru ba."

ALHAMDULILLAHI

Alhamdulillah! I have finally completed my book series “5-Stars Chronicle” after three years (2022 to 2025) of dedication and hard work. The series includes Yel, Freeya, Vixeen, and Centuar.

My heartfelt gratitude goes to all my amazing readers who have stood by me from the very beginning until now, and to my mentor who tirelessly supported and guided me throughout this journey. Thank you for your love, encouragement, and loyalty.

I hope you all enjoyed the books and learned valuable lessons from them. For those who haven’t read Yel, Freeya, and Vixeen yet, I invite you to do so because I’m confident you won’t regret it.

I wish you all the very best and send you my love. There’s also a possibility of a small giveaway to celebrate the completion of this journey. Stay tuned! ❤️

Urs Aisha Sani Abdullahi Xayyeesherthul-humaerath
08103080717